SALON TALLATA ‘YAN TAKARA A WAQOQIN JAMHURIYA TA HUXU: NAZARI A KAN WASU WAQOQIN SIYASAR JAMHURIYA TA HUXU

NA

MURTALA ADAMU
M.A/ARTS/00907/2008-2009

A Thesis Submitted to the School of Post Graduate Studies, Ahmadu Bello University, Zaria. In partial fulfilment to the requirements for the Award of Degree of Master of Arts in African Languages (Hausa). Department of African Languages and Cultures, Ahmadu Bello University, Zaria-Nigeria.

FEBRUARY, 2014.

Declaration

I hereby declare that the work in this thesis titled " The Stylistic Campaign in the Political Verses of the Fourth Republic: A Texual Analysis of Some Selected Hausa Political Verses of the Fourth Republic" was performed by me in the Department of African Languages and Cultures, Ahmadu Bello University, Zaria, under the supervision of Dr. M.Y. Tsoho and Dr. B.S.Y. Al- Hassan .

The information derived from the literature has been duly acknowledged in the text and a list of references provided. No part of this work has been presented for another degree or diploma at any institution.

_____

MURTALA ADAMU
MA/ARTS/00907/2008-2009

Certification

This thesis titled " Campaign Style in the Political Verses of the Fourth Republic: A Texual Analysis of Some Select Hausa Political Verses of the Fourth Republic" meets the regulations governing the award of the degree of Masters of the Ahmadu Bello University, Zaria, and is approved for its contribution to knowledge and literary presentation.

Chairman, Supervisory Committee (Dr. M.Y. Tsoho)	(Signature)	(Date)
Member, Supervisory Committee (Dr. B.S.Y. Al- Hassan)	(Signature)	(Date)
Head of Department (Dr. Balarabe Abdullahi)	(Signature)	(Date)
Dean, School of Post Graduate Studies (Prof. Adebayo Joshua)	(Signature)	(Date)

Sadaukarwa

Na sadaukar da wannan aiki ga mahaifana Marigayi Malam Adamu Musa da Malama A’isha Ibrahim da kuma iyalina.

Godiya

Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah maxaukakin Sarki, wanda ya raya ni, kuma ya ba ni ikon gudanar da wannan bincike da taimakonsa har ya kammalu. Tsira da amincin Allah su qara tabbata ga Shugaban Manzanni, kuma cikamakin Annabawa, Annabi Muhammadu xan Abdullahi tare da Alayensa da Sahabbansa da waxanda suka bi shi da kyautatawa, har ranar tashin qiyama.

Godiya ta musamman ga jagororin duba wannan aiki, Dr. Magaji Tsoho Yakawada da Dr. Bello Sodangi Yaro Al-Hassan. Ina miqa matuqar godiyata gare su saboda duk da ximbin ayyukan da ke gabansu, suka yi haquri da ni, duk lokacin da na je neman shawara su saurare ni su ba ni wadda ta dace, kuma su sanya ni hanya, ba tare da nuna gajiyawarsu ko qosawa ba. Sannan kuma da sadaukar da lokacinsu da suka yi suka duba aikin da taimakonsu ne har aikin ya kawo inda yake a yau, a kammalensa. Allah ya saka masu da alherinsa. Allah kuma ya qara yi masu jagora a dukkan al'amuransu na yau da kullum. Ina kuma miqa godiyata ga Farfesa Muhammad Lawal Amin wanda shi ne ya duba aikin daga cikin gida, tare da qarfin gwiwa da shawarwari da ya yi ta ba ni ba tare da gajiyawa ba, ta yadda aikin ya inganta. Sannan kuma godiya ga Shugaban Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Dr. Balarabe Abdullahi da kuma Jami'i mai kula da karatun manyan Digirori, Dr. Salisu Garba Kargi da Farfesa Munnir Mamman da Dr. Abdullahi Garba Wurma (Marigayi, Allah ya ji qansa) kan shawarwari da kuma qaimi da qarfin

gwiwa da suka ba ni lokacin gudanar da wannan aikin. Haka kuma ina miqa godiyata mai tarin yawa ga Farfesa Balarabe Zulyadaini na Sashen Harsuna da Kimiyyar Harshe na Jami'ar Maiduguri, wanda shi ne ya duba aikin daga waje, sannan kuma ya ba da shawarwari waxanda da su ne aikin ya kammalu, har ya ba da siffa da sigar da ake ganin sa da ita. Dukansu Allah ya saka masu da alkhairinsa mai yawa tare da yi musu jagora a cikin al'amuransu.

Ba zan yi tuya in manta da albasa ba, don haka ina miqa godiyata ga malamaina da suka koyar da ni, waxanda suka haxa da babanmu Farfesa Xalhatu Muhammad da Farfesa Muhammad Lawal Amin da Farfesa Munir Mamman da Farfesa Sa'idu Muhammad Gusau da Dr. Magaji Tsoho Yakawada da Dr. Bello Sodangi Yaro Al-Hassan da Dr. Ilyas Abbas da Dr. B.S. Bawa (Marigayi, Allah ya ji qansa). Allah ya saka masu da alkhairi baki xaya.

Haka ma, ba zan manta da malaman Sashe da wasu malamai na wasu Jami'o'i kan shawarwari da qarfin gwiwa da suka ba ni ba. Waxannan kuwa sun haxa da Malam Adamu Ibrahim Malumfashi da Malama Rabi Garba (Allah ya ji qanta) da Malam Shu'aibu Abdulmumini da Malama Hauwa Muhammad Bugaje da Malama Halima Kabir da Dr. Aliyu M. Busa da Dr. Shu'aibu Hassan da Malam Sani Masinjan Sashe da dai sauran malamai da ma'aikatan Sashe. Haka kuma ina gode wa Farfesa Isah Mukhtar da Farfesa Tanimu Musa 'Yar'adua da Farfesa Haruna Abdullahi Birniwa da Dr. Aliyu

Mu'azu da Dr. Hafizu Miko Yakasai, da Farfesa Ibrahim A.M. Malumfashi da Farfesa Atiku Ahmad Dunfawa da Farfesa Salisu Ahmed Yakasai da Farfesa Ahmed Tela Baba.

Godiyata mai yawa ga Mahaifana da suka rene ni, kuma suka ba ni kyakkyawar tarbiyya har na zama mutum. Ina gode wa iyalina, Hafsat da Sa'adiya da 'ya'yana baki xaya kan addu'o'insu da haquri da suka yi kaxaici da matsalolin da kan taso a lokacin da nake gudanar da wannan bincike. Haka kuma, ina gode wa qanena Xahiru, kan irin taimakon da ya yi mini a wasu harkokin gidana duk lokacin da buqatar haka ta taso a lokacin da ba ni gida. Ina kuma godiya ga abokaina Abdurrahman Lado Doka, na Sashen Ayyukan Gona na Jami'ar Bayero, Kano, da Mal. Mohammed K. Abubakar na Sashen Kimiyyar Xakin Karatu, Jami'ar Umaru Musa 'Yar'adua, Katsina da kuma kawuna Adamu Suleiman Bello.

Godiyata ga abokan karatuna irin su Abdulqadir Xan'alhaji da Safiyanu Bayero Kyambo da Zainab Isah da Haliru Musa Kuta da sauran waxanda sunayensu ba za su zayyanu ba, saboda qarancin lokaci. Haka ma ina godiya ga abokan aikina a Sashen Harsunan Nijeriya na Jami'ar Umaru Musa Yar'adua Katsina, da suka haxa da Shugaban Sashe Farfesa Sabry Ibrahim Ali Salama da Dr. Bashir Aliyu Sallau (Sarkin Askar Yariman Katsina) da Dr. Aminu Galadima Vatagarawa da Malam Shu'aibu Mustapha da Malam Bashir Abu Sabe da Malam Sirajo Ibrahim da Malam Shamsu Usman da dai sauransu.

Haka kuma ba zan yi halin kaza ba, in ci in goge baki, don haka, ina miqa matuqar godiyata ga Gwamnatin Jihar Katsina da kuma Hukumar Jami'ar Umaru Musa Yar'adua

Katsina, da suka xauki nauyin dukkan hidimomin wannan karatu tun daga farkonsa har qarshe. Allah ya saka da alkhairi.

Godiya musamman ga duk waxanda na yi amfani da ayyukan fasaharsu a wannan bincike, musamman, Alhaji Ibrahim Aminu Xandago da Garkuwansa, Abdurrahman Buhari Assada da Ibrahim Yala Hayin Banki Kawo Kaduna da mai taimaka masa a Sitidiyonsa, Mahmud M.G. da kuma Mohammed Aminu Musa Dako, a Qaramar Hukumar Giwa. Ina godiya a kan yadda suka ba ni lokutansu a lokacin da na yi hira da su, duk kuwa da ximbin ayyukan da ke gabansu. Allah Ya saka masu da alkhairi.

Daga qarshe ina miqa godiyata ga Malam Sani Masinjan Sahen Harsuna da Al'adun Afirka. Sannan kuma da Malam Muhammad Sani Adam na Kasuwar ICSA, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya, da kuma Saifullahi Aliyu Saulawa, Katsina, da suka buga wannan aikin a na'urar Kwamfuta. Haka kuma godiyata ga duk wanda ya taimaka ta kowace hanya aikin ya sami kammaluwa, amma ba a ambaci sunansa ba saboda qarancin lokaci. Allah ya saka wa kowa da alherinsa.

TSAKURE

Siyasar Jamhuriya ta huxu a Nijeriya, ta zama tamkar kakar waqoqin siyasa. Saboda a wannan jamhuriya ce aka samu yaxuwa da bunqasar waqoqi da ake shiryawa ko dai a kan jam'iyyu ko wasu xaixaikun 'yan siyasa. A wannan lokacin ne aka samu waqoqi da jigogi iri daban-daban. Wasu game da aqidun siyasu ko 'yan siyasa,wasu kuma masu nuna bijirewa ga jam'iyyun siyasa ko shugabanni, wasu kuma ma xaixaikun 'yan siyasa ne kawai suke wasawa. Wasu waqoqin ma duk da kasancewarsu na siyasa, ba su shafi jam'iyya ba. Suna magana ne game da yanayin mulki da xabi'un shugabanni. A wannan binciken an wasu waqoqin siyasa a jamhuriya ta huxu da suka zo da wani irin sauyi da aka samu na salon waqoqin, inda maimakon su mai da hankali ga yaxa manufofi da aqidun jam'iyyu, sai suka karkata ga shirya waqoqi da suke wasa ko tallata xaixaikun 'yan siyasa a cikinsu. Duk da cewa waqoqi ne na siyasa, amma wani lokaci, ko sunan jam'iyyar da xan takarar ya ke ba a ambata. A wasu waqoqin ma, a cikin amshin ne kawai ake jin xuriyar sunan jam'iyya. Kamar yadda Bahaushe ke cewa, 'Ruwa ba ya tsami banza,' don haka ne a cikin aikin an gano wasu daga cikin dalilan da suka haifar da irin wannan salo waqoqin da ake shiryawa, musamman don tallata xan takaran ga jama'a. A cikin babi na xaya an gabatar da aikin inda aka bayyana ginshiqan da aka shimfixa aikin a kan sa. Wato dalilin bincike da muhimmancin bincike da manufar bincike da farfajiyar bincike da hasashen bincike da hanyoyin bincike da sharuxxan bincike. Sannan kuma, an bayyana ra'in bincike. A babi na biyu kuwa, an yi waiwaye adon tafiya, a inda aka duba ayyukan da suka gabata da suke da dangantaka da wannan aiki. An waiwayi ayyukan da suka yi magana a kan siyasar kanta, ko game da waqoqin siyasar wata jamhuriyya a keve ko a kan jam'iyyun siyasa ko 'yan siyasa da dai sauransu. Sannan kuma an duba taqaitaccen tarihin samuwar siyasa a Nijeriya da samuwar waqoqin siyasa da dalilan samuwar salo ko wasu jigogi a wannan jamhuriya(ta huxu). Haka kuma, an duba ire-iren jigogi da salon waqoqin siyasa. A babi na uku an yi sharhin wasu daga cikin waqoqin siyasa na jamhuriya ta huxu da aka xauka a matsayin misali daga jam'iyyun ANPP da CPC da kuma PDP. Sai a babi na huxu aka duba salo da tsari na waxannan waqoqi. A babi na biyar an kammala bincike tare da bayyana abin da binciken ya gano domin tabbatar da hasashensa. Binciken ya gano wasu waqoqin siyasar Jamhuriya ta huxu da suka raja'a a kan tallata xan takara kawai ba tallata aqida da manufofin jam'iyya ba. Haka kuma mawaqan kan tallata 'yan takara da fito da halayensu na kirki ta hanyar yabo da kirari.

ABSTRACT

Many political verses have emerged in the Fourth Republic in Nigeria. It is during this republic or political era that many poets composed poems of diversified themes; on parties' manifestos, aspirational candidate, party leaders and many more. There are, infact some other poems that are being composed to praise individuals only. Although these poems are political ones, hardly the names of the polical parties are mentioned in the poems. However, what predominates the poems superficially is the praise of the particular candidate, the poet is concerned with. Sometimes the party is only mentioned in the chorus. The findings of this research revealed the factors responsible for this type of poems. The chapter one of this work consists of problems, hyphothesis, objectives and scope and delimitation to the research. The theory of formalism and structuralism used for this research is also discussed in the chapter. The second chapter is made up of the literature review. The chapter three of this work contains analyses of the selected Hausa Political Verses in the Fourth Republic from ANNP, CPC and PDP. In chapter four, the style and structure of the selected poems have been analysed. Chapter five consists of the research findings and recommendations. The research has come out with new trend in Hausa Political Poetry, where the political poets, tilted toward the candidate not the party manifesto. It also discovered the new technique adopted by the Hausa political poets, in campaign composing poetry with full of simile and metaphors. The work has clearly discovered the departure of the contemporary Hausa poets and the traditional poets in the 60^{th} and 90^{th}.

QUMSHIYA

Title Page - - - - - - - - - i

Declaration - - - - - - - - - ii

Certification - - - - - - - - - - iii

Sadaukarwa - - - - - - - - - - iv

Godiya- - - - - - - - - - v

Tsakure - - - - - - - - - - ix

Abstract - - - - - - - - - - viii

Qumshiya - - - - - - - - - x

BABI NA XAYA: SHIMFIXA

1.0 Gabatarwa -- - - - - - - - 1

1.1 Manufa da Muradin Bincike - - - - - - 5

1.2 Hujjar Bincike - - - - - - - - 4

1.3 Hasashen Bincike - - - - - - - - 6

1.4 Farfajiyar Bincike - - - - - - - - 5

1.5 Muhimmancin Bincike - - - - - - - 4

1.6 Hanyoyin Bincike - - - - - - - - 6

1.7 Sharuxxan Bincike - - - - - - - - 8

1.8 Ra'in Bincike - - - - - - - - - 8

1.9 Kammalawa - - - - - - - - - 10

BABI NA BIYU: WAIWAYEN AYYUKAN DA SUKA GABATA

2.0 Gabatarwa - - - - - - - - - - 11

2.1 Kundayen Bincike - - - - - - - - 11

2.1.1 Tarihin Kafuwar Jam'iyyun Siyasa - - - - - 12

2.1.2 Nazarin Waqoqi A Kevantattun Lokutan Siyasa - - - 13
2.1.3 Waqoqin Xaixaikun Jam'iyyu - - - - - 16
2.1.4 Waqoqin Xaixaikun Mawaqa - - - - - - 19
2.1.5 Waqoqi a Kan Talla da Farfaganda - - - - - 29
2.2 Bugaggun Littattafai - - - - - - - 34
2.3 Takardu Da Mujallu - - - - - - - 44
2.4 Ma'anar Siyasa - - - - - - - - 50
2.4.1 Ire- Iren Siyasa - - - - - - - - 52
2.4.2 Taqaitaccen Tarihin Samuwar Siyasa a Nijeriya - - - 55
2.4.3 Kafuwar Jamhuriya a Nijeriya - - - - - 58
2.4.3.1 Jamhuriya ta Xaya - - - - - - - - - 59
2.4.3.2 Jamhuriya ta Biyu - - - - - - - 61
2.4.3.3 Jamhuriya ta Uku - - - - - - - 66
2.4.3.4 Jamhuriya ta Huxu - - - - - - - 68
2.5 Samuwar Waqoqin Siyasa - - - - - - 77
2.6 Dalilan da Suka Haifar da Sabon Salo a Waqoqin Siyasa
a Jamhuriya ta Huxu - - - - - - - 80
2.7 Jigogi da Salon Waqoqin Siyasa - - - - - - 84
2.7.1. Jigon Faxakarwa - - - - - - - 85
2.7.2 Jigon Yabo - - - - - - - - - 87
2.7.3 Jigon Habaici - - - - - - - - 89
2.7.4 Jigon Talla - - - - - - - - - 90
2.8.0 Sarrafa Harshe a Cikin Waqoqin Siyasa - - - - 93
2.8.1 Siffantawa - - - - - - - - - 94
2.8.2 Tamka - - - - - - - - - 95
2.8.2.1 Tamkar Fifiko - - - - - - - - 96

2.8.2.2 Tamkar Kashi - - - - - - - 96
2.8.2.3 Tamkar Daidaito - - - - - - - - 97
2.8.3 Jinsintarwa - - - - - - - - - 98
2.8.3.1 Mutuntarwa - - - - - - - - - 98
2.8.3.2 Dabbantarwa -- - - - - - - - 100
2.8.3.3 Abuntarwa - - - - - - - - - 101
2.8.4 Aron Kalmomi - - - - - - - - - 101
2.8.5 Karin Magana - - - - - - - - - 103
2.9 Kammalawa - - - - - - - - - - 104

BABI NA UKU: SHARHI A KAN WASU WAQOQIN SIYASAR JAMHURIYA TA HUXU

3.0 Gabatarwa - - - - - - - - - 106
3.1 Sharhin Waqar *"Adon Gaskiya Ba Ya Vata"* ta Alhaji Ibrahim Aminu Xandago - - - - - - - - - - - - - 106
3.1.1 Tarihin Alhaji Aminu Ibrahim Xandago - - - - 106
3.1.2 Taqaitaccen Tarihin Jam'iyyar PDP - - - - - 108
3.1.3 Yadda Ake Tallata Xan Takara a Cikin Waqoqin Siyasa - - 110
3.1.3.1 Talla ta Fuskar Yabo - - - - - - - - - 111
3.1.3.2 Talla ta Fuskar Habaici - - - - - - - 115
3.1.3.3 Talla ta Fuskar Zambo - - - - - - - 118
3.1.3.4 Talla ta Fuskar Kirari - - - - - - - - 119
3.1.4 Jigon Waqar "*Adon Gaskiya Ba Ya Vata"* - - - - 121
3.2 Sharhin Waqar "*Yau Nijeriya Riqo Sai Mai Gaskiya* ,", ta Ibrahim Yala Hayin Banki Kawo Kaduna wadda ya yi wa Janar Muhammadu Buhari (ANPP) 124

3.2.1 Tarihin Ibrahim Yala Hayin Banki - - - - - - - 122
3.2.2 Taqaitaccen Tarihin Jam'iyyar ANPP - - - - 126
3.2.3 Sharhin Waqar "*Yau Nijeriya Riqo Sai Mai Gaskiya"* - - - 127
3.3 Sharhin Waqar "*Mu Kasa, Mu Tsare, Mu Raka"* ta Mohammed Aminu Musa Dako - - - - - - - - - 130
3.3.1 Tarihin Mohammed Aminu Musa Dako - - - - 130
3.3.2 Taqaitaccen Tarihin Jam'iyyar CPC - - - - - 132
3.3.4 Sharhin Waqar "*Mu Kasa Mu Tsare Mu Raka"* - - - 135
3.4 Kammalawa - - - - - - - - 137

BABI NA HUXU: SALO DA TSARIN WAQOQIN SIYASAR JAMHURIYA TA HUXU

4.0 Gabatarwa - - - - - - - - 138
4.1. Salon Waqar "*Adon Gaskiya Ba Ya Vata*," ta Alhaji Aminu Ibrahim Xandago - - - - - - - - - - - - - 138
4.1.2 Kamantawa - - - - - - - - 138
4.1.3 Kamancen Fifiko - - - - - - - 139
4.1.4 Abuntarwa - - - - - - - - 139
4.1.5 Abuntarwar Abuntarwa - - - - - - 140
4.1.6 Jinsintarwa - - - - - - - - - 141
4.1.7 Alamtarwa - - - - - - - - 141
4.1.8 Kambamar Zulaqe - - - - - - - 142
4.1.9 Sarrafa Harshe- - - - - - - - 142
4.1.9.1 Karin Magana - - - - - - - - 142
4.1.9.1 Amfani da Kalmomi - - - - - - - 143
4.1.9.3 Amfani da Karin harshe - - - - - - 146
4.1.10 Tsarin Waqar - - - - - - - - 147

4.1.11 Amsa-Amon Waqar - - - - - - - 147
4.1.12 Amsa-Amon Karin Waqar "*Adon Gaskiya Ba Ya Vata"* - - 148
4.2 Salon Waqar "*Nijeriya Riqo Sai Mai Gaskiya"* - - - 149
4.2.1 Siffantawa - - - - - - - - 149
4.2.2 Kwatancen Fifiko - - - - - - - 150
4.2.3 Abuntarwa - - - - - - - - 150
4.2.4 Alamtarwa - - - - - - - - 150
4.2.4 Aron Kalmomi - - - - - - - 151
4.2.5 Karin Harshe - - - - - - - - 151
4.2.6 Nahawu - - - - - - - - 152
4.2.7 Azancin Magana a Cikin Waqar - - - - - 153
4.2.8.1 Karin Magana - - - - - - - - 153
4.2.8.2 Zambo - - - - - - - - - 153
4.2.9 Tsarin Waqar - - - - - - - - 154
4.2.10 Amsa-Amon Waqar - - - - - - - 155
4.2.11 Amsa-Amon Karin Waqar "*Yau Nijeriya Riqo Sai Mai gaskiya*" - 155
4.3 Salon Waqar "*Mu Kasa Mu Tsare Mu Raka"* - - - 156
4.3.1 Amsa-Amon Waqar - - - - - - - 156
4.3.2 Amsa-Amon Karin Waqar - - - - - - 157
4.3.3 Tsarin Waqar - - - - - - - - 157
4.4 Kammalawa - - - - - - - - 158

BABI NA BIYAR: NAXEWA

5.0 Gabatarwa
5.1 Naxewa
5.2 Kammalawa - - - - - - - 159

5.3 Shawarwari - - - - - - - - 162
Manazarta
Rataye

BABI NA XAYA:
SHIMFIXA

1.0 Gabatarwa

Siyasa wata aba ce da ta shafi rayuwar al'umma a duniya, kuma ta yi tasiri matuqa a zukatansu. Don haka ne ma mawaqan siyasa, su ma ba a bar su a baya ba, suke da irin wannan tasirin a cikin jininsu da rayuwarsu ta yau da kullum. Saboda da wannan tasirin ne, ya sa waqoqi na siyasa da kuma 'yan siyasar kan su, sun zama tamkar jini da tsoka. Watau dai, ba a raba su. Don haka ne ma ya sa waqa a qasar Hausa ba abin nema ba ce. Domin kuwa, an yi nazarce-nazarce da dama a lokuta daban-daban a kan waqoqi, tun ba na siyasa ba. Samuwar siyasa da havakarta a Nijeriya ya sanya ake samun waqoqi da ake shiryawa kama tun daga masu yaxa manufofin jam'iyyun siyasa da 'yan siyasar kan su da na yabon shugabannin siyasa da jam'iyyunsu da na tallata siyasa da 'yan takararsu. Duk suna yin haka ne dangane da muhimmancin shiga jam'iyya da kuma zaven shugabanni na gari. Ganin yadda aka samu yawaitar waqoqi a wannan kakar siyasa a jamhuriya ta huxu, ta kai ga yin la'akari da cewa an sami waqoqi musamman da ake yi wa 'yan siyasa maimakon yi wa jam'iyyu. A irin waxannan waqoqi ba manufofi da aqidun siyasa ko jam'iyya aka fi ba muhimmanci ba, babban abin da aka fi ba qarfi, shi ne tallata xan takara. A wannan aiki an mai da hankali ne ga jigo da salon irin waxannan waqoqi.

Wannan batu ne aka gudanar da bincike a kan sa, wanda ya shafi irin waqoqin da ake shirya wa 'yan siyasa domin bayyana su da kuma tallata su ga jama'a kamar yadda aka

ambata a sama. Wannan shi ya sa aka gudanar da bincike game da waqoqi da suke tallata ‘yan takara maimakon tallata aqidar siyasa. Daga qarshe an fahimci wani sabon salo da masu shirya waqoqin Hausa suka xauka a fagen waqoqin siyasa.

Dangane da waqoqin siyasa kuwa, masana da dama sun bayar da ma’ana daban-daban. Birniwa, (1987 : 62 da 204) ya bayyana cewar Bello Gixaxawa ya bayyana waqar siaysa da cewa:

> “Ita ce waqar da ta qunshi cikakken yabo ga jam’iyya da bayyana kyawawan manufofinta. Sannan kuma ta kasance ta kushe abokan gaba”.

Haka shi ma Yusuf Kantu, (Birniwa, 1987: 204) ya bayyana cewa :

> “Waqar siyasa ita ce wadda ta qunshi kushe jam’iyyun hamayya sannan kuma take bayyana manufofin jam’iyyar da mutum yake mara wa baya”.

Furniss, (1996:228), yana ganin cewar mafi yawa waqar siyasa tana karkata ne ga shugabannin siyasa ta bayyana kyawawan halayensu da asalinsu ta fuskar nasaba. Haka kuma waqoqin siyasa na kushe shugabannin siyasar abokan hamayya. Gusau (2008:290) yana ganin cewar waqoqin siyasa su ne irin waqoqin da ake shirya wa siyasar kanta da jam’iyyun siyasa da kuma ‘yan siyasa.

Idan aka yi la’akari da bayanan da suka gabata a sama, a dunqule za a iya cewa waqoqin siyasa su ne waxanda suka qunshi yaxa manufofin jam’iyyun siyasa da kuma yabon mutanen cikin jami’iyyun da kuma kushe abokan hamayya da jam’iyyunsu.

Daga nan za a iya fahimtar cewar waqoqin da ake yi na tallata ‘yan takara, wani sabon salo ne da waqoqin siyasa suka xauka. Wannan kuwa ya faru ne saboda wasu dalilai da

wannan bincike yake hasashe, kuma yake so ya gano ya tabbatar da su. Domin kuwa ana cewa: “Idan kixa ya canza, to rawa ma za ta canza.” Yahaya (2001:2) ya bayyana sabon salo da cewa:

> “Sabon salo na nufin sabuwar hanya, hanyar da take daban da wadda aka saba.”

Waqa aba ce da fasihai ke amfani da ita domin bayyana wata manufarsu cikin sauri ga jama’a. Domin kuwa, waqa ta fi saurin karvuwa ga jama’a, kuma an fi son sauraren ta fiye da wa’azi. Wannan ne ma ya sa mafi yawan ayyukan malaman jihadi waqoqi ne (Sa’id, 1978:66). Ke nan, daga wancan bayani, a iya cewa ana amfani da waqa a matsayin wata kafa ta yaxa manufa cikin gaggawa kamar dai yadda iska ke kaxawa ta game ko’ina cikin xan qanqanen lokaci. Wannan na iya kasacewa dalilin da su ma ‘yan siyasa suke amfani da waqa wajen bayyana manufofinsu da kuma tallata kawunansu.

Ana samun waqoqin siyasa da dama masu bayyana manufofi da ra’ayoyi daban-daban. Wannan ya haxa da waqoqin da suke yaxa manufofi da aqidun siyasa da ‘yan siyasa. Bayan waxannan ta kai ga samuwar wasu salailai na waqoqin sayasa. Daga ciki akwai masu nuna bijirewa da gargaxi ga ‘yan siyasa. Misali waqar “*Shegiyar Uwa*” da waqar “*Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba*”, na Haruna Aliyu Ningi, na kira ne ga bijire wa jami’iyyar PDP da kuma tawaye daga shirin tazarce na Obasanjo (Binta, 2007). Akwai kuma waqar “Motar siyasa: Saqon Talakawa Guwa ga ‘Yan Siyasar Zamani,” ta Bello

Xanshabiyu, da take bayyana irin yadda talakawa suka waye da kuma aika saqonsu ga ‘yan siyasa cewa su gyara halayensu. (Bayero da Dunfawa, 2010).

Hausawa na cewa “Idan kixa ya canza, rawa ma sai ta canza”. Kasancewar canjin yanayi da qasa ta sami kan ta, watakila ya sa aka sami sauyin salon waqoqi na siyasa. Domin a halin yanzu an sami sauyi mai yawan gaske ta fuskar salon waqoqin siyasar da ake da su na yanzu, idan aka kwatanta su da na da. Domin idan aka lura da mafi yawan waqoqin siyasar zamunan farko, sun fi mai da hankali ga tallata aqidar siyasa, savanin na yanzu da suka fi mai da hankali ga tallata “haja” (‘yan takara).

Wannan dalili ne ya sa aka gudanar da bincike domin a gano dalilan da suka haifar da wannan sauyi. Ana so a gano mece ce waqar siyasa, sannan a ga shin waxanne waqoqi ne na siyasa zalla, ko kuwa za a kira su waqoqin tallar ‘yan takara. Domin masana da masu bincike da dama sun yi rubuce-rubuce da bincike a kan waqoqin siyasa, amma dai ba a qarfafa binciken a kan wannan “kakar” waqoqin da aka samu a wannan zamanin siyasa ba. A cikin wannan bincike za a bijiro da wasu nazarce-nazarcen da aka yi da suka shafi wannan batu.

1.1 Manufa da Muradin Bincike

Wannan bincike, ya yi nazarin wasu waqoqin siyasa na Jamhuriya ta huxu ne da suka ginu kan ‘yan takara, maimakon kan jam’iyyu. An tattaro wasu daga cikin irin waxannan waqoqi an yi sharhin a kan su tare kuma da taskace su a cikin rumbun adabin Hausa a matsayin gudunmuwa a wannan fanni. An duba wannan sabon salo a waqoqin ne ta

kallon yadda ake gabatar da su ga al'umma. A cikin binciken, an yi nazari kan jigogi da tsari da kuma salon sarrafa harshen waqoqin.

1.2 Hujjar Bincike

An gina tunanin wannan bincike ne ganin yadda waqa take da muhimmanci a fagen nazarin adabi. Sannan kuma, musamman ganin yadda waqoqin siyasa suka sauya salo a jamhuriya ta huxu, savanin salon da suka xauka a zamanin siyasar farko da ta biyu.

An wayi gari, maimakon a shirya waqoqi kan yin farfagandar manufofin jam'iya da nufin jan hankalin mutane su ba da goyon bayansu, sai marubuta suka mayar da hankalinsu wajen tsara waqoqi na siyasa don yabon mutanen da suke ganin suna da qima a jam'iyyun. Wasu saboda wani muhimmin abu da suka lura gwanayen nasu na da shi, misali gaskiya da riqon amana, a yawancin lokaci kuma a wani lokaci saboda kyautar da suke yi masu.

Saboda haka, hujjar da ta sa aka gudanar da wannan bincike, ita ce don cike wani givi da aka lura da shi da ba a yi maganarsa ba. Wannan givi shi ne, yadda a hankali waqoqin siyasa suka xauki wani sabon salo a Jamhuriya ta huxu. Irin wannan salon, shi ne maimakon a shirya waqoqi a kan jam'iyya, kamar dai yadda yake a waqoqin siyasa na jamhuriya ta xaya da ta biyu, da ma ta uku, sai aka koma ana tallata 'yan takara da wasu mutanen da suka yi fice a jam'iyyun.

An duba sabon salo da mawaqan zamani suka xauka ne don nuna sauye-sauyen da suka kunno kai a waqoqin na siyasar Jamhuriya ta huxu.

1.3 Dalilin Bincike

An a duba sabon salo da mawaqan zamani suka xauka maimakon yin waqoqi na yaxa manufofin jam'iya da yin farfaganda a zavi jam'iyyun, sai suka koma suna yin waqoqi na yin tallar 'yan takaransu kawai.Yawancin lokaci za a tarar ana faxar sunan jam'iya ne kawai don sama masu ko nuna masu majinginarsu kawai.

Domin idan aka dubi waqoqin siyasa a jamhuriya ta farko da ta biyu, za a ga cewar sun mai da hankali ne ga yaxa aqidar siyasa da kishin jam'iyya da kuma mutanen jam'iyya, a maimakon tallata xan takara kacokam. Misali, waqar Sa'adu Zungur "**Arewa Jamhuriya ko Mulukiya,**" da ta Mudi Sipikin "**Arewa Jamhuriya Kawai**" da ta Shekara Sa'ad "**Waqar Yabon Ahmadu Bello,**" da ta Bello Gixaxawa "**Waqar Siyasa Zamanin Salama,**" da ta Gambo Hawaja "**Waqar 'Yan Sawaba,"** da dai sauransu da yawa, duk za a ga cewar suna bayyana manufofi ne da aqidun siyasa da kuma kishin qasa. Suna kuma tallata jam'iyyun siyasa ne don su samu karvuwa ga jama'a, ba wasu 'yantakara ba. Wannan shi ne maqasudin da ya sa aka gudanar da wannan bincike.

1.4 Farfajiyar Bincike

Wannan bincike ya taqaita ne kacokam a kan waqoqin siyasar jamhuriya ta huxu. Su ma a cikinsu, an taqaita binciken ne kan irin waqoqin da ake yi wa xaixaikun ‘yan siyasa ko jama’a ‘yan siyasa.

Saboda haka, a wannan binciken an zavi waqa guda xaya daga jam’iyyu guda uku da ake ganin sun fi fice, kuma an fi jin xuriyarsu a qasar Hausa. Waxannan jam’iyyun kuwa su ne: **PDP** da **ANPP** da kuma **CPC**. Waqoqin da aka nazarta su ne: *Waqar ‘Adon Gaskiya Ba Ya Vata*’ ta PDP ta Alhaji Ibrahim Aminu Xandago da Waqar *‘Yau Nijeriya Riqo Sai Mai Gaskiya’* ta ANPP ta Ibrahim Yala Hayin Banki Kawo Kaduna, da kuma Waqar *‘Mu Kasa Mu Tsare Mu Raka’* ta CPC ta Mohammed Aminu Musa Dako Giwa. An zavi waxannan waqoqi ne saboda saqon da ke cikinsu da kuma kasancewar su daga jam’iyyun da ake ga an fi jin xuriyarsu a qasar Hausa. Haka kuma kasancewar jam’iyyar PDP ita ce mai mulki, yayin da jam’iyyun ANNP da CPC suke manyan jam’iyyun hamayya a Nijeriya, musamman qasar Hausa. Kuma an zavi waqoqin ne ba don nuna goyon baya ga wata jam’iyya ba. A’a, sai dai domin a yi amfani da su a matsayin misali saboda da ganin dacewarsu a wannan bincike domin haqa ta cim ma ruwa. Don haka ne aka zave su domin a aza su kan mizanin nazari domin a tabbatar da hasashen da ake da shi a wannan binciken.

1.5 Hasashen Bincike

An duba sabon salo da mawaqan zamani suka xauka maimakon yin waqoqi na yaxa manufofin jam’iya da yin farfaganda a zavi jam’iyyun, sai suka koma suna yin waqoqi na

yin tallar ‘yan takaransu kawai.Yawancin lokaci za a tarar ana faxar sunan jam’iya ne kawai don sama masu ko nuna masu majinginarsu kawai. Wannan ne ya sa daga qarshen binciken aka amsa waxannan tambayoyin game da waqoqin jamhuriya ta huxu:

i) Shin ko da waxannan waqoqi na siyasa ne?

ii) Anya tallar ‘yan takara ba ta fi yawa a cikinsu ba?

iii) Me ya haifar da wannan sauyin salo?

iv) Ina waqoqin siyasa na gaba suka dosa?

1.6 Muhimmancin Bincike

Hausawa na cewa; don lada ake sallah; Binciken yana da muhimmanci ga hukumomin ilimi wajen tsara manhajar karatun Hausa ga mkakarantun sakandare da na gaba da sakandare. Haka kuma binciken yana da amfani a xakunan karatu da sassan nazarin harsuna na jami’o’i da kwalejojin ilimi. Watau binciken ya samar da abin karantawa da kayan bincike a xakunan karatu. Musamman kasancewar binciken a kan waqa ne,wadda kandami ce a fagen nazarin adabi, ba ma na Hausa kawai ba. Sannan kuma ya faxaxa rumbun adabin Hausa, ta yadda ya taskace wasu hikimomi da suke qunshe a cikin harshen Hausa daga waqoqin da aka nazarta.

Haka kuma binciken yana da muhimmanci ga masu nazarin ilimin walwalar harshe da rayuwar xan Adam ta hanyar sanin yadda al’amuran rayuwa ke sassauyawa yau da kullum. Sannan kuma binciken ya yi rana ga ‘yan siyasa su kansu, da ma masu nazarin ilimin kimiyyar siyasa da kuma masu sha’awar tsunduma a cikin harkokin siyasa.

1.7 Hanyoyin Bincike

Hausawa na cewa “Kome nisan gari, da wani a gabansa.” Don haka ne ya sa aka bi hanyoyi da dama domin bin sawun wasu ayyuka da magabata suka yi masu dangataka da kusanci da wannan aikin domin ganin ya kyautata. Hanyoyin da aka bi sun haxa da:

An yi amfani da kaset- kaset aka tattaro waqoqin da aka yi nazari a kan su, sannan aka juya su a rubuce kan takarda.

An gana da mutane daban-daban da suke da nasaba ta kusa ko ta nesa da wannan batu domin samun shawarwari da qarin haske da bayanai. Wato an yi hira da mutane a lokuta daban- daban da tattara bayanai cikin diwani . An tattara bayanai ta hanyar sauraren duk wani shirin rediyo da ya shafi wannan a rubuta muhimman abubuwa aka aje su. Kai har ma da saurare da tattaunawa da wasu masana da duba jaridu a rubuta abin da aka gani ya shafi aikin, da ma duk wani tunani da ya faxo. Domin an ce “ yaro nemi kuxi tun abin saye bai zo ba”, shi ya sa aka tattara bayanai aka taskace har lokacin amfaninsu ya zo.

Sannan kuma, an bi hanyar neman nazartar bugaggun littattafai da suka shafi wannan aiki a xakunan karatu, da ma duk inda aka same su.

Haka kuma an yi amfani da kundayen digiri na matakai daban-daban; kama daga kundin digiri na farko har zuwa na uku. Sannan an duba duk wani aiki da aka yi don ba da shaida (Certificate), inda aka duba ayyuka masu nasaba da wannan bincike. Wannan ya taimaka qwarai wajen samun bayanai da kuma alqiblar da ta dace da wannan aikin.

Sannan kuma an bi hanyar karance- karance, inda aka ziyarci xakunan karatu da dama aka sami kundayae da littattafai da Kundayen Bincike da sauransu. Daga cikin xakunan karatu da aka ziyarta, sun haxa da: Xakin Karatu na Sashen Harsuna da Al'adun Afirka da Xakin Karatu na Sir Kasim Ibrahim(Main Library) na Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. Sannan akwai Xakin Karatu na Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Xanfodiyo, Sakkwato. Haka kuma, an ziyarci Xakin Karatu na Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya da Babban Xakin Karatu na Jami'ar Bayero, Kano, da dai sauransu.

1.8 Ra'in Bincike

Wannan bincike ya dogara ne a kan ra'in *Sigar Adabi* (Structuralism) domin nazarin waqoqin siyasa da suke da salon tallata xan takara ko ake tallata xaixaikun 'yan siyasa, waxanda ake aiwatarwa a wannan kakar siyasa (Jamhuriya ta huxu). Wannan ra'i na sigar adabi an fara amfani da shi tun a tsakiyar qarni na 20 a fagen nazarin harshe. An qirqiro wannan mazahaba a Faransa a dalilin wani aiki da Ferdinand De Saussure (1857-1913) ya yi a Faransa a kan nazarin harshe, mai suna: *La Langue La Parole* (1914) da kuma *Course in General Linguistics* (1923). Wannan mazahaba ta ci gaba har ta zama ta nazarin adabi a Faransa a wajen 1960, ta kuma yaxu har zuwa Rasha da Ingila da Amurka (Shu'aibu, 2013:111). Babbar manufarsa ita ce bayyana aikin adabi dalla-dalla. Makarantar sigar adabi ta Rashawa da ta Prague da masu goyon bayan ra'in salon adabi da sauransu, duk sun haxu a kan cewa ana qoqarin bayyana qumshiyar ayyukan adabi ne

ta fuskar tsari da sigoginsu (Klarer, 2004: 79). Wannan makaranta ta yi qoqarin tarke ayyukan adabi a lokacin yaqin duniya na xaya. Roman Jokobson (1896-1982), ya bayyana cewa batun nazari ko tarken adabi, ba shi ne adabi ba kawai. A'a , sai dai abin da ya sa aka kira duk wani aikin adabi da sunan aikin adabi, kamar su rauji da amsa-amo da kari da sauransu (Klarer, 2004: 78). Haka ma, Sani, (2011: 96), ya bayyana cewa a al'adance duk lokacin da ake nazarin waqa, to lalle ne a yi magana game da tsari da kuma sigar adabi.

Haka kuma daga cikin manufofin wannan ra'in akwai:

i. Siffantawa da fexe tsarin da aka rubuta adabin kan sa.
ii. Kula da nazarin kimiyyar harshen adabi da aka xora zubi da tsari.
iii. Duba yadda ake fexe tsarin abu ta la'akari da wasu alamu.
iv. Xaukar adabi da yadda yake da tasiri ko ake aiwatar da shi, ta bar lura da tasiri da zamantakewar jama'a.
v. Fito da tsarin voye ko tubalan gina aikin adabi (qwarangwal) ko wasu dokoki na aikin adabi, kamar yadda Gerard Genette ya bayyana yadda za a qarfafi sigarta.
vi. Yana kula da yadda ake shirya matani don a samar da jerin ma'anoni a cikinsa.
vii. Duba wasu dokoki na musamman (codes) masu samar da aukuwar ma'ana a cikin matani, wanda kuma ke nuna aukuwar a cikin tsarin matanin ko a cikin al'umma .
viii. Kallon matanin adabi a matsayin wani tsari da ke tantance ma'ana (gamaxen abubuwa na alamomi da lambobi da makaranci ke fahimtar matani da su).

ix. Mayar da hankali ga abin da ya kamata makarancin matani ya sani ko wanda yake buqatar sani, game da fashin baqin kowace alama ko kalma ko salo da sauransu.

x. Mayar da hankali kan ra'ayin kimiyyar harshe da ya danganci sadarwa da fashin baqinsa; da kuma ra'ayin adabi mai samar da dokokin da za a yi amfani da su a rarrabe tsakanin maganar adabi da abin da ba adabi ba.

xi. Qarfafa komawa ga sigar adabi don gano qwarangwal na aikin adabi.

xii. Ra'in na da manufar fito da ma'ana tare da bayyana ta daki- daki daga cikin matani. (Shu'aibu, 2013: 112-113).

Ra'in Sigar Adabi, ra'i ne da ke nuna cewa kowane abu yana da sigar da aka san shi da ita, kuma ake gane shi da ita. Wato dai, kamar gini ne mutum zai yi, to lalle sai ya samu wata siga ko sifa da yake so ya kasance ginin yana da ita, wadda da wannan sigar ce za a iya ganin abu har a gane shi, a kuma bayyana shi. Don haka ne a wannan bincike aka bi wannan ra'in aka fexe waqoqi da nazartar su da kuma tsarin su. Domin ba za a yi wani rubutu ko a shirya wata waqa ba, face tana da siga ko tsari. Domin haka ne aka ga cewa kowane aikin fasaha aka yi, to yana da siffa da kuma tsari da za a kalle shi da su, a kuma iya bayyana abin da ya qunsa. Watau ta wannan tsari ko salo ne kuma za a fahimci qumshiya ko saqon da waqoqin ke xauke da shi da kuma salon da aka yi amfani da shi. Waxannan waqoqi sun qunshi wani sabon salo da ake shirya waqa a kan xaixaikun 'yan siyasa ko wasu 'yantakara, maimakon bayyana aqidun jam'iyya, duk da cewa waqoqin na

siyasa ne. Babbar manufar su (ire-iren waxannan waqoqin), ita ce a xaga xan takara sama duniya ta gan shi, domin ya samu karvuwa gare ta.

1.9 Naxewa

Wannan babi, kamar yadda aka gani haska tsanin da za a hau ne don hango manufofi da matsaloli da dalilai da kuma muhimmancin gudanar da wannan bincike. Sannan kuma, babin ya yi bayanin farfajiya da hasashe da kuma hanyoyin da aka bi wajen gudanar da bincike da suka haxa da ganawa da masana da ziyartar xakunan karatu da sauransu. Haka kuma an bayyana ra'in da binciken ya ta'allaqa a kan sa, wato ra'in Sigar Adabi.

BABI NA BIYU:

WAIWAYEN AYYUKAN DA SUKA GABATA

2 Gabatarwa

“Waiwaye adon tafiya,” in ji ‘yan magana. Masana da dama sun gabatar da bincike da nazari a kan siyasa da waqoqinta ta fuskoki daban-dabam . saboda an ce da na gaba ake gane zurfin ruwa. Wannan ya sa aka waiwaiyi ayyukan magabata a wannan fage don samun alqiblar wannan bincike. Don haka, a wannan babi an duba wasu ayyuka da aka yi da suke da dangantaka da wannan bincike. Kasancewar binciken ya shafi siyasa, za a duba taqaitaccen tarihin samuwar siyasa a Nijeriya da ayyukan da suka shafi waqoqin Siyasa da ma wasu ayyuka da suka danganci waqa ko farfaganda ko talla da suke da nasaba da wannan bincike. Sannan kuma, binciken ya qunshi ire-iren jigogin waqoqin siyasa da yadda ake amfani da salo a cikinsu. A cikin waiwayen an duba kundayen digiri kama daga digirin farko har zuwa na uku. Sannan an duba mujallu da bugaggun littattafai.

An waiwayi ayyukan malamai da manazarta , waxanda ko dai suke da dangantaka ta qut-da-qut , ko kuma ta nesa da wannan aiki. Wannan waiwaye kuwa, ya haxa da kundayen bincike tun daga matakin digirin farko, har zuwa matakin digirin digirgir. An yi haka ne kuwa domin a sami madafa da kuma alqiblar wannan bincike.

Domin kuwa Hausawa na cewa “Da tsohuwar zuma ake magani”.

2.1 Kundayen Bincike

An duba kundayen bincike a matakan digiri, tun daga digirin farko har zuwa digirin digirgir. An duba ayyuka da suka danganci kevantattun lokutan siyasa da waqoqin xaixaikun ‘yan siyasa da aka gabatar da nazari a kan su. Haka kuma an yi waiwaye game da waqoqin da aka nazarta na xaixaikun jam’iyyu.

2.1.1 Tarihin Kafuwar Jam’iyyun Siyasa

Masana da manazarta da dama sun gabatar da bincike a kan waqoqin siyasa ta fuskoki daban-dabam da kuma lokuta mabambanta. Daga cikin irin ayyukan da aka ci karo da su a wannan bincike sun haxa da:

Mashi (1986) a cikin aikinsa ya bayyana tarihin samuwar siyasa da kafuwarta Nijeriya. Ya yi bayanin kafuwar jam’iyyun siyasa tun daga jamhuriya ta xaya har zuwa ta uku. Misali, ya yi bayanin kafuwar jam’iyyu irin su NPC da NEPU da NPN da PRP da sauransu. Sannan ya kawo waqoqin baka da aka yi wa wasu jam’iyyun siyasa tare da yin sharhinsu.

Shi ma Birniwa (1987) ya duba tare da yin cikakken bayanin tarihin samuwar siyasa a Nijeriya tun daga zamanin sarauta zuwa zamanin jihadin Shehu Usmanu Xanfodiyo da tsarin shugabanci na musulunci har zuwa siyasar jam’iyya da zamanin siyasa na xaya har zuwa zamanin siyasa na biyu.

Shi ma Mu'azu (2002) ya fara aikinsa ta yin waiwayen tarihin siyasar Nijeriya tare da duba wasu kevavvun kalmomin siyasa kamar su kamfe da farfaganda da bijirewa da ita kanta siyasa da sauransu. Misali, ya bayyana ma'anar siyasa da cewa:

> "*Siyasa ita ce hanyar tafiyar da jama'a cikin kyautatawa, adalci da haqqoqin jama'a bisa adalci da tsaurarawa a wuraren da suka dace".*

Ita kuwa farfaganda, ya bayyana ta da cewa:

> "*.....hanya ce ta jawo hankalin jama'a domin yin na'am da wani sabon abu ko qarin karvuwa ga wani abu da dama can aka sani".*
> (Mu'azu, 2002: 10-11).

Funtua (2003) shi ma a aikinsa ya yi waiwaye a kan tarihin siyasar Nijeriya. Daga cikin abubuwan da ya bayyana sun haxa da tarihin samuwar siyasa da waqoqinta. Inda ya bayyana waqoqi da yawa da aka samu a siyasar jam'iyya. Misali waqoqin NEPU da NPC da NPN da PRP da SDP da PDP da ANPP da sauransu. Ya bayyana cewar cuxanyar mawaqa da siyasa ita ta sa suka qware wajen tsara waqa ga jam'iyyu da kuma 'yan takara, kamar yadda ya bayyana, a cikin waqar ne suke bayyana alamomi da manufofin Jam'iyya.

Babu shakka, ayyukan su Mashi (1986) da Birniwa (1987) da Mu'azu (2002) da Funtua (2003), ba qashin jefarwa ba ne. saboda suna da kyakkyawar dangantaka da wannan aikin. Domin sun yi magana kai tsaye game da tarihin samuwar siyasa a Nijeriya. Wato kafuwarta da kuma ginuwarta. Duka ayyukan sun ba da haske ga fahimtar alqiblar siyasar

Nijeriya. Kasancewar a wannan bincike ana nazarin waqoqin siyasa ne, don haka za su taimaka qwarai wajen fahimtar ciki-da-waje na siyasar Nijeriya.

2.1.2 Nazarin Waqoqi a Kevantattun Lokutan Siyasa

Haka kuma akwai masana da manazarta da suka gabatar da bincike da nazarce-nazarce kan wasu kevantattun lokutan siyasa ko jamhuriya. A cikin ayyukansu, sun yi sharhi ko nazarci waqoqin siyasa na lokuta mabambata. Wasu sun kwatanta wasu waqoqin wani zamanin siyasa da na wani zamanin. Wasu kuma sun xauki wasu waqoqin wani zamanin siyasa suka nazarce su ta fuskoki daban-dabam. Waxannan masanan sun haxa da Babanzara (1980) da Birniwa (1987) da Dalladi (2003) da Funtua (2003) da Ajiwa (1998) da Adamu (2006) da Zainab (2013).

Babanzara (1980) ya duba waqoqi guda biyu ne da suka danganci zaven shekarar 1979 a Nijeriya. Waxannan waqoqin su ne: "Waqar Xan Masara" da kuma "Waqar Pii –Ar-Pii Rundunar Nasara", dukkansu na Aqilu Aliyu. Ya yi sharhin waxannan waqoqin gaba xaya, inda daga ciki ya duba salo da sarrafa harshe; ya duba Karin magana da kwalliya da tamka da aron kalmomi da sauransu.

Birniwa (1987) a aikinsa ya kwatanta waqoqin zamanin siyasar farko da na zamanin siyasa na biyu. Dukkan waqoqin da aka duba an yi sharhinsu cikin Hausa da Turancin Ingilishi. Masanin ya kwatanta waqoqin siyasar NPC/NPN a zamanin siyasa na xaya da kuma NEPU/PRP na zamanin siyasa na biyu, daga wajajen shekara ta 1946 zuwa 1983. Ya xauki waqoqi hurhuxu daga kowace jam'iyya daga cikin jam'iyyun can guda huxu da

aka ambata a sama. Dukansu ya yi sharhi a kan su, ya tsettsefe su ciki-da-waje ta fuskar salo da tsari da amsa-amo da kari da sauransu.

Ajiwa (1998) ya yi aikinsa a kan waqoqin siyasa. A cikin aikin nasa ya bayyana cewar daga cikin dalilan da ke sa ‘yan siyasa ke amfani da waqe-waqe don yayata ra’ayoyi da manufofi, shi ne domin an fi sha’awar waqa fiye da maganar da ake yi a zube. Ya duba waqoqin siyasa na mai da mulki hannun farar hula a zamanin Abacha. Ya xauki waqoqi guda uku ya yi sharhinsu tare da bayyana jigoginsu da muhimmancinsu ga mai da mulki a hannun farar hula. Ya xauki waqoqin Alhaji Sabo Wali da ta Muhammadu Umaru da ta Bello Zurmi. Sannan kuma Ajiwa ya xauki waqoqi guda biyar, xaya daga kowace jam’iyyun nan biyar na zamanin Abacha, su ma ya yi sharhinsu.

Waqoqin da ya duba su ne:

(i) “*Waqar CNC”* ta Shu’aibu Usman – Jigon waqar shi ne tallata jam’iyyu da kushe abokan hamayya.

(ii) “*Waqar Jam’iyyar DPN*” ta Garba Gashuwa mai jigon jawo hankalin jama’a zuwa ga jam’iyyar DPN.

(iii) *“Waqar Jam’iyyar GDM”* ta Muhammadu Xan-Shata wadda ke wayar da kan jama’a kan qudurori da kuma wayar da kan jama’a kan qudurori da manufofin jam’iyyar ta GDM.

(iv) “*Waqar Jam’iyyar NCPN*” ta Ibrahim Aminu Xandago wadda jigonta, shi ne tallata jam’iyyar da jawo hankalin mutane ga abin da ta qunsa.

(v) Sharhin *"Waqar jam'iyyar UNCP*" ta Lawal Musa Xan Qwari, mai jigon farfaganda da kuranta jam'iyyar.

Funtua (2003) ya duba waqoqin siyasa na Hausa a jamhuriya ta uku. A cikin aikin nasa ya duba yanaye-yanaye da sigogin waqoqin siyasa a jamhuriya ta uku. Ya bayyana waqoqi da yawa da aka samu a siyasar jam'iyya. Misali waqoqin NEPU da NPC da NPN da PRP da SDP da PDP da ANPP da sauransu. Funtua ya yi nazarin waqoqin ta fuskar sigoginsu da zubi da tsari da salon waqoqin da jigoginsu. Ya bayyana cewa waqoqin jamhuriya ta uku sukan fara da zubin buxewa da Basmala. Akan kuma sami zubin wasu waqoqin ba su da qayyadaddun xango a cikinsu, wato an faye samun taqadarun baituka. Ya ba da misali da waqar 'Yammedi da ya yi wa Alhaji Muhammad Abubakar Rimi mai suna "Tambari".

Adamu (2006) shi kuma ya duba tasirin waqoqi kan cigaban siyasa a jamhuriya ta huxu ta fuskoki kamar haka:

i. Jigo – A nan ya bayyana cewa an sami jigon neman dukiya a jamhuriya ta huxu.
ii. Zubi da tsari – ya bayyana cigaban da aka samu a jamhuriya ta huxu domin yawaitar ilimin zamani da shigowar baqin abubuwa ta fuskar sadarwa da qere-qeren kimiyya da fasaha.
iii. Salo – Ta fuskar salo ya bayyana cewa an sami bunqasar waqoqin siyasa a jamhuriya ta huxu. Shi ya sa ake samun wasu mawaqan siyasa na haxawa da kixa kamar yadda ya bayyana.

Dukan waxannan ayyuka suna da alaqa ta kusa- da- kusa da wannan bincike. Domin kuwa a cikin ayyukan, an yi nazari ne a kan waqoqin siyasa na wasu kevantattun lokuta ko zamanun siyasa , wato Jamhuriya. Kamar yadda a wannan binciken ma ya kevanta ga waqoqin siyasa na jamhuriya ta huxu. Don haka dukan ayyukan za su taimaka ga wannan binciken. Ganin cewar an nazarci waqoqi a Jamhuriyoyi daban-dabam tare da sharhinsu ta fuskar salo da tsari da sigoginsu da kuma jigoginsu da dai sauransu. Watau za a sami haske sosai a kan yadda za a gudanar da binciken cikin nasara.

2.1.3 Waqoqin Xaixaikun Jam'iyyu

Haka kuma a wasu nazarce-nazarcen da masana suka gudanar, sun yi su ne kacokam a kan waqoqin wasu xaixaikun jam'iyyun siyasa. A cikin ayyukan wasu masana sun zavi wasu jam'iyyu inda suka nazarci wasu daga cikin waqoqinsu. Daga cikin waxannan masana sun haxa da: Xiso (1997) da Yahaya (2000) da Binta (2007) da Ibrahim (2007) da Ibrahim (2009) da Yahaya (2010).

Xiso (1997) ya yi nazarin zambo da yabo a matsayin dabarun jawo hankali a rubutattun waqoqin siyasa na Hausa. A cikin aikinsa ya yi nazari tare da kawo zambo da yadda ake amfani da shi a cikin rubutattun waqoqin siyasar jam'iyyu na Hausa. Haka kuma, ya kawo misalin yabo a cikin waqoqin siyasa tare da yin nazari da kawo misalai na hanyoyin da yabo yake yin tasiri a rubutattun waqoqin siyasa na Hausa.

Yahaya (2000) ya yi sharhi ne a rubutattun waqoqi jam'iyyar PDP. A cikin aikinsa ya duba rawar da rubutattun waqoqin jam'iyyar PDP suka taka wajen xaukaka jam'iyyar,

musamman ta hanyar tallata ta a gidan rediyo. Ya yi sharhin waqoqi da suka haxa da: "Waqar iyata sarauniya" da "Waqar jam'iyyar mutane Nijeriya" da "*Waqar Qalubale*" da *"Waqar Garkuwa*" da "*Waqar Gaskiya dokin qarfe*" da kuma *"Waqar Qasidar Godiya"*. Ita kuwa Binta (2007), ta duba kamanci da bambanci da ke akwai tsakanin waqar "*Shegiyar Uwa"* da ta *"Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba*", na Haruna Aliyu Ningi, dukansu kuma na jam'iyyar PDP. A cikin aikin ta fara kawo tarihin Haruna Aliyu Ningi da tarihin siyasar Nijeriya. Sannan ta duba jigogin waqoqin Haruna Aliyu Ningi da suka haxa da gargaxi da faxakarwa da siyasa da suka haxa da waqoqin tallata jam'iyyar PDP da manufarta da kuma jigon yabo.

Shi kuwa Ibrahim (2007), ya gudanar da bincikensa ne a kan fa'idoji da illolin waqoqin siyasa. Kamar yadda ake cewa: "Komai yana da amfaninsa da rashin amfaninsa" to, ya tankaxe ya rauraye inda ya fito da fa'idoji da kuma illoli da waqoqin siyasa suke da shi. Daga cikin fa'idojin da ya kawo sun haxa da:

i. Faxakar da jama'a a kan shugabanci da waxanda suka cancanci zave.
ii. Nuna wa al'umma muhimmancin siyasa da yadda ya kamata *mulkin Dimokuraxiya* ya kasance.
iii. Wayar wa jama'a kai kan rajistar zave.

A nan kuma ya kawo misalai na waqoqi game da waxannan fa'idoji. Misali, ya kawo waqar da Abdullahi Rabo Yabo ya yi wadda ya kira "Siyasa Yanzu Ta Sake Hali". A

cikin waqar yana bayyana muhimmancin yin rajista. Sannan kuma ya kawo wasu daga cikin illolin waqoqin siyasa kamar haka:

i. Kawo gaba tsakanin ‘yan wata jam’iyya.

ii. Haddasa matsala ga matasa.

iii. Kawo matsala ga shugabanni da ‘yan takara da kuma manyan ‘yan siyasa.

Bayan haka, ya kawo salo da yadda ake amfani da shi a cikin waqoqin siyasa. Daga cikin irin salon da ya yi maganarsa sun haxa da salon kinaya da na kamance da na daidaito da kuma salon kamance da na fifiko. Sannan kuma ya yi nazarin wasu waqoqin siyasa kamar na jam’iyyun SDP da NRC da UNCP da sauransu. Ya kuma duba ire-iren jigogin waqoqin siyasa inda ya bayyana cewa jigogin sukan kasa waqa kashi-kashi kamar haka: Habaici da zuga da Zambo da kirari da wa’azi da sauransu.

Shi kuma Ibrahim (2009), ya duba waqoqin jam’iyyar PSP a Kano. Farko ya kawo tarihin mutanen Kano. Sannan ya yi bayanin canzawar tsarin shugabanci, daga daular Have zuwa daular Fulani, daga nan kuma zuwa tsarin mulkin Turawa, waxanda suka kawo Dimokuraxiya. Ya kuma duba kafuwar jam’iyyar PSP da kuma yadda mawaqan jam’iyyar PSP suka ba da gaggarumar gudunmuwa a jamhuriya ta uku.

Shi kuwa Yahaya (2010), ya yi bincikensa ne a kan waqoqin addini na siyasa inda ya nazarci waqoqin Emmanuel Wise mai Molo. Ya duba tarihin kafuwar Qungiyar qasashen musulmi ta Duniya (OIC), wadda ya bayyana da cewa ita ce Hukuma ta biyu mafi girma a duniya, bayan majalisar Xinkin Duniya (UN). Sannan kuma tana da wakilai daga

qasashe hamsin da bakwai (57) daga Nahiyoyi huxu daga cikin shida na duniya. Manufarta ita ce kare haqqin musulmin duniya da mutuncinsu da kuma tabbatar da zaman lafiya.

Haka kuma, Yahaya ya bayyana dangantakar siyasa da addini, inda ya nuna cewar siyasa da addini sun daxe suna haxe a Nijeriya. Wannan ya haifar da kai-ruwa-rana tsakanin Musulmi da Kirista game da shigar musulmin Nijeriya cikin qungiyar. Ya kawo misalin inda mawaqin ya tavo siyasar qasar waje inda yake bayyana adawar kiristoci dangane da kasancewar qasar Nijeriya cikin qungiyar a cikin "*Waqar OIC"*. Ya yi nazarin salo da tsarin waqoqin Emmanuel Wise mai Molo. Ya bayyana cewar ta fuskar salo an sami adon harshe; aka sami kamance da jinsintarwa da salon tambaya. Ta wajen tsari kuwa, ya bayyana ce waqoqin sun xan hau kan mizanin nazari kaxan. An kuma sami zubin waqa da qullin waqa da kuma saqon waqa.

Haqiqa akwai dangantaka ta kusa tsakanin waxannan ayyukan da kuma wannan aikin.

Idan aka duba aikin Xiso (1997), zai taimaka saboda ya yi magana ne dangane a zambo da yabo waxanda kuma su ne qashin bayan gina waqa, domin da wuya a shirya waqa ba tare da an samu duka ko xaya daga cikinsu ba. Don haka aikin ya taimaka wajen ba da haske na yadda aka zaqulo iren- iren waxannan a cikin waqoqin da za a nazarta. Yahaya (2000) ya yi sharhin rubutattun waqoqin jam'iyyar PDP ne, da suke xaukaka da kuma tallata jam'iyyar.

Haqiqan waxannan ayyuka sun taimaka ainun. Domin a wannan aikin ma, za a yi nazarin waqoqin siyasa ne na jamhuriya ta huxu masu tallata xaixaikun ‘yan siyasa ko kuma ‘yan takara. Shi ma aikin Binta (2007) da ta gabatar da aikinta a kan waqar “*Shegiyar Uwa”* da ta “*Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba*,” na Haruna Aliyu Ningi, ta duba jigogin waqoqin. Binciken Ibrahim (2007) ya duba fa’idoji da illolin waqoqin siyasa ne. Duk za su taimaka ga wannan aikin. Saboda an ce “abin biki na biki ne”. Kasancewar bincikensu game da waqoqin siyasa ne, kuma wannan aikin ma a kan waqoqin siyasa ne. Don haka, duk “bori xaya ake wa tsafi”. Haka su ma ayyukan Ibrahim (2009) da na Yahaya (2010), suna da muhimmanci ga wannan aikin. Domin kuwa dukansu sun yi magana game da waqoqi ne na siyasa. Ibrahim (2009) ya nazarci waqoqin siyasar jam’iyyar PSP. A yayin da Yahaya (2010), ya nazarci waqoqin siyasa, amma ta Musulunci, ba ta jam’iyya ba. Duk dai suna da muhimmanci a wannan aiki domin duk a kan waqa ne.

2.1.4 Waqoqin Xaixaikun Mawaqa

Bayani ya gabata cewar kowane manazarci da inda ya kalla a nazarinsa. Wannan ne ya sa wasu manazarta suka taqaita bincikensu kan wasu mawaqa da waqoqinsu. Saboda haka, an ci karo da wasu ayyukan da aka xauki waqoqin xaixaikun mawaqa na siyasa, ko wasu da ba na siyasa ba aka nazarce su.

Waxanda suka xauki waqoqin wasu xaixaikun mawaqa sun haxa da: Amin (2005) da Sa’adiyya (1983) da Bunguxu (1990) da Binta (1997) da Mu’azu (2002) da Tijjani (2002) da Daura (2004) da Salamatu (2006) da Ibrahim (2007) da Samira (2010).

Amin (2005), ya yi tarken Bakandamiyar *"Waqar Tabuka"* ta Audu Makaho, a inda ya tsettsefe ta ciki da waje. Binciken ya nuna cewar wannan waqar kandami labara ce a Hausa. An fahimci cewar waqar tana da siffofin waqar baka. Saboda binciken ya bayyana cewar ba ta da daidaitaccen tsarin baitoci. Domin tsarin baitocinta ya kama daga layi xaya zuwa shabiyar. Sannan kuma an lura waqar tana da amsa- amon kari ne da ake samu a rubutatta da kuma waqar baka (Amin, 2005: 163). Duk da kasancewar waqar kandamin labari, binciken ya nuna qarara cewar waqar tana da nau'o'in adabi da yawa da ake samu a cikin waqa, kamar sigar baiti da sigar zubin labari da karin magana da kirari da sauransu. Kirari, kamar yadda masana suka bayyana, fitaccen nau'i ne a adabin Hausa, wanda ake samun sa a cikin zube da kuma waqa, misali shi ne:

"....kashe kahuri, gaba da maqi- Sallah,
Manzon Allah Baqwan
Kwangam,Baqwan Badar...." (Amin, 2005: 167)

Haka ma daga cikin nau'o'in adabi da wannan waqar take qunshe da shi, ita ce karin magana. Masana da dama sun yi bincike a kan karin magana, inda suka bayyana ta da cewar ana auna qwarewar mutum a harshen Hausa ne ta yadda yake amfani da ita acikin maganganunsa.

Misali: *i. Durqusa ma wada ba yi hana miqewa.*
ii. Linzami ya fi qarfin bakin kaza.
(Amin, 2005: 167).

Haqiqa wannan aiki yana da alaqa da wannan bincike, kasancewarsa a kan abin da ya shafi waqa ne. Don haka, aikin ya taimaka qwarai wajen bad a haske ga fahimtar wasu daga cikin hanyoyin da ake nazarin waqa.

Zulyadaini, (2005), ya yi aiki a kan irin yadda mawaqa suke jefa karin harshe, maimakon daidaitacciyar Hausa, a wasu wurare cikin waqoqinsu. A cikin aikin nasa ya yi amfani da waqar "*Maraba da Soja'' ta Sa'adu Zungur.* Ya yi cikakken sharhi tare da kawo misalai na wuraren da ake samun irin wannan musayar. Sannan kuma ya yi amfani da ma'aunin waqa domin nuna Karin waqar wajen bayani domin tabbatar da hashensa a kan dalilan da ka sa mawaqa su yi amfani da wannan (ta amfani da Karin harshe). Daga cikin dalilan kuwa, su ne cewar mawaqin yana so ne ya cim ma burinsa na dabarun salo a cikin waqar, kamar su kari da amsa- amo da nuna martaba da sauransu. Wato mawaqa sukan yi amfani da karin harshe a wasu wurare domin karin waqarsu ya daidaita. Sa'adu Zungur a cikin waqarsa, *'Maraba da Soja,*' ya yi amfani da karin harshenSakkwato da na Bauchi da na Kano da na Katsina da kuma na Guddiri (na Katagum). Ya kawo misali a cikin waqar na inda Sa'adu Zungur ya yi amfani da Karin harshen Sakwwatanci domin ya tabbatar da katrin waqar na *Ramal*. Ga misalin:- v - - / - v - -

"Baabu halin zaa su daagee,
-v - - / v 4– v - -
Birbishinsuu akwai jiraagee
V2 v – v3. V4 – v - -
Ga su siiginaa maasu hange,
-v -7 / - v – 7/ - v - -
Rundunarsu ta zam buraagee,

-v - -. -5 / v4 – v - -
Sai a raamii baa halin fitoowaa."

Mawaqin a nan ya yi amfani da Karin Sakkwatanci a layi na huxu na wannan baitin inda y ace:

" Rundunarsuu ta zam buragee."
(Zulyadaini, 2005: 216).

Haqiqa wannan aiki ya taimaka matuqa lokacin gudanar da wannan binciken. Domin kuwa ya sa an fahimci abubuwa day a yawa da suka kamata duk mai nazarin waqa ya yi la'akari das u kamar amsa-amon waqa da yadda mawaqa kan yi amfani da Karin harshe a cikin waqoqinsu.

Ita Sa'adiyya (1983) ta xauki wasu waqoqin Mu'azu Haxeja ne ta nazarce su ta fuskar salo da sarrafa harshe. Daga cikin waqoqin da ta yi wa sharhi sun haxa da:

i. *"Waqar Gaskiya Ba Ta Sake Gashi".*
ii. *"Waqar Karuwa".*
iii. *"Waqar Tutocin Shehu da Waninsa".*
iv. *"Waqar Ilimin Zamani*".

Bunguxu (1990) ya yi nazarin waqoqin Auwalu Isa Bunguxu. Waqoqin da ya duba sun haxa da: "Varawon Akwati" da "*Waqar PRP Maganin Zamba*" da "*Waqar PRP ta Tsaya Gaskiya*", da sauransu. Ya nazarci waqoqin ta fuskar salo da zubi da tsari.

Ita kuwa Binta (1997) ta duba harshen waqa, inda ta yi nazari kan salon wasu waqoqin Soyinka da Osundare. Ta bayyana cewar harshen waqa yana iya sava wa qa'idojin

harshe, kuma fasihi, musamman mai shirya waqa yana da ‘yancin amfani da kalmomi yadda ya so. Ya ma iya kauce wa qa’idar wannan harshe. Haka kuma, a harshen waqa ana amfani da adon harshe , kodayake ana samun sa a harshen yau da kullum. Ta bayyana salo da cewa hanya ce da marubuci ke zaven kalmomi. Yana iya kasancewa mai armashi ko akasin haka, gwargwadon yadda aka yi amfani da shi.

Mu’azu (2002) ya xauki wasu waqoqi guda biyu na Sa’adu Zungur ya yi cikakken sharhi a kan su ta fuskar jigo da salo da tsari, sannan kuma ya kawo kamanci da bambanci tsakanin waqoqin. Waqoqin da ya nazarta su ne:

(i) *“Waqar Arewa, Jumhuriya ko Mulukiya*” ya bayyana jigonta da siyasa da farfagandar neman jan ra’ayin ‘yan arewa kan zavin irin gwamnatin da suke so a kafa masu.

(ii) “*Waqar ‘Yanci*” ita ma ya bayyana jigonta da siyasar ya kwatanta waxannan waqoqin guda biyu a cikin nasa. Ta fuskar jigo ya bayyana cewar duk sun yi kama domin duk na siyasa ne. A yayin da ta fuskar bambanci, ya bayyana cewar a yayin da ake fahimtar maganar jam’iya a “*Waqar ‘Yanci*”, a cikin “*Waqar Arewa Jumhuriya ko Mulukiya*” babu maganar Jam’iyyar siyasa.

Abdullahi, (2011), ya duba waqoqin Haruna Aliyu Ningi, inda ya kalli jigo da tsarin waqa da amsa-amo da salon sarrafa harshe da dai sauran abubuwan dubawa a cikin waqa. Waqoqin da ya yi sharhi a kan su, su ne:

i. *Waqar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba*

ii. *Waqar PDP Shegiyar Uwa Mai Kashe 'Ya'yanta*

iii. Waqar Atiku Abubakar 2007 mai suna *'Warwara'*

iv. *Waqar AC Jam'iyyar Talakawa*

Daga cikin salon sarrafa harshe ya kawo misalai na habaici da zambo da sauransu. Misali a waqar Haruna Aliyu Ningi ta *Shegiyar Uwa*, ya kawo misalin habaici a baiti na 30 a baiti kamar haka :

30. "*Jam'iyyar da ba a zave cikin ta,*
Sai naxi kawai ko ku yi ku bar ta,
Tunda mun ga har ta fita hayyyacin ta,
Mai kuke jira sai mu guje ta shegiya alga."
(Abdullahi, 2011 : 122)

A nan ya bayyana cewar mawaqin yana yi ne da jam'iyyar PDP a kaikaice.

Haka kuma, ya kawo misali na zambo a cikin waqar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba ta H aruna Aliyu Ningi, a baiti na 9 inda ya ce:

9 .*" Da akwai wani gwamna, muryarsa ya wanda ya sha giya,*
Dan-Daudu da jar hula yara ku kaxa masa nanaye,
Wai shi na tazarce ne mun gane abin da yake voye,
Shi Ribaxu yake tsoro ba wai haxuwa a qiyoma ba."
(Abdullahi, 2011: 137)

Abdullahi (2011) ya bayyana cewar a wannan baitin, Haruna Ningi ya yi zambo ne ga gwamnan jihar Yobe Bukar Abba Ibrahim.

Aikin Abdullahi haqiqa yana da dangantaka da wannan bincike, kasancewarsa shi ma, game da waqoqin siyasa ne. Sai dai, ya kalli waqar wani mutum guda ne, a inda wannan

aikin aka kalli waqoqin wata Jamhuriya. Duk da haka ya taimaka qwarai ga samun hasken da aka gudanar da wannan binciken. Domin kuwa, shi ma aikin nasa an gudanar shi ne kacokam a kan waqoqin siyasa.

Salisu (2011 : 46), ya duba salon sarrafa harshe a Waqoqin Aqilu Aliyu. Ya bayyana salon sarrafa harshe da cewar a gwari – gwari yana nufin dabarar jujjuya harshe da nuna gwaninta a cikin waqa. Ya duba abubuwa da dama a inda ya fexe biri har wutsiya dangane da abin da ya shafi salo a waqoqin Aqilu Aliyu. Daga cikin abubuwan da ya duba sun haxa da: Jituwar matani da jituwar xangaye da qarangiya da luguden kalmomi da tagwaicin baiti da fasalin gava da dai sauransu. Wannan aiki shi ma yana da matuqar muhimmanci a wannan bincike. Domin kuwa, ya ba da haske qwarai wajen gudanar da binciken, kasancewar salo na daga cikin abubuwan da aka nazarta a waqoqin da aka gudanar da nazari a kan su.

Shi kuwa Tijjani (2002) ya nazarci adon harshe a adabin baka. Ya bayyana cewa kalmomi ne guda biyu suka gina “adon harshe” wato “ado” mai nufin qawata abu da kayan kwalliya yadda zai ba da sha’awa ya kuma burge wanda ya gan shi. “Harshe” kuwa, ya bayyana shi da tunanin xan Adam da yake wanzarwa ta hanyar furuci da baki ko ta hanyar rubuta shi. Don haka ya bayyana cewa “adon harshe”, shi ne yi wa harshe kwalliya ta hanyar qawata shi da wasu zantuka ko kalmomi masu daraja ko fifita shi cikin hikima da fasaha.

A cikin aikinsa ya duba dangantakar adabin baka da adon harshe. Ya bayyana cewar kasancewar abin da xan Adam abin da ya fara mallaka a duniya, shi ne harshe, to wannan ne ya ba shi damar tunanin qirqirar adabi. Ya bayyana dangantakar adabin baka da harshe cewa ta qut-da-qut ce. Sannan ya nazarci yadda adon harshe ke kasancewa a adabin baka. Ya kuma duba nau'o'in kwalliya a cikin rakunonin adabin baka, kamar su tatsuniya da almara da hikaya da waqar baka da dai sauransu.

Tsoho (2002), ya qalailaice tare da tsettsefe hanyoyin da ake bayyana jigogin yabo a cikin waqoqi. Ya fayyace ire- iren kalmomin yabo da yawa da mawaqa ke amfani da su. Waxannan kalmomi ana amfani da su ta hanyoyi da dama a yabi mutum ko a kushe abokin hamayyarsa. Misali, mawaqa na amfani da sunayen dabbobi da sauran abubuwa a kwatanta mutane da su domin nuna yaba halayensu ta hanyar yabo da kirari da zuga ko kuma kushe wani a cikin waqa. Kalmomin sun haxa da :

i. *Dila* : Akan yi amfani da ita a nuna wayo.
ii. *Biri* Akan yi amfani da ita a nuna varna .
iii. *Mujiya* : Akan yi amfani da ita a nuna baqin- jini.
iv. *Fari* : Akan yi amfani da ita a nuna farin- ciki ko rashin mugunta.
v. *Raqumi* : Akan yi amfani da ita a nuna juriya da dai sauransu. (Tsoho, 2002: 144-145).

Haka kuma, Tsoho,(1987), ya yi nazarin waqar *"Kanzil Azimi, "* ta Aliyu Namangi, a inda cikin aikin nasa ya duba muhimman abubuwan da duk mai nazarin waqa ya kamata

ya duba. Abubuwan kuwa da ya yi magana game da su , sun haxa da: Jigo da salon tsari da ya haxa da karin waqa da amsa- amo da salon sarrafa harshe. Haka kuma, ya duba karin magana da kirari da mutuntarwa da tamka da kwalliya da sauransu.

Haqiqa waxannan ayyuka suna da matuqar muhimmanci ga wannan bincike. Domin kuwa, sun ba da haske sosai ta yadda aka fahimci abubuwa da dama da suka taimaka aka gudanar da wannan bicike. Kasancewar binciken an gudanar da shi ne a kan nazarin waqoqi.

Shi kuwa Daura (2004) ya xauki wasu waqoqin Jatau Kamba, ya nazarci jigon yabo a cikinsu. A cikin nasa aikin ya bayyana ire-iren jigogin yabo da mawaqan baka ke amfani da su a cikin waqoqinsu. Ya bayyana waxannan jigogi da cewa yabo yana da shika-shikai guda shida kamar haka:

i. Yabo ta fuskar addini.

ii. Yabo ta fuskar asali.

iii. Yabo ta fuskar hali.

iv Yabo ta fuskar jarunta .

v. Yabo ta fuskar kyauta.

v. Yabo ta fuskar mulki.

Ya nazarci waxannan nau’o’in yabo da misalai daga waqoqin da ya nazarta. Ya ba da misalin yabo ta fuskar addini a waqar da Jatau ya yi wa Sarkin Shikon Kamba, Alhaji Attahiru inda yake cewa:

"Makarinka sallah,
Gwarzon Sama'ila
Kowa ka tsahi,
Ba naka na ba ." (Daura, 2004: 59)

A vangaren iya mulki kuwa, ya ba da misali da waqar da Jatau ya yi wa Shugaban qasa na jamhuriya ta biyu, Alhaji Shehu Shagari inda ya ce:

"Mulkin Nijeriya sai kai,
Kowa ya riqa,
His she shi a kai ." (Daura, 2004: 75*)*

Ita kuwa Salamatu (2006) ta nazarci jigogin waqoqin bijirewa na siyasa. Ta kalli iren-iren jigogin da ake samu a cikinsu. Ta dubi ma'anar waqoqin bijirewa, da ta bayyana da cewa su ne waqoqin da ke nuna qi ko mayar da martini ko adawa ko kuma sukar ra'ayi dangane da wani abu cikin waqe.

Sannan kuma ta duba taqaitaccen tarihin samuwar siyasa da yadda aka samu waqoqin bijirewa na siyasa. Ta bayyana cewar waqar Sarki Attahiru, ita ce waqar bijirewa ta farko kafin shigowar siyasar Jam'iyya a Nijeriya. A siyasar Jam'iyya kuwa, akwai waqoqi masu yawa da aka rubuta. Daga ciki, ta kawo misalin waqoqin NPN da PRP da GNPP da sauransu. Misalin waqoqin sun haxa da: *"Waqar Ku Zo Mu Taru Mu Zavi PRP"* ta Auwalu Isa Bunguxu da "*Waqar 'Yan Santsi Kun Zama Kaya"* ta Muntari Sabo. A cikin aikin nata, ta bayyana cewar jigon bijirewa guda xaya ne. Wato nuna qiyayya ga abu ko yaqi da shi. Sai dai ta bayyana cewar akwai hanyoyi da yawa da ake bi a bayyana bijirewa da suka haxa da: mayar da martani da habaici ko shaguve ko gugar zana da yaxa

manufa da sauransu. Ta ba da misali da waqar Aqilu Aliyu ta "*Baqi Uku Sharrin NPC"* ta bijire wa NPC. Sai kuma "*Waqar 'Yanci*", ta Sa'adu Zungur wadda a ciki yake bijirewa ga NPC, da sauransu.

Shi kuma Ibrahim (2007) ya xauki rubutattun waqoqin siyasa na Haruna Aliyu Ningi, inda a ciki ya bayyana jigogin yabo da zambo. Bayan ya bayyana tarihin marubucin waqoqin, sai kuma ya yi bayanin yadda aka yi amfani da yabo da zambo a cikin waqoqin.

Ya bayyana waqa da cewa ruhi ne na siyasa wadda tana daga cikin ginshiqan da siyasa ke qara kafuwa da ita. Ya ba da muhimmancin yabo a cikin waqoqin siyasa. Domin kamar yadda ya bayyana, ta fuskar yabo ne ake yabon jam'iyya ko 'yan takara, tare da fito da manufofin jam'iyyu da yaxa su ga jama'a. Ta fuskar jigon Zambo kuwa, mawaqi na muzanta wani xan takara ko jam'iyyarsa ko kuma su nuna gazawar shugabanni da 'yan takarar da suke cikin jam'iyyun hamayya.

Ita kuma Samira (2010), ta xauki waqoqin siyasa na Abdullahi Stim ta nazarce su. Bayan taqaitaccen tarihin marubucin, ta kawo wasu hanyoyin nazarin rubutattun waqoqin Hausa. Sannan ta kawo wasu daga cikin waqoqin Abdullahi Stim, ta nazarci jigoginsu. Ta bayyana cewa mawaqa na amfani da jigogin da suka haxa da: Habaici ko Zambo da kambamawa da roqo da tarihi da tallatawa da kuma yabo.

Mai binciken ta yi amfani da wasu waqoqin jam'iyya a matsayin misali, inda ta duba jigogin da aka ambata a sama. Daga cikin jam'iyyun da ta xauka sun haxa da UNCP da

SDP da kuma ANPP. Sannan ta xauki wasu daga cikin waqoqin ta baje su a faifai ta fitar da jigoginsu dalla-dalla.

A cikin jigon talla, ta bayyana cewa tallatawa na nufin fitar da jam'iyya a fili da kyawawan manufofinta domin mutane su so ta, ko su aminta da ita. Ta ba da misali da waqoqin da Abdullahi Stim ya yi wa jam'iyyun UNCP da SDP, domin tallata su tare da manufofinsu. Misali, a waqar SDP da Abdullahi Stim ya yi yana cewa a baiti na shida:

6. *"Jam'iyyar da ta dace,*
Mu yi wannan mai kalar tsanwa,
Da farin dokinmu ingarma,
SDP jam'iyyar manya,
Don kar mu bi jam'iyyar maiki".
*(*Samira, 2010: 38).

Haka kuma, ta duba ire-iren salailan da gwarzon nata ke amfani da su a cikin waqoqinsa. Daga cikin salailan akwai aron kalmomi da salon amshi da kinaya da sauransu. Alal misali, ta kawo yadda Abdullahi Stim ke amfani da kinaya a baiti na takwas cikin waqarsa ta UNCP inda yake cewa:

8. *"Kura da Dila ba mu yarda ba,*
Don ba za ku biya quri'armu ba,
Mun san ku idan ba ku san mu ba,
Mu ba za mu aminta da riqon ku ba,
Ba ruwanku da son ku yi gaskiya."
(Samira, 2010:44).

Dangantakar ayyukan nan da wannan aiki ta bayyana qarara, a inda Sa'adiyya (1983) ta xauki waqoqin Mu'azu Haxeja ta nazarta. Wannan zai taimaka ga wannan bincike, domin ta bi hanyoyin da ake nazari ko sharhin waqa. Don haka aikinta zai ba da haske ga

wannan bincike, duk da cewa shi a kan waqoqin siyasa ne. Aikin Bunguxu (1990) shi ma zai taimaka a wannan binciken. Domin kuwa kai tsaye aikinsa a kan waqoqi siyasa ne. Ya nazarci waqoqin Auwalu Isa Bunguxu a keve, a yayin da wannan bincike ya duba waqoqin siyasa na jamhuriya ta huxu da suke tallata xaixaikun ‘yan siyasa a qarqashin wasu jam’iyyu. Ita kuwa Binta (1997) ta duba salon sarrafa harshe ne a waqoqin Soyinka da na Osundare. Shi ma wannan aikin zai taimaka qwarai. Domin kuwa, duk da cewar a wannan binciken kan waqoqin siyasa ne aka gabatar da shi, amma dai salon sarrafa harshe na daga cikin abin da aka duba. Don haka, shi ma zai ba da haske qwarai da gaske wajen sanin makamar wannan bincike.

Haka kuma ayyukan Mu’azu (2002) da na Salamatu (2006) da na Ibrahim (2007) duk sun yi magana ne game da waqoqin siyasa. Sun duba jigogi ta fuskoki daban-dabam. Daga cikin jigogin akwai siyasa da yabo da sauransu. Don haka, waxannan ayyuka suna da alaqa da wannan aiki, kuma za su taimaka ainun. Haka ma aikin Samira (2010) da ta nazarci waqoqin siyasa na Abdullahi Stim, ita ma aikinta na da alaqa da wannan aikin. Domin kuwa ta xauki wasu jam’iyyu ta nuna yadda ake tallata su a cikin waqa. Haka ma a wannan bincike an xauki wasu waqoqi daga wasu jam’iyyu a cikin jamhuriya ta huxu da suke yaba ‘yantakara da tallata su ga jama’a domin a zave su. A cikin aikin an nazarci ire-iren waqoqin da suke tallata xaixaikun ‘yan siyasa ko ‘yantakara. Don haka aikin zai taimaka ga wannan binciken.

2.1.5 Waqoqi a Kan Talla da Farfaganda

Haka kuma wasu sun yi ayyukan a kan talla da farfagandar siyasa da kuma farfagandar shugabanci da al'amuran rayuwa daban-dabam. Daga cikin masana da manazartan da suka yi aiki a wannan fage sun haxa da: Amin (2006) da Muhammad (2007) da Dalladi (2003) da Ibrahim (2012) da Zainab (2013) sun yi aiki a kan abin da ya shafi yaxa manufa da tasirin farfaganda a tallar 'yan siyasa.

Amin (2006), ya nazarci waqoqin Hausa na siyasar addini, waxanda suke nuna yaxa manufa da jaddada addinin Musulunci. Ya yi waiwayen wasu daga cikin qungiyoyi da xaixaikun malamai da suka yi qoqari jaddada addinin Musulunci. Wannan binciken kuwa, ya xauko tun daga tushe,inda ya fara bayar da misali da Shehu Usmanu Xanfodiyo a qarni na shatara da Sarkin Musulmi Attahiru na II a 1903. Haka kuma, ya bi diddigin yadda qungiyoyi suka taimaka da gudunmuwa wajen jaddada addinin Musulunci a arewacin Nijeriya. Misali, Qungiyar Izala qarqashin Marigayi Abubakar Gumi da Qungiyar 'Yan'uwa Musulmi qarqashin El Zak- Zaky (Amin, 2006:235- 236).

A cikin binciken da ya gudanar, ya raba jigogin waxannan waqoqi zuwa gida biyu; wato masu qunshe da jigon addini da gyaran hali da cusa aqida da kyawawan xabi'un addini. Ya kawo misali daga "*Waqar Musulunci* " ta Abdulmuni Bauchi, inda ya ce:

'Ni na yi kiran Musulmi mu san,
Matashi mai hamasa ka san,
Rashin ilimi iyakar tsiya.'

A nan yana nuna muhimmancin ilimi ne a cikin addinin Musulunci,domin sai da shi za a san yadda za a bauta wa Allah (Amin, 2006 : 237 .)

Sannan kuma, akwai waqoqi masu jigon yaxa manufa da siyasar zamantakewar Musulunci da qarfafa Daular Musulunci. Ya ba da misali da Waqar Rayuwar Musulunci ta Aliyu Rabi'u, inda ya ce :

''Ka daxo rahama gurin Shehuna bini Fodiyo,
Wanda ya hana yin bokanci.
Lallai haqiqa shi masoyin Allah ne
Wanda ba ya son kafiraci.
Mu ma a yau ga shi muna ta kira,
A daina bin tsarin Kafirci.'' (Amin, 2006: 239).

Haqiqa wannan aiki ya taimaka qwarai wajen gudanr da wannan bincike da aka gudanar. Domin kuwa binciken a kan waqoqi ne, kuma na siyasa, duk da cewar siyasar Musulunci ce. Duk da haka, ya ba da haske ainun wajen fahimtar yadda mawaqa ke amfani da waqoqi wajen yaxa manufofi. Don haka, an yi amfani irin dabarar da aka bi aka nazarci waqoqin siyasar Jam'iyya.

Muhammad (2007), a cikin aikin nasa ya nazarci tarihi da ma'anar talla, haka kuma ya duba tarihi da ma'anar farfaganda, fa'idojinta da matsalolinta. Amma game da fa'idojin farfaganda, ya nuna cewa mai yin ta ne kaxai ya san irin fa'idar da zai samu. Haka ma ta vangaren matsalolinta, ita ma, mai yin ta ne ke iya tantance irin matsalolin da ya ka iya fuskanta. Sai dai, matsala ta zahiri, ita ce xaukar nauyin alhakin duk abin da ya biyo bayan yin farfagandar.

Game da ma'anar talla ya nuna amincewarsa da ra'ayin Josef (2000) da ya bayyana talla da wata hanya ta sanarwa ta amfani da dabarun sadarwa ko isar da saqon wani abu na

koyo ne ko aiki ne, ko kuma wata haja ko ra'ayi ne wanda wani ya bayyana na kansa domin a yi masa wannan tallar domin cin gajiyar kansa. A aikin ya kawo misalan tallace-tallace da suka haxa da tallar Alhaji Aminu Bello Masari xan takarar Majalissar Tarayya da Alhaji Ahmed Maqarfi xan takarar gwamnan Jihar Kaduna da ta Alhaji Ibrahim Shekarau xan takarar gwamnan Jihar Kano, da sauransu.

Haka kuma ya bayyana ma'anar farfaganda ta gaba xaya, da kuma a siyasance. Sannan kuma ya kawo ire-iren farfaganda. Ya bayyana farfaganda kamar haka:

> *"Yaxa wani sabon abu musamman na magana ko na kwatance ko na zane da nufin mutane su karva su yarda da shi farfagandar wanda a qarshe mai wannan shi ke cin gajiyar*."
> *(*Muhammad, 2007:45)

A siyasance kuma ya bayyana cewar kalmar farfaganda, mutane na kallon ko ganin abin ne da nufin kushe ko muzanta wani abu ko kuma canza ra'ayin mutane kan wani abu ko lamari. Muhammad ya ba da nau'o'in farfaganda guda uku kamar yadda ya bayyana cewar Wilfred (2006) ya qwanqwance su. Ga su kamar haka:

i. **Farar Farfaganda**: Ita ce mai tsabta ba qarya ko yaudara ciki ta kowace fuska. Misali: tallar Muhammadu Buhari wadda Bashir Isma'ila Ahmed ya yi masa.
ii. **Fatsi-fatsi ko jirwayen Farfaganda**: Ya ba da misali da tallar da Bashir Isma'ila Ahmed ya yi wa Ahmed Maqarfi.
iii. **Baqar Farfaganda:** Ya kawo misalin Bush da Saddam kan makamin qare-dangi.

Haka kuma ya kawo nau'o'in talla inda ya kasa ta zuwa tallar gargajiya da ta zamani. Ya nuna cewar a tallar gargajiya ana amfani da irin su waqa da kirari da take da kuma zube wanda ake ba da labarin wani abu a magance shi. Nau'o'in tallar zamani kuwa sun haxa da ta rediyo da jarida da allunan kan titi da talabijin da yanar gizo da sauransu.

Shi kuwa Dalladi (2003) ya yi bincikensa ne a kan tallar 'yan siyasa a gidan Rediyo Nijeriya na Kaduna a jamhuriya ta huxu. Ya duba abubuwa da dama da suka haxa da talla da ire-irenta a gidan rediyo. Ya yi sharhin yadda ake tallata jam'iyya da 'yan takara a gidan rediyo. Ya bayyana ma'anar talla kamar haka:

> *"Talla tana nufin yaxawa ko yekuwa ko sanarwa a kan wani abu ga mutane, kowa kuma yana amfani da irin harshensa domin tallata hajarsa ko manufarsa daidai matsayi da kuma yanayin sana'arsa ."*

Haka kuma, ya zayyana ire-iren talla a gidan rediyo da suka haxa da: tallar cimaka da tallar kayan masarufi da ta takin zamani da bankuna da ilimi da sauransu. Sannan kuma, ya yi cikakken sharhi da misalan tallata 'yan takara a Gidan Rediyo Nijeriya na Kaduna. Daga cikin tallar da ya kawo ta haxa da ta Obasanjo da Atiku na PDP da kuma tallar gwamnan Jihar Kebbi a jam'iyyar UNPP da tallar Sardaunan Gumel da jam'iyyar PDP da sauransu.

Shi kuwa Ibrahim (2012) ya yi nazarin harshen talla ne, inda ya bayyana salailai da dama da ake talla da su, da suka haxa da sarrafa harshe ta fuskar amfani da kirari da karin magana da qarangiya da waqa da sauransu. Ya bayyana ma'anar talla kamar haka:

> *"Talla tana nufin hanya ce da ake amfani da ita dan isar da saqo zuwa ga jama'a ta amfani da Hausar da za ta iya jan hankulan jama'a su sayi ko su yarda da wata manufa ko saqo".* (Ibrahim, 2012: 36).

Ibrahim ya karkasa ire-iren talla a qasar Katsina da suka haxa da:

i. Tallar abinci da abin sha.
ii. Tallar magungunan gargajiya.
iii. Tallar kayan buqatu na rayuwar yau da kullum.
iv. Tallar kayan qawa.
v. Tallar bukukuwa/taruka.
vi. Tallar yaxa manufa.
vii. Tallar siyasa.

Ita kuwa Zainab (2013) ta gudanar da bincikenta ne a kan farfaganda a cikin waqoqin Hausa na zamani da ake amfani da kayan kixa na zamani kamar su jita da fiyano da tasoshi da sauransu. A cikin aikinta ta yi binciken qwaqwaf kan ire-iren waqoqin zamani waxanda ba su da alaqa da jam'iyyun siyasa, amma suna yaxa farfaganda kan faxakar da al'umma game da irin yadda 'yan siyasa ke shugabantar su da kuma halayen shugabanni

da suke yi wa talakkawa na “kashin dankali”. Ta haka ne waqoqin suke faxakar da al’umma game da gwamnati, da kuma faxakar da jama’a zuwa ga yi wa gwamnati bore da tawaye kan yanayin yadda ake gudanar da mulki.

A cikin aikin nata, ta bayyana cewar ire- iren waxannan waqoqi sun jivanci abubuwa guda huxu kamar haka:

i. Yanayin mulki.
ii. Addini
iii. Tattalin arziki
iv. zamantakewa

Zainab ta duba waqoqi masu yawa, tare da yin cikakken sharhi a kan su, da fexe biri har wutsiya game da jigoginsu. Daga cikin waqoqin da ta duba sun haxa da: “Waqar Baubawan Burmi” da ta “Xaurin Gwarmai”; na Aminu Ala da “Waqar Mafarkin Mulki I”, ta Jibrin Jalatu, mai nuna yadda cin hanci ya zama ruwan dare a Nijeriya, inda ake ba sarakuna kuxi don su ba gwamnati goyon baya. Haka kuma ta nazarci “Waqar Rigar ‘Yanci” ta Abdul’aziz Abdullahi Ningi, da take nuna yadda ake yin naxi a tsarin shugabancin Nijeriya, maimakon zave. Sannan kuma da “Waqar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba” ta Haruna Aliyu Ningi, da take jawo hankulan ‘yan qasa da su lura da makircin shugabanni da rashin kishin qasa da son dawwama a gadon mulki da tazarce da yawan varnar da suke tabkawa. Waxannan dai kaxan daga cikin waqoqin da ta duba ne.

Haqiqa duka waxannan ayyuka suna da alaqa da wannan aiki. Don haka za su ba da haske da samar da alqiblar gudanar da binciken. Domin ayyukan Sa'adiyya (1983) da Bunguxu (1990) da Binta (1997) da Mu'azu (2002) duk sun ce wani abu game da salo a cikin waqa. Daura (2004) da Salamatu (2006) da Samira (2010) sun yi sharhin jigogin wasu waqoqi. Wannan aiki zai amfana matuqa, domin a cikin binciken salo da jigo na daga cikin abubuwan da za a duba a cikin waqoqin da za a yi nazari a kan su. Haka ma Dalladi (2003) da Ibrahim (2012) da kuma Zainab (2013) sun yi magana a kan farfaganda da talla. Wannan ayyukan su ma za su taimaka ga wannan aikin. Domin zai taimaka a rarrabe tsakanin talla da kuma farfaganda. Duk da cewa a wannan binciken ana duba waqoqin siyasa ne da suke tallata xan takara a qarqashin jam'iyyun siyasa na jamhuriya ta huxu.

2.2 Bugaggun Littattafai

An sami littattafai da yawan gaske da ko dai suke maganar siyasa ko waqoqin siyasa ko kuma duka biyun. Domin a halin yanzu ana iya cewa da siyasa da waqoqinta, kamar "Xanjuma" ne da "Xanjummai", saboda "Bori xaya suke wa tsafi". Gusau (2008:5) ya bayyana cewa xan'adam mutum ne mai son yin tsokaci bisa xabi'arsa wanda kuma rayuwar yau da gobe da yadda al'amura suke faruwa ke tabbatar da haka. Wannan ya sa ake samun wasu fasihai su gina waqa a kan wata siyasa ko xan takara don bayyana ra'ayinsu.

William F. Arens da wasu (2008:7-8), sun bayyana cewa talla takan fita a yanayoyi iri-iri kamar a mujallu da alluna da kafofin yaxa labarai. A farkon qarni na ashirin (20) kafin samuwar rediyo da talabijin, sun ruwaito wani masani Albert Lasker da ya bayyana talla da cewa:

> *"Talla na nufin bayyana abun sayarwa ko wasu manufofi a rubuce.*"

Daga baya kuma aka bayyana talla da cewa:

> *"Talla na nufin sadarwa ko hulxa ko kuma hanya ta lallashin jama'a."*

William da wasu, sun ci gaba da bayyana cewa talla ta kai matsayin da ake amfani da ita domin bayyana wasu manufofi, ko dai waxanda suka shafi tattalin arziki ko siyasa ko na addini ko kuma na zamantakewar rayuwar jama'a.

Don haka, wannan aiki zai taimaka qwarai ga mai wannan bincike. Domin kuwa, aikin ya fayyace mana abin da tallar ta qunsa cewar har da lallashin jama'a da kuma yaxa manufofin siyasa. Saboda haka, za a fahimci cewa salon waqoqin da ake yi na tallata 'yan takara, ana yin su ne domin lallashin jama'a su zavi 'yan takara na wata jam'iyya. Savanin shirya waqoqin da suke bayyana manufofin jam'iyyun siyasa da kuma aqidun 'yan siyasar kansu.

Xambatta (2010) da Daure (2000) sun ba da tarihin Nijeriya da irin gwagwarmayar da aka sha ta neman 'yancin kai daga hannun Turawan mulkin muluka'u. Sannan kuma sun bayyana yadda siyasar Nijeriya ta ginu tun daga lokacin da aka sami 'yanci (1960) da

yadda aka kafa jam'iyyun siyasa daga jamhuriya ta farko (ta su Sardauna) har zuwa wannan jamhuriyar da ake ciki.

Su kuwa Paden (2008) da Umaru (2003) da Hiskett (1977), bayan sun tavo ginuwar siyasa a Nijeriya da tarihin gudanar da mulki, sun kuma yi sharhi a kan abin da ya shafi zave. Paden, ya xauki Nijeriya a matsayin qasa ta gwaji ta fuskar siyasar duniya. Saboda a ganinsa, Nijeriya ce take da yawan qabilu sannan kuma ga yanayin zamantakewar al'ummar qasar. Ya nuna cewa tsakanin kudu da arewa ne ake gogayya. Kuma arewa musulmi suka fi yawa, a kudu kuma kiristoci suka fi yawa. Ya yi maganar tsarin karva-karva a siyasar Nijeriya. Ya kuma bayyana Nijeriya

ciki-da-wajenta da dangantakarta da sauran qasashen duniya. Paden (2008) ya duba yadda aka gudanar da zave a 2007, musamman inda ya fi ba da qarfi a Katsina ne inda ke da 'yan takarar shugaban qasa guda biyu; Umaru Musa 'Yar'adua a PDP da kuma Muhammadu Buhari a ANPP. A cikin littafin ya yi cikakken bayani na siyasar Nijeriya da tattalin arziki da addini da dai sauransu.

Shi kuwa Umaru (2003) ya ba da tarihin Nijeriya daga 1960-2003 a siyasance, ya tattauna yadda aka yi gwagwamayar kafa Nijeriya a matsayin 'yantattar qasa. Ya kuma duba kafuwar siyasar jam'iyyu tun daga jamhuriya ta farko har zuwa 2003. Bayan wannan babban abin da ya karkata gare shi, shi ne dokokin zave da kuma irin hanyoyin da 'yan siyasa ke bi suna tabka maguxi. A nan ya taqaita ga zaven 2003 inda ya kawo hanyoyi arba'in da biyu (42) da 'yan siyasa suka yi amfani da su wajen tabka maguxin

zave. Misali amfani da wasu rumfuna da babu su a zahiri da ba da cin hanci ga jami'an zave da surar akwati da karkatar da kayan zave da sauransu.

Haqiqa waxannan ayyuka za su taimaka a wannan binciken. Domin kuwa ana cewa "abin biki, na biki ne." ai abin da ya shafi siyasa, ya shafi waqoqinta. Saboda kamar yadda aka bayyana a baya, abubuwa da yawa na son yin sharhi ko tsokaci ga xan'adam, na haifar da waqa. misali harzuqa mutane wajen tabka maguxin zave, na haifar da samuwar waqa.

Shi ma Hiskett (1977) ya tavo taqaitaccen tarihin Nijeriya da na yadda tsarin shugabancinta ya kasance tun daga 1900, lokacin Turawan mulkin Ingila suka kafa tungarsu ta mulkin mallaka. Ya bayyana yadda aka yi mulkin mallaka har lokacin samun 'yancin kai a 1960, qarqashin Firayim Minister na farko, Alhaji Abubakar Tafawa Valewa. Sannan har zuwa kashe Janar Murtala a 1976, lokacin da aka mai da Nijeriya qarqashin jihohi sha- tara. A wannan lokacin ne Janar Obasanjo ya hau shugabancin qasa a matsayin soja.

Ta fuskar siyasa da waqoqi su ma akwai littattafai masu tarin yawa. Misali Adamu (2007) da CNHN (2006) da Furniss (1996) da Muhammad (ed. 1990) Yahaya (1988) da Kafin Hausa (1983) da Abdulqadir (1974) da Hiskett (1977) da Sani (2011) da Junaidu (1981) da sauransu, duk sun maganta kan abin da ya shafi waqa.

Adamu (2007) ya yi magana kan hanyoyi da dabaru da ake bi a fexe waqa. Da irin abubuwan da ake dubawa kamar zubi da salon sarrafa harshe da sauransu. Misali, a salo da sarrafa harshe ya bayyana irin abubuwan da ake dubawa a cikin waqa kamar karin

magana da karin harshe da aron kalmomi da sauransu. A ciki ya ba da misalai da waqoqi da yawa; kamar waqar “Hausa Mai Ban Haushi” ta Aqilu Aliyu da waqar “Arewa Jamhuriya Ko Mulukiya” ta Sa’adu Zungur.

Kasancewar wannan bincike ya shafi waqa, ke nan wannan aiki zai zama abin alfahari kuma abin koyi a gare mu. Musamman yadda marubuci ya tavo har da waqoqin siyasa ya yi bayaninsu. Misali waqar “Arewa , Jamhuriya Ko Malukiya” ta Sa’adu Zungur. Ga ma misalin da ya bayar game da abin da ya shafi salon aron kalmomi a cikin waqar:

*Allah **Sudda** asiri a duniya*
*Jikan **modibbo** subaxo sai,*

Ka tsare daularka da gaskiya.
***Jaumirawo** ya taimaki **julve** duk.*

CNHN (2006) a cikin wannan littafin an kawo tarihin uku daga cikin shahararrun marubuta waqoqin Hausa da irin gudunmuwar da suka ba da a fagen raya adabin Hausa, musamman waqa. Waxannan mutane uku su ne:

i. Malam Lawan mai Turare

ii. Alhaji Mudi Sipikin

iii. Alhaji Aqilu Aliyu

Waxannan mutane sun ba da gagarumar gudunmuwa ga harshen Hausa, tun ba ma raya adabinsa ta fuskar waqoqi ba. Sun rubuta waqoqi da dama da suke magana kan fannoni daban-daban na rayuwa, ciki kuwa har da waqoqin siyasa.

A cikin wannan aiki an bayyana tubalan da ake gina nazarin waqa a kai. Muhimmai daga ciki su ne: Jigo da zubi da tsari da salo da sauran dabarun salon sarrafa harshe da tasirin adabin baka da jawabi kan tsarin adabin baka.

Kasancewar dukkansu mutanen nan gwarzaye ne kuma suna cikin siyasa, an nuna gudunmuwarsu ga waqoqi. Misali, Malam Lawan mai Turare ya rubuta waqoqi da suka kai sittin da biyu (62, a lokacin rubuta littafin) amma mafi rinjayensu duk na siyasa ne. Ga ma waqoqi guda 4 da ya ce ya fi so daga cikin waqoqinsa, waxanda kuma na siyasa (NEPU) ne:

i. *"Sadaukar da rammu ga Nijeriya,*

ii. *"Zavi tauraron sawaba,*
Bar fartanya fisi banza,"

iii. *"ya 'yan NEPU muna yawa,*
Zalumai kun canja baqin zama,"

iv. *"Azzalumai kun wahal,*
Kun yi asarar banza,"

Sannan kuma an kawo waqa guda-guda ta kowane fasihi kamar haka:

i. Alhaji Lawan mai Turare-*Waqar komawa ga Allah.*

ii. Alhaji Mudi Sipikin -*Waqar Gadar Zare.*

iii. Alhaji Aqilu Aliyu- *Waqar Kadaura Babbar Inuwa.*

Babu shakka shi ma wannan aiki ba abun yadawa ba ne, domin zai taimaka a kai ga tudun-mun-tsira a wannan bincike.

Furniss (1996) ya bayyana yadda arewa take qoqarin kare kanta daga danniyar da ‘yan kudu ke yi musu a siyasance (shugabanci) bayan samun ‘yanci. Ya tattauna siyasun da ake da su a arewa, NEPU da NPC. Waxannan jam’iyyu sun kasance abokan hamayyar juna. A kan haka ake samun waqoqin da suke musayar maganganu don kushe juna da kuma neman karvuwa ga jama’a. Jam’iyyun NEPU da NPC su ne aka yi yayin zamanin siyasa ta farko daga wajajen 1950-1960, su ne kuma suka rikixe zuwa PRP da NPN a jamhuriya ta biyu a 1979, amma da wasu jam’iyyu kamar GNPP a arewacin Nijeriya.

Furniss ya ruwaito cewa Birniwa (1987) ya yi cikakken nazari a kan waqoqin waxannan jam’iyyu (watau jam’iyyun jamhuriya ta farko da ta biyu). A cikin aikin nasa kamar yadda ya bayyana, ana amfani da waqoqin wajen yabon shugabannin jam’iya sannan kuma abokan hamayya na amfani da waqoqin wajen kushe shugabanni da suke ganin suna yi masu danniya. Kan haka Furniss (1996: 228-233) ya tattauna ire-iren waxannan waqoqi. Ya buga misalansu da waxannan waqoqi:

i. *“ Waqar yabon Sardauna,” ta Shekara Sa’ad*
ii. *“ Waqar Arewa Jamhuriya kawai,” ta Mudi Sipikin*
iii. *“ Waqar a Yau Ba Maqi NEPU Sai Wawa,” ta Gambo Hawaja.*

Saboda haka, idan aka duba za a ga cewar wannan aiki ya dace duk mai bincike irin wannan ya duba shi. Dalili kuwa ya haska mana kandamin aikin nan na Birniwa (1987)

da ya yi a kan waqoqin siyasa na jamhuriya ta xaya da ta biyu, wanda kuma ya kamata a ce duk mai aiki irin wannan ya duba shi.

Muhammad (ed. 1990) ya kawo mafi yawan kevavvun kalmomin da ake amfani da su a fagen nazarin harshen Hausa, musamman ma fannin nazarin adabin Hausa. A ciki akwai kalmomi da dama da suka shafi nazarin waqa. Misali:-

i. amsa-amo (rhyme(s)).
ii. Aruli (prosody)
iii. Fasahar baka (orature)
iv. Waqar baka (oral poem)
v. Mai zalaqa (orator)
vi. Rauji (rhythm)
vii. Adabin baka (oral literature) da sauransu.

Wannan aiki haqiqa ba qaramin taimako zai yi ba a wannan aiki. Domin kuwa ta wannan aiki za a iya sanin kalmomin da ake amfani da su fagen nazari. Saboda ya nuna cewa ba kowace kalma ce za a yi amfani da ita ba, a'a akwai kevavvun kalmomi na musamman. Wajibi ne mai bincike ya san su, da inda ya kamata ya yi amfani da su.

Shi kuwa Yahaya (1988) ya rubuta babban kundi na nazarin adabin Hausa, musamman abin da ya shafi rubuce-rubuce wanda ciki har da waqoqi; samuwarsu da havakarsu a qasar Hausa.

Dangane da samuwar rubutattun waqoqi ya kawo tarihinsu tun kafin jihadi har zuwa lokacin jihadi da ma bayan jihadi. Ya kawo gudunmuwar malamai a qarni na 17 kamar

ayyukan su Wali Xan Marina da Wali Xan Masani. Sannan a qarni na 18 an sami malamai irin su Malam Muhammadu bn Muhammad al-Katsinawi da Malam Muhammadu na Birnin Gwari da Malam Shitu Xan Abdurra'ufu.

A qarni na 19 kuwa ya kawo gudunmuwar malaman Jihadi ne, Shehu Usman Xan fodiyo da jama'arsa. Dukkan waqoqin wannan qarni na addini ne. Sai dai ko a cikinsu akwai masu magana a kan siyasar Musulunci (shugabanci). Misali, akwai "Waqar Tsarin Mulki Na Musulunci," da "Waqar Murnar Cin Birnin Alqalawa," dukansu na Shehu Abdullahi Fodio. Haka ma a qarni na 20 Yahaya (1988) ya kawo Misalai na waqoqin da aka yi masu jigon siyasar zamani (watau ta jam'iyya) Misali:

i. *Waqar- Arewa Jamuriya ko mulukiya-ta M. Sa'adu Zungur.*

ii. *Waqar maraba da 'yanci-ta A.Na'ibi Suleiman Wali.*

iii. *Waqar haxa kan Afirka- ta A. Abubakar Ladan.*

iv. *Waqoqin jam'iyyun siyasa- waqoqin NEPU, NPC, PRP. ds.*

Haqiqa wannan aiki babban kundi ne kuma rumbun adabin Hausa. Don haka kammala wannan bincike ba tare da an waiwaye shi ba, to, sai a ce "an yi tuya an manta da albasa". Domin aikin zai ba mu cikakken haske na gudanar da wannan bincike. Don haka ne yake da muhimmanci a nan.

Shi kuwa Kafin Hausa (1983) a aikinsa ya tattaro wasu waqoqi ne na Alhaji Aqilu Aliyu ya yi sharhin su. Dukan waqoqin na siyasa ne, kuma masu goyon bayan jam'iyyar NEPU. Ya ba da uzurinsa da cewar ba don goyon bayan wata jam'iya ne ya sa ya xauki

waxannan waqoqi ba. A'a, ya yi haka ne saboda sha'awarsa ga waqoqin Alhaji Aqilu Aliyu kasancewarsa fitacce wajen rubuta waqoqin Hausa. Ya bayyana cewar lokacin siyasa, waxannan waqoqi sun taimaka wajen jan hankalin jama'a da kawo wa jam'iyyu magoya baya.

Kafin Hausa ya kasa littafinsa gida biyu. A kashi na farko ya kawo waqoqin da ya yi sharhi kan su. Sannan a kashi na biyu ya yi sharhin waqoqin. A cikin sharhin waqoqin ya duba abubuwa muhimmai guda uku da ya ce a kan duba wajen sharhin waqa. Abubuwan su ne: Qunshi (jigo) da salo da tsari. Waqoqin da ya yi sharhi a kan su, su ne:

i. *A hura wuta a ga na mai rabo*
ii. *Jiya da yau.*
iii. *Inuwar sawaba.*
iv. *Maraba maraba*
v. *'Yar Fulani*
vi. *Inkwariya*
vii. *Fillori 'yar indiya.*
viii. *Baqi uku sharrin NPC.*
ix. *Tauraron zamani*
x. *Jihar Kano munka fi so a ba mu ba Kaduna ba*

Idan aka duba, za a ga cewar wannan aiki yana da alaqa ta kai tsaye da wannan bincike da ake so a gudanar. Sai dai yayin da a cikin aikin an duba waqoqin siyasa na jamhuriya ta farko (lokacin NEPU /NPC), a nan ana so ne a duba waqoqin siyasa a jamhuriya ta huxu.

Abdulqadir (1974) A littafinsa da ya rubuta a kan tarihin rayuwar Sa'adu Zungur, ya bayyana tarihin rayuwar Sa'adu Zungur da yadda aka samu kafuwar jam'iyyun siyasa a Nijeriya.

Haka kuma, ya kawo wasu daga cikin waqoqin Sa'adu Zungur tare da yin sharhinsu. Waqoqin da ya kawo su ne: "**Waqar Bidi'a**" da "**Waqar Maraba da Soja**" da "**Waqar 'yan Baka**" da kuma "**Waqar Arewa Jamhuriya ko Mulukiya**" wadda tana a sahun farko a waqoqin siyasa na Hausa.

Hiaket (1977) shi ma ya nazarci wasu waqoqin siyasa ya yi sharhi tare da bayani dalla-dalla. Waqoqin da ya nazarta su ne:

i. "*Arewa Jamhuriya Kawai,* " ta Mudi Sipikin
ii. *"A Yau Ba Maqi NEPU Sai Wawa,"* ta Malam Gambo Hawaja
iii. *"Allah Shi Sa Musulunci Ya Danne Kafirci,"* ta Malam Shekara Sa'ad
iv. *"Ya Allah Ka Ba Mu Sawaba ,"* ta Malam Yusuf Kantu
v. "*Waqar Yabon Sir Ahmadu Bello* ," ta Malam Shekara Sa'ad
vi. "*Waqar Murnar Dawowar Malam Aminu Kano Daga Landan* ," ta Malam Lawal Mai Turare Yelwa

Sani (2011) ya duba yadda aka sami qirqirar wasu kalmomi tare da ba su ma'ana a harshen Hausa sanadiyyar tsunduma cikin harkokin siyasa a qasar Hausa. Ya duba dangantakar siyasa da harshe, inda ya bayyana cewar ire-iren waxannan kalmomi ana aiwatar da su duk a cikin zube ko waqa. Sani ya bayyana jawaban da ake yi wajen yaqin

neman zave a matsayin zube (Sani, 2011: 93). Sannan kuma ya duba wasu waqoqin siyasa da aka yi tsakanin shekarar 1978 zuwa 1983, waxanda ya bayyana da cewar suna bayyana manufofin jam'iyyun magoya baya ta hanyar yabo da zuga. Sannan kuma, su kushe da aibanta abokan hamayya ta hanyar zambo. Daga cikin misalan da ya ba da daga waqoqi sun haxa da:

i. "*Waqar Maso Ceto*" ta jam'iyyar PRP, wadda a cikinta aka bayyana manufofin jam'iyyar .
ii. "*Waqar Ku Mu Taru Mu Zavi PRP*," wadda ita ma, ta bayyana manufofin jam'iyyar PRP.
iii. "Waqar Tambaya Da Amsa 16 ," wadda ta bayyana tsadar kayayyaki da hauhawar farashi

Junaidu (1981) ya duba wasu waqoqi guda goma masu jigogi daban- dabam da suka haxa da harshe da al'ada da addini da sauransu. Duka waqoqin da ya duba, ya kawo sharhin kowace tare da bayyana salo da jigo da tsarin waqar. Waqoqin da ya nazarta sun haxa da: "Waqar Harshen Hausa" da " *Waqar Al'adun Gargajiya"* da " *Waqar Xangata*" da " *Waqar Gaskiya Mai Xaci* " da sauransu. Wannan aiki zai taimaka matuqa wajen fahimtar hanyar da za a nazarci waqa, kasancewar wannan nazari ya shafi nazarin waqa.

Alal haqiqa ayyukan Hiskett (1977) da Sani (2011) da Junaidu (1981), duk za su taimaka ga wannan aiki domin duk suna magana ne game da abin da ya shafi waqa da yadda ake nazarinta. Don haka ne mai bincike kasancewar aikinsa a kan waqa ne, zai san inda

aikinsa ya kamata ya dosa da kuma samun cikakken haske na hanyar da zai bi ya nazarci waqoqin da aka xauka domin yin nazari.

Everyman's Encyclopaedia Vol.10 (1967) da *The Columbia-viking Desk Encyclopedia, Vol.2* (1953) sun yi magana kan farfaganda inda dukansu suka bayyana cewa asalin kalmar daga kalmar Latin ce (de parpaganda fide mai nufin yaxa aqidar addini).

Shi kuwa the *Columbia-Viking Desk encyclopedia* ya bayyana farfaganda da cewa hanya ce da ake qirqira wata xabi'a don cusa ta ga wani, ko jan ra'ayinsa. Ya bayyana cewa yana iya kasancewa ta kafar yaxa labarai ko kuma ta aikin fasaha (kamar waqa). Hanyar farfaganda a coci da qungiyoyin mishan na yaxa addini. Sun kuma bayyana cewa qasashe masu aqidar kwaminasanci farfaganda ce babbar hanyarsu ta yaxa manufofinsu.

Shi kuwa *Everyman's encyclopaedia* ya bayyana cewa farfaganda tana ma iya kasancewar babban makami na yaxa mummunar aqida, idan aka voye gaskiyar manufar yin ta. Sun nuna cewa aba ce da aka daxe ana yi, amma zuwan rediyo ya qara havaka ta. Wani mutum Gustar Le Bon (1895) ya nazarci farfaganda inda ya bayyana ta da cewar reshe ce na bayyana nazarin tunanin xan Adam ta fuskar sadarwa (mass- psychology). Tun 1918 ne salon farfaganda ya canza lokacin da qasashen kwamisanci ke amfani da ita wajen yaxa munanan aqidu. Hanyoyin da ake yaxa farfaganda sun haxa da: rediyo da talabijin da majigi da bukukuwa da maganganun hikima da qungiyoyin addini. Babbar manufar farfaganda dai ita ce yaxa wata manufa da mutum ko ma qasa ke so ya yi.

A Jamus lokacin yaqin duniya na biyu bisa umurnin Goebbels an yi amfani da qarerayi domin a qirqiri wani ra'ayi game da wata manufa da ake so a yaxa. misali an ba da qarfi ga fitattun mutanen da aka kashe don ruruta wutar yaqin. misalin Edith Cavell da Rose Luxemburg.

Haqiqa wannan batu na farfaganda shi ma zai taimaka ga wannan bincike. Domin daga gare shi za a fahimci cewa farfaganda da talla abubuwa ne guda biyu daban-daban, an kuma fahimci hanyoyin da ake yin su.

2.3 Takardu da Mujallu

Muhammad (1978), ya bayani game da abin da ya shafi amsa- amo a cikin waqa, wanda ya kira amsa-amon kari. Ya bayyana cewar fitaccen salon tsarin waqa rubutacciya shi ne yadda kowane layi ko baitin waqa yake qarewa. Wato ya kasance a cikin gavovin qarshe na layuka ko na baitoci sun haxu da juna wajen samun harafi iri xaya. Ya kasa amsa- amo zuwa na ciki da na waje. Ya kawo misali daga waqar *"Kadaura Babbar Inuwa,"* ta Aqilu Aliyu, inda ya ce:

> *i. "Hauka da jahilci suna da zumunta,*
> *Makusanciya ta ququt marar jayawa,*
> *ii.Har ma kusan in ce su wa da qane ne,*
> *saqo da saqo ne wajen haifawa.*
> *iii. Kai hasalin magana tagwaye ne su,*
> *'ya'yan ciki xaya ne a daina rabawa. ''*
> (Muhammad, 1978 : 48)

A waxannan baitoci ya bayyana cewar sun da amsa- amon harafin *wa* . haka kuma ya bayyana cewar akwai amsa- amon harafi iri biyu; na ciki da na waje. Ya ba da misali da waqar Imfiraji ta Aliyu Nsmangi, inda ya ce :

i. 'Shi ya ce mana ai juhala,
Shi da kafirci g ailla,
'yan'uwa ne la muhala,
'yan kwanika ma la'alla,
Girman ba zai wata bakwai ba.

ii.Shi fa jahilci ya sarbu,
Ne na kafirci ga aibu,
Wanga zance ya zamo bu-
Xin batun Malam Habibu.
Da yakan mana ba abin musu ba.''
(Muhammad, 178: 48)

A waxannan baitoci ya bayyana amsa- amon ciki a baiti na farko da *la*, a na biyu kuma *bu*. Sannan amsa- amon wajen kowane baiti ya qare da *ba*. Haka kuma, ya bayyana cewar ana samun amsa- amon harafi ne a rubutattar waqa kawai. A yayin da amsa-amon kari ake samun sa a duka biyun; rubutatta da tab aka. Amsa- amon kari shi ne yadda ake samun hawa ko sauka na murya a gavovin qarshe a cikin layukan waqa.

Ga misalin amsa- amon kari kamar yadda ya bayar da shi daga wasu baitoci na waqar "*Qaiqayi ,''* ta Aqilu Aliyu, inda ya ce:

i. "Ba zai kasha ba kishin jinni labudda,
Ga gaskiya, qarya ta tashi ta sheqa.
ii. Qarya tsawonta da kaurara, faxinta,
Ko ta fi rimi dole sai ta duqa."
(Muhammad, 1978 : 50).

Ya bayyana layukan farko na baitocin, gavarsu ta qarshe kalmomin *labudda* da *faxinta* karinsu mai sauka ne ; wato suna da amsa- amon kari iri xaya. Wato sautin yana hawa ya sauka (HS).

Babu shakka, wannan aiki ba sai an faxa ba. Yana da matuqar muhimmanci ga wannan bincike. Domin kuwa babu yadda za a yi nazarin waqa ba tare da an yi maganar amsa-amo ba. Saboda da haka, haqiqa wannan aiki ya taimaka matuqa a lokaci gudanar da wannan bincike.

Umma (2011) Ta duba adon harshe a wasu rubutattun waqoqin siyasa na jamhuriya ta uku. A cikin aikin nata bayan ta yi sharar fage da yadda siyasa ta kafu, sai ta kawo nau'o'in adon harshe inda ta bayyana cewa sun qunshi waxannan abubuwa kamar haka: Siffantawa da Kamantawa da Jinsintarwa da kuma Alamtarwa. Duk ta bayyana ma'anoninsu da yadda suke fitowa a cikin waqa ta hanyar ba da misalai. Misali, a Waqar Dauda Kahutu Rarara ta "Saura Qiris Deputy qara haquri Baba", ta ba da misalin Siffantarwa inda ya ce:

'Farin wata idan ka fito duhu ya yaye.'

A kamantawa kuma ta ba da misali a dai cikin waccan waqar inda ya ce:

*'Ka zamo **kamar** namijin goro gun iyaye,*
Dole ne a neme ka idan gari ya waye.'

Birniwa (2005) ya duba karin magana a cikin waqoqin siyasa. Ya bayyana yadda mawaqan siyasa ke amfani da karin magana a cikin waqoqinsu, domin bayyana waxansu

manufofi. A cikin wannan aiki nasa ya nuna yadda mawaqa kan yi amfani da karin magana a cikin waqoqinsu ba yadda aka saba yin su ba a maganganun yau da kullum watau sukan canza lafuzzan, amma dai ma'anonisu na asali ba su canza ba. Misali, a waqar Aqilu Aliyu mai suna: "*Tauraron Zamani,*" ya yi amfani da karin magana inda ya ce:

> *"Ba ma buqata ga romon java mai wari,*
> *Ku bari zagage na mota doke sui sauri,*
> *Nijeriya ce ta quna take shirin qauri,*
> *Mai hankali ka fahimci abin da mai tsari,*
> *Allah ka taimaki NEPU gyara zamani."*
> (Birniwa, 2005:58 – 59).

Karin maganar da aka yi amfani da ita a nan, ita ce:

"Romon java ga kitse, ga wari."

Mawaqin a nan yana yi wa 'yan jam'iyyar NPC gugar zana ne cewa su, ko abin da suke das hi, romon java ne, wanda yake da kitse, ga kuma wari. Warin dai ba zai wuce ganin da yake (mawaqin) yi musu ba na cewa su masu cin zalin ne ko haram ne (Birniwa, 2005: 59). Saboda haka wannan karin maganar tana nuna cewa a qyamaci 'yan NPC saboda miyagun halayensu. Domin kuwa duk abin da yake da wari, to ana qyamarsa kuma ba ma a so a kusance shi, balle ma har a so shi.

Haka kuma Birniwa (2010) ya duba yadda 'yan siyasa sukan yi amfani da waqoqin siyasa wajen yaqin neman zave a jamhuriya ta xaya da ta biyu. Ya kawo misalai masu tarin

yawa daga waqoqin jam'iyyun NEPU da NPC a jamhuriya ta xaya da kuma PRP da NPN a jamhuriya ta biyu. Ya yi cikakken bayanin yadda aka yi amfani da waqoqin wajen kushe abokan hamayya da kuma xaukaka martabar wasu jam'iyyun daga magoya bayansu. Misali ya kawo waqar Shekara Sa'ad:

"*Waqar yabon Sardauna*" inda ya ce:

''Maqiyammu ko sun yarda ko da sun qiya,

NPC sai ta mallake Nijeriya.''

Haka kuma wani misalin shi ne a waqar Aqilu Aliyu mai suna "Fillori 'yar Indiya, ya ce:

'*Sun yi shiri sun yi mitin sun haxa kwamba,*
wai su kashe NEPU a binne su ci gumba,
sun yi kaxan ba su da iko su kashe ta,
NEPU dashe ne fa da Allah ya kafa ta.''

Bayero da Dunfawa (2010), sun yi nazarin "Waqar motar siyasa: Saqon Talakawa zuwa ga 'yan siyasar zamani". Ta Bello Danshabiyu. Bayan waiwayen wasu ayyuka da suka shafi waqoqin siyasa, sun yi sharhin waqar dalla-dalla tare da fito da jigonta. Wannan nazarin ya fito da halayen 'yan siyasar zamani na xauka – da – ajewa da yadda suke neman taimakon talakawa lokacin yaqin neman zave. Haka kuma da yadda siyasar take haddasa gaba a tsakanin talakawa. Da zaran an gama zave, 'yan siyasar sun haye kujerar mulki, ba a qara ganin su, kamar dai 'an yi ruwa an xauke".

Hausawa na cewa, "idan ka ji gangami da labari." Saboda irin wannan hali na 'yan siyasa ne ya sa aka shirya waqar motar siyasa domin isar da saqon talakawa gare su. Domin a

nuna cewa talakawa fa “an sha su, sun warke.” Don haka, ba za su qara taimakon duk wanda aka zave shi, ya yi watsi da al’amuran talaka ba. Ga misali daga waqar:

‘Ba ni tura ta,
Kuma ba mu ce ku tura ba,
In dai motar siyasa ce,
To dab bana ba ni tura ta.

An sare wane don hauka,
An mare wane don hauka,
Wani ya yi faxa da danginai,
Hay yau kuma ba su gaisawa,
Ta hau bai sake taggo ba.

Dum mai gyarawa shi gyara,
Kamag gobe za a koma yin zave,
Mai alheri a zave shi,
Kog ga mai sherri wa ka xaukatai.’’
(Bayero da Dunfawa, 2010: 216-222)

Haqiqa, shi ma wannan aiki zai taimaka qwarai ga mai gudanar da wannan bincike. Domin kuwa aiki ne da ya kalli wani abu da ya shafi waqoqin siyasa.

Abdulmunini (2009) ya yi aiki ne kan Hausar talla a rediyo, inda ya yi tsokaci a kan tallar hana cin mutuncin takardar kuxin naira. Ya bayyana cewar talla daxaxxiyar sana’a ce da xan Adam ya daxe yana yi. Ana gudanar da ita ne ta hanyar xaukan kayan sayarwa ko hajar sayarwa zuwa duk inda matattarar jama’a take ana gabatar da kayan ta amfani da shiryayyen zance cikin hikima don jawo hankalin mutane zuwa ga abin sayarwa da ake tallatawa.

Talla tana qunshe da lafazin harshe mai taushi kuma mai qunshe da azanci tare da zantukan hikima irin su karin magana da kirari da habaici da zambo har ma da waqa da makamantansu don nuna alfanun abin sayarwa ga jama'a; sannan don a kwarzanta hajar sayarwa.

Haka kuma ya bayyana cewar ba sai lalle haja ake tallatawa ba. Ana tallata ra'ayi da manufa da wasu qudurori na hukuma ko na mutum ko na qungiya ko na siyasa ko na jam'iyyar siyasa don mutane su karve su kuma su yarda da su. Ya kawo misalai da yawa na waqoqin da ke talla game da mutunci da darajar kuxi. misali

i. *"Waqar "Naira da Kwabo sabon kuxi," ta Haruna Uji*

ii. *"Waqar kuxi a kashe su ta hanya mai kyau," ta Alhaji Mamman Shata.*

iii. *"Waqar Tsakanin Xan'adam da kuxi ta Alhaji Abdu Wazirin Xanduna". Da sauransu.*

A ra'ayin mai bincike daga bayanan da suka gabata, talla, ita ce:

> *"Nuna wani abu ko wani ga jama'a ta salo da hikimomin magana da hanyoyi daban-daban domin su saya ko su zave shi".*

Ke nan, za a iya fahimtar cewa a talla haja ce, wadda kuma tallata ta ake yi. A yayin da farfaganda manufa ce, wadda yaxa ta ake yi.

Wannan aiki yana da nasaba da binciken da ake so a gudanar. Domin kamar yadda aka gani an bayyana rukunonin talla da suka qunshi azancin magana kamar su yabo da kirari

da zambo, waxanda kuma duk suke cike maqil a cikin waqoqin Siyasa. Har ma an nuna cewa ba haja kaxai ake tallatawa ba, a'a har ma da mutane da jam'iyyun siyasa. Don haka, aikin zai taimaka qwarai a binciken da ake so a gudanar.

Hiskett, (1975) ya bayyana zamanin siyasar farko da cewa ta samu daga 1946 zuwa 1966. A wannan tsakanin ne Hiskett ya bayyana cewar aka samu vullowar jam'iyyun siyasa a qasar Hausa, waxanda kuma suka samu sakamakon kafa qungiyoyi daban-dabam a arewacin Nijeriya. Hiskett, (1975:4) ya yi bayanin yadda Sa'adu Zungur ya yi amfani da waqoqinsa wajen wayar wa jama'a kai ta hanyar farfagandar bayyana ra'ayinsa game da harkokin mulki da siyasa, musamman a arewa. Waqoqin da ya duba su ne: *"Waqar Maraba da Soja". da*

"Waqar Arewa, Jamhuriya ko Mulukiya," da kuma"*Waqar Maraba da 'Yanci,"* dukansu na Sa'adu Zungur.

Malumfashi (2009) da Kuna da Malumfashi (1998) sun duba yadda mulki ke sauya fuska a zunguna daban-daban, musamman a tsarin mulki na hada-hadar siyasa. A nan ne aka duba rawar da en'e-en'e da 'yan doka da alqalai suka taka wajen haifar da ayyukan adabi. Musamman an dubi irin danniya da babakere da ake samu a tsakanin wani rukunin mutane. Wannan danniya ita ta haifar da tashin-tashina da sa-in-sa a tsakanin jam'iyyun siyasa wajen mayar da martani, musamman tsakanin **NPC** da **NEPU**, wadda ta haifar da samuwar ayyukan adabi (waqoqi).

2.4 Ma'anar Siyasa

Kasancewar wannan bincike ya shafi al'amarin siyasa xungurungum da ya shafi waqoqi, ya dace a xan san wani abu game da ma'anar ita kanta kalmar "siyasa". Kalmar siyasa ta samo asali ne daga kalmar "al-siya-sat" ta harshen Larabci, wadda take nufin "sarrafa abu", a ma'anarta ta lugga. (Xiso, 1997:17).

Dangane da ma'anar wannan kalma ta siyasa, masana da dama sun ba da ma'anarta daban-daban gwargwadon fahimtarsu. Misali, Nuruddin (2005:736) ya bayyana ma'anar siyasa ta fuskoki biyu kamar haka:

i. "Siyasa na nufin jivintar mutane da shugabantar al'amarinsu da shiryar da su zuwa tsayayyar hanya".

ii. "Siyasa na nufin fannin hukunci da gudanar da ayyukan daula da abubuwan da aka kafa ta ciki da waje".

Shi kuwa Xiso (1997:3) ya bayyana ma'anar siyasa da cewa:

"Siyasa wani tsari ne da ake bi wajen qoqarin sarrafa al'ummar qasa da warware musu matsalolinsu na rayuwa da kuma qoqarin cusa musu waxansu ra'ayoyi".

A Qamusun Oxford kuwa, an bayyana ma'anar siyasa da cewa:

"Siyasa na nufin sha'anonin gwamnati; al'amuran siyasa ko na rayuwa".

Dangane da yadda Hausawa ke kallon siyasa kuwa, ana ganin ta da sifofi iri-iri dangane da yadda aka fahimce ta. Misali, a idon Bahaushe, idan an ce siyasa, to yana xaukar ta a matsayin dabara, yaudara, qarya, sauqi, sulhu ko iya hulxa da jama'a.

Har ila yau kuma, wasu sun xauki siyasa da cewar cin amana ce da butulci da wayo ko zance mai daxi ko lallashi ko danne haqqi da sauransu. (Mashi, 1986:16) da

(Xiso, 1997:3) da (Funtua, 2003:20).

Saboda haka, a ra'ayin mai bincike, yana ganin cewar siyasa a idon Hausawa, tana nufin rashin cika alqawali. Wannan ya yi daidai da yadda idan wani ya yi alqawali aka ga kamar ba zai iya cikawa ba, sai a ce "Kada ka yi mini maganar 'yan siyasa", watau faxa ba cikawa. Dalilin haka kuwa, bai wuce halayyar 'yan siyasa ba ta rashin cika alqawulan da suke yi wa jama'a a lokacin yaqin neman zave, bayan sun xare karagar mulki.

Haka kuma, wasu na kallon siyasa a matsayin wani irin nau'i na wasa, kamar yadda Hausawa kan ce "siyasa mugun wasa, in ba ka shiga ba, kar ka shiga, idan ka shiga kar ka fita". Wannan magana tana da nasaba idan aka lura da yadda 'yan siyasa ke amfani da 'yan banga ana ruxu da halin a-mutu-ko-a-yi-rai lokacin yaqin neman zave. Da kuma fito-na-fito da ake yi, wani lokaci har da makamai a tsakanin jam'iyyu a qoqarin kare xan takara da nufin tilas sai ya kai ga gaci a muqamin da yake nema. Sakamakon haka, akan sami miyagun raunuka, wani lokaci ma, har da rasa rayuka.

Haka kuma, za a iya cewa wasu na ganin siyasa a matsayin wani salon shugabanci da al'umma ke zaven shugabanni da kansu a qarqashin tsarin jam'iyyun siyasa. Wannan nau'i na shugabanci, shi ne mulkin farar-hula, wanda babu hannun Soja a ciki.

Don haka, ma'anar siyasa a dunqule a wannan bincike, a iya cewa dabara ce ta jagorancin al'umma cikin 'yanci da walwala don cim ma wasu qudurori na cigaban rayuwa.

2.4.1 Ire-Iren Siyasa

Siyasa kasancewar ta qunshi harkar tafiyar da jama'a, a iya cewa ta shafi rayuwa gaba xaya. Don haka, za a same ta da nau'o'i daban-daban dangane da aqidar al'umma. Ke nan, a cikin al'umma, za a sami mutane da irin burinsu da aqidarsu da kuma yadda suke kallon rayuwa gaba xaya.

Kasancewar siyasa tsari ne na shugabanci, Birnawa (1987) ya kalli tsarin shugabanci a qasar Hausa ta fuska uku; kafin shigowar addinin Musulunci da lokacin shigowarsa da kuma lokacin jihadi.

Shi kuwa Mashi (1986), ya kalli siyasa ne ta fuska biyu, rak, inda ya raba ta zuwa siyasar gaba xaya da kuma siyasar jam'iyya. Xiso (1997) kuma, sai ya kalli ire-iren siyasa ta fuska uku, watau siyasar aqida da siyasar jam'iyya da kuma siyasa ta gabaxaya.

Kamar yadda Birniwa, (1987) ya bayyana a shimfixarsa, akwai yadda shugabanci ya fara da yadda yake sake salo dangane da cigaban yanayin rayuwa har zuwa lokacin da aka samu siyasar jam'iyya a Nijeriya. Misali, a shimfixarsa, ya bayyana tsarin shugabanci kamar haka:

i. **Siyasa Ta Gargajiya:** wannan shi ne tsari da ya gudana tun kafin shigowar addinin Musulunci qasar Hausa. A irin wannan tsari ne ake samun tsarin barantaka da sarki da jakadanci da sauransu. Misali shi ne kamar sarautar Kano yadda ta samo asali, shi ne daga mai kula da gidan tsafin tsumburbura. Wannan dodo yana kan dutsen Dala, a Kano. Mai

tafiyar da al'amuran wurin da tsumburburar take shi ne Barbushe. Shi ne shugaban mutanen da suke bauta wa wannan gunki. (Birniwa, 1987:10) da (Daure, 2000:01) da (Dokaji ,1978:7).

ii. **Siyasa (Shugabanci) Bayan Shigowar Addinin Musulunci:** Wannan shi ne lokacin da Musulunci ya shigo daga Afirka ta Arewa. Wannan sauyi da aka samu a qasar Hausa ya yi tasiri ainun ga sarauta. Misali, a wajen qarni na 15 qarqashin Sarki Rumfa, a Kano, wasu manyan Malamai sun yi tasiri a kansa. Daga cikin malaman akwai Muhammad B. Abdul-al-karim al-Maghili. Tasirin wannan sarauta mafi yawa ta gado ce. wannan ya cigaba har zuwa farkon qarni na 19 lokacin da Shehu Usman Xanfodiyo ya qaddamar da jihadi. (Birniwa, 1987:10).

iii. **Tasirin Shugabanci Na Musulunci:** Wannan ya samo asali ne tun lokacin da Annabin tsira, Muhammad (SAW) ya yi wafati a hijira ta 632, wanda kafin wafatinsa, bai naxa wanda zai shugabanci Musulmai ba. Shugaban farko da aka zava, shi ne Sayyidina Abubakar, dalilin cewar shi ne babba a cikin sahabbai. Kuma mafi yawa shi ne Annabi yakan wakilta ya jagoranci sallolin farilla.

Bayan Sayyidina Abubakar, an ci gaba da zavar shugabanni a Musulunci, a inda aka zavi sauran halifofi uku da suka biyo bayansa a bisa tsarin matsayin kowane;

Umar ibn Khattab sai Uthman ibn Affan, sannan Ali bn Abi Talib (Birniwa, 1987:11).

Dangane da abin da ya gabata a sama, a ra'ayin wannan bincike, siyasa ko shugabanci a rayuwar xan Adam, a iya cewa "Tun ran gini, tun ran zane, " watau tun lokacin da Allah ya halicci xan Adam, akwai son shugabanci a cikin jininsa. Haka kuma Allah (SWT) da kansa ya shimfixa tsarin shugabanci a bisa doron qasa. Kamar dai yadda aka ga al'amarin Annabi Adamu (AS) da Allah ya sa a matsayin Khalifa. Allah ya ce a cikin suratul Baqara aya ta 30 (2: 30):

"Kuma a lokacin da Ubangijinka ya ce ga mala'iku. Lalle ne, Ni mai sanya wani halifa ne a cikin qasa".

Saboda haka, a nan, dangane da bayanan da suka gabata, mai bincike ya kasa siyasa zuwa nau'i huxu kamar haka:

i. **Siyasar Xabi'a:** Kamar yadda Nuruddin (2005:820) ya bayyana a qamusunsa, ya bayyana xabi'a da cewar hanya ce wadda aka halitta mutum a kan ta. Don haka, siyasar Xabi'a, ita ce wadda aka halicci xan Adam da ita a cikin jininsa. Misali, shi ne abin da ya faru tsakanin Annabi Adamu (AS) da Shaixan da tsakanin Annabi Musa (AS) da Fir'auna da tsakanin Annabi Yusuf (AS) da 'yan'uwansa da tsakanin Habila da xan'uwansa Qabila. Duk abubuwan da suka faru, idan aka

lura, suna da nasaba ne da son shugabanci. Saboda haka, ana iya bayyana wannan xabi'a ko halayya da **Siyasar Xabi'a**.

Wannan nau'in siyasa za a iya ba da misalinsa da abin da ya faru tsakanin Annabi Yusuf (AS) da 'yan'uwansa. A cikin Alqur'ani mai girma, suratul Yusuf, aya ta 8 (12 :8), Allah (SWT) yana cewa:

"*A lokacin da suka ce, lalle ne Yusufu da xan'uwansa ne mafiya soyuwa ga ubanmu daga gare mu, alhali kuwa mu jama'a guda ne. lalle ne ubanmu, haqiqa, yana cikin vata bayyananniya".*

Wannan ya nuna cewa xabi'ar xan Adam ce ta son shugabanci, domin duk kasancewar Annabi Yusuf (AS) da 'yan'uwansa sun fito daga tsatso guda, amma suna hassada da irin yadda suka ga mahaifinsu yake nuna ya fi son Annabi Yusuf (AS), a xabi'ance.

Haka ma, Aqilu Aliyu, a waqarsa "*Tauraron Zamani*", a baiti na 23, yana cewa:

"Mai hassada ni fa ban ce ka yi laifi ba,
Ga ubanmu Adamu Shaixan ya yi tun a gaba,
Qabila ma shi ya kar Habila don jaraba,
Kuma babu wai ga shi an yi wa Alu Ya'aquba,
Kai mai musu da faxata duba Qur'ani."
(Birniwa, 1987:129).

ii. **Siyasar Gargajiya:** Wannan ita ce tsarin siyasa wadda take a kan tsarin sarautar gargajiya. Ita ce wadda take samun sarki da mabiyansa.

iii. **Siyasar Addini** (Musulunci): Ita ce wadda take a kan tsarin shugabanci na Musulunci. Misali shi ne irin tsarin da aka samu a qasar Hausa

lokacin da Shehu Usman ya qaddamar da jihadi. Sannan ya ba da tutoci ga wasu, domin su jagoranci al'umma a garuruwa daban-daban.

iv. **Siyasar Aqida (Jam'iyyu)**: Ita ce wadda ta ginu a bisa tsarin aqidar da wasu mutane suka haxu a kan ta. Watau tsari na jam'iyyu da aka kafa don neman shugabanci a qarqashinsu.

2.4.2 Taqaitaccen Tarihin Samuwar Siyasa a Nijeriya

Samuwar Siyasa irin ta jam'iyya a Nijeriya, ta samu ne a sakamakon zuwan Turawan mulkin mallaka. Kuma ta samu ne tun daga kafa qungiyoyi daban-daban a sassan qasar nan, musamman wajen fafutukar neman 'yanci.

Tsarin siyasar jam'iyya a Nijeriya, kamar yadda za a gani, ya shafi vangaranci; tsakanin Kudu da Arewa, ta fuskar mulki da tattalin arziqi.

Dukan zangunan da aka ratso na jamhuriyoyin can guda huxu, akwai bambancin kudu da arewa a tsarin siyasun. Arewa suna jin tsoron kada 'yan kudu su danne su. Tun lokacin da ake yunqurin neman 'yanci, 'yan Arewa suna da ilimin addinin Musulunci. Su kuwa Kudu, suna ganin sun yi wa 'yan Arewa fintikau a fagen ilimin zamani. A wajajen shekara ta 1940 zuwa 1950, Sardauna shi ne jigo a siyasar Arewa. Babban burinsa, shi ne ya ga an sami haxin kan 'yan Arewa, da kuma ganin sun sami ilimin zamani ta yadda za a tafi tare da su a cikin harkokin mulkin qasa.

A yammacin qasar kuwa, vangaren da mafi yawa Yarabawa ne, Cif Obafemi Owolowo ne ke jagorantar siyasar yankin. A Gabas kuwa inda Inyamurai suke, Cif Nnamdi Azikwe ne yake murza sitiyarin siyasarsu. (Furniss, 1996:3-4).

Don haka ne ake ganin har sai ‘yan Arewa sun farka daga barci, sun bar lalaci da son jiki, sun yi ilimin boko. Idan ba haka ba kuwa, to ‘yan Kudu za su taushe su a harkokin mulkin qasa (Abdulqadir, 1974:14).

Ke nan, akwai manyan qabilu uku a qasar, waxanda suka mamaye harkokin mulki ko siyasar qasar nan. Waxannan qabilu, su ne suke taka muhimmiyar rawa, kuma suke juya al’amuran siyasar Nijeriya. Hausa/Fulani (29%) a Arewa, da Yarabawa (21%) a Kudu maso yamma da kuma Inyamurai (18% a yawan jama’a) a Kudu maso gabas. Ana kuma ganin cewa rinjayen ‘yan Arewa, Hausawa Musulmi ne wanda sun kai kashi 50 cikin xari na jama’ar qasa, sun fi dukkan mutanen Kudu, waxanda mafi rinjayensu, ba Musulmi ba ne, da suke da kashi 40 cikin xari. Waxannan rukunai na qabilu guda uku, (Hausa da Igbo da Yarabawa), su suka xauki kashi 68 cikin xari na jama’ar qasar. Kamar dai yadda Hukumomin Gwamnatin Amurka da na Nijeriya suka qiyasta (Paden, 2008:7).

Wannan ya nuna akwai bambanci tsakanin Arewaci, da take da rinjayen Musulmi, da Kudu da suke galibi ba Musulmi ba. Duk da cewa Musulmi ‘yan Arewa suna da ilimi na addinin Musulunci sama da shekara 500, amma sun rasa dama a al’amarin neman mulki da ‘yanci a Nijeriya. Damar da suka rasa, ita ce ta rashin ilimin boko, savanin takwarorinsu na kudu da suke da shi da daxewa. Don haka ne ‘yan Arewa suke ganin

‘yan Kudu za su danne su a fagen mulki ko siyasar Nijeriya idan aka sami ‘yancin kai da wuri (Birniwa, 1987:17).

Kamar yadda aka ambata tun a baya, siyasa a Nijeriya, ta fara samo asali ne ta qungiyoyi daban-daban. Waxannan qungiyoyi kuma an kakkafa su ne don neman ‘yancin kai da wayar da kan jama’a ga fafutukar neman mulki. A cikin irin wannan fafutuka, akwai wasu fitattun mutane da dama daga vangarorin qasar nan da suka taka muhimmiyar rawa don ganin an sami ‘yanci daga Turawan Mulkin Mallaka.

Waxannan mutane sun yi ta faxi-tashi, su-kai-gwaro-su-kai-mari, a ciki da wajen qasar nan. Suna shirya tarurruka da tuntuvar Turawan Ingila, har dai aka sami ‘yanci a shekara ta 1960. A vangaren arewa an sami gwarzaye irin su Sir Ahmadu Bello da Sir Abubakar Tafawa Valewa da Alhaji Mudi Sipikin da Mallam Sa’adu Zungur da Mallam Aminu Kano da sauransu. A Kudu kuma akwai zarata irin su Sir Herbert Macauley da Nnamdi Azikiwe da Cif Obafemi Owolowo da Anthony Enahoro da sauransu.

Samuwar siyasar jam’iyyu a qasar nan ya soma da qungiyoyi a vangarori daban-daban na qasar nan. Misali, a yankin arewa na qasar nan, an samu wasu qungiyoyi masu nasaba da siyasa a garuruwa daban-daban. A Bauchi akwai Qungiyar Tattaunawa ta Bauchi, a Zariya akwai Qungiyar Zumunta, a Sakkwato akwai Qungiyar Matasa, Kano akwai Qungiyar Lardin Kano da kuma Qungiyar Jam’iyyar Mutanen Arewa da dai sauransu.

A Kudu kuma, a 1923 Herbert Macauley ya kafa jam’iyyar siyasa ta farko mai suna Jam’iyyar Mulkin Dimokuraxiyar Nijeriya (NNDP). Ya lashe duk zaven da aka yi a

Legas a 1923-1934. A 1936, wasu mutane da suka haxa da Samuel Akinsanya da H.O. Davies da Ernest Ikoli da Dr. J.C. Vauglin suka kafa Qungiyar Matasan Nijeriya (NYM). Sun kafa wannan qungiya ne domin yin fito-na-fito da mulkin mallaka, watau neman ‘yanci. Sai kuma Nnamdi Azikiwe a 1937, shi ma ya shiga qungiyar. Dukan waxannan qungiyoyi dai, manufarsu ita ce wayar da kan al’umma kan al’amuran rayuwa da tattaunawa kan abubuwan da suka shafi yankunansu da kuma neman ‘yanci.

2.4.3 Kafuwar Jamhuriya a Nijeriya

Kalmar jamhuriya (watau republic da Turanci) baquwa ce wadda ta samo asali daga Latin ‘*res publica’* , wadda take nufin al’amuran jama’a, wadda kuma mafi yawan lokuta ake amfani da ita a bayyana tsarin shugabancin qasa da ya shafi al’umma. Jamhuriya a qasar Rome, kamar yadda ta samo asali, da can ta shafi tsarin sarauta, har aka kai ga ana amfani da ita lokacin mulkin dauloli. A zamanance, da tafiya ta yi tafiya, sai ta kasance ana amfani da Jamhuriya a qasashe irin su Amurka da Indiya, a matsayin tsarin shugabancin da masu riqe da ragamar mulki, suke samun matsayin ta hanyar zabe daga jama’a. Kuma suna gudanar da al’amuran mulkin da zartar da abubuwa ta amfani ko dogaro da tsarin mulki (constitution). Watau dai tsarin shugabanci ne na jama’a, kuma daga jama’a. Daxin daxawa, jamhuriya na nufin tsarin shugabanci da jama’a suke zaven shugaba da kansu. Ba naxi ake yi ba, ko gado kamar tsarin sarauta. A taqaice dai, a wannan bincike, a iya bayyana jamhuriya cewa nau’i ne na shugabanci wanda ake sakar wa jama’a mara da ba su cikakken ‘yancin zavar wanda suke so ya jagorance su bisa cancanta. A tsarin

shugabanci irin na Jamhuriya ana amfani da tsarin mulki (constitution). Masana sun bayyana cewar asali, Jamhuriya tsari ne na shugabanci wanda ba sarauta yake amfani da ita ba. Wato savanin shugabancin da ake yi ta hanyar gado. Misali, Daular Rom, kafin kafuwarta a qarni na Xaya, tana amfani da tsarin shugabanci ne ta hanyar gado. Daga baya, a Amurka, kalmar ta xauki ma'anar tsarin shugabancin da ake zavar mutane, kuma yake amfani da tsarin mulki (constitution) wajen gudanar da al'amuran mulki (Leon, 2008: 109). A taqaice, a wannan binciken, an fahimci cewar duk qasar da aka kira ko take cikin tsarin Jamhuriya, to tana qarqashin mulkin zavavven shugaba ne. Wato dai a tsarin Jamhuriya, jama'a ne ke zaven shugabanninsu. Sannan kuma, ana tafiyar da al'amuran mulki ne ta amfani da Tsarin Mulki na qasa (constitution), a maimakon dokar soja (decree).

2.4.3.1 Jamhuriya ta Xaya

Wannan lokacin siyasa ya yi yayinsa da manyan jam'iyyu da suka haxa da **NPC** da **NCNC** da **AG** DA KUMA **NEPU**. An yi ta wannan gwagwarmaya tun daga 1946 har zuwa 1966 lokacin da jamhuriya ta xaya ta rushe.

Manyan jam'iyyu da suka fi tasiri a arewa, su ne **NPC** da kuma abokiyar hamayyarta **NEPU**. A kudu kuma akwai jam'iyyun **NCNC** ta Nnamdi Azikiwe da kuma jam'iyyar **AG** ta Obafemi Owolowo. Jam'iyyar **NPC** ta samo asali ne daga wata qungiya mai suna Qungiyar Mutanen Arewa. An kafa ta a 1946. Daga cikin waxanda suka kafa ta akwai mutane irin su Dr. A.B. Dikko da Ahmadu Bello da Abubakar Imam. Ita kuwa Jam'iyyar

NEPU, ta samo asali ne daga qungiyar da ake kira **NEPA,** watau Qungiyar Cigaban Mutanen Arewa. An kafa jam'iyyar a 1950, qarqashin jagoracin Malam Raji Abdullah. Daga cikin jiga-jiganta akwai Malam Aminu Kano da Malam Sa'adu Zungur. Ita wannan jam'iyyar ta **NEPU**, ita ce babbar jam'iyyar adawar **NPC.**

Kasancewar jam'iyyun **NPC** da **NEPU**, su ne manya a arewa, ya kamata a ga tsarin manufofinsu a taqaice.

Babbar manufar jam'iyyar **NPC**, ita ce kau da jahilci da lalaci da zalunci. Ita kuwa jam'iyyar **NEPU**, qwato wa talakawa haqqinsu daga hannun Turawa 'yan mulkin mallaka da sarakuna da sauran waxanda 'yan jam'iyyar suke ganin suna zaluntar su. (Birniwa, 2010:4 da 9). Sauran manufofin jam'iyyar **NEPU** sun haxa da:

i. Yin aiki domin haxa kan duk mutanen Nijeriya.
ii. Waye wa talakawa kansu domin su fahimci haqqinsu a kan Hukuma da kuma haqqin hukuma a kansu.
iii. Gwagwarmayar mai do mulkin jama'a a hannun jama'a ta hanyar zave a maimakon hanyar gado.
iv. Gwagwarmayar nema wa Nijeriya 'yancin kanta daga hannun Turawan mulkin mallaka (Mashi, 1986).

Kafuwar jam'iyyun siyasa a Nijeriya, sai aka yi zave na farko 1952-1952 tsakanin jam'iyyun uku; **NCNC**, domin haxaxxiyar Nijeriya, **AG,** daga yankin yamma, **NPC** mai

yaqi don arewa da mutanen arewa. Kowace jam'iyya ta lashe zaven a yankin da ta fi rinjaye.

A zaven da aka yi a 1959, babu wata jam'iyya da ta cinye zaven da rinjaye. **NEPU,** mai hamayya da **NPC,** ta haxe da **NCNC,** wadda ta tsai da Zik a matsayin xan takarar Gwamna Janar. Ita kuwa **NPC,** mai rinjaye a arewa, ta xora Sir Abubakar Tafawa Valewa a matsayin Firayim Minista da kuma Ministan Harkokin Waje. Ita kuma jam'iyyar **AG,** ta yankin yamma, ta zama jam'iyyar hamayya (Daure, 2000).

A qidayar jama'a da aka yi a 1963, an samu cewa 'yan Nijeriya su Miliyan 55.6 ne, kuma arewa ita ce shiyyar da ta fi yawan jama'a. Wannan ya jefa 'yan kudu cikin kokwanto. A kuma wannan shekarar ce Nijeriya ta zama jamhuriya. A 1964 an yi zave wanda wasu jam'iyyu suka haxe a cikinsa. **AG, NCNC** da **NEPU** suka haxe a qarqashin suna **UPGA, NPC** da kuma vangaren Akintola da **AG** wanda ya zama da rinjaye. Sai dai wani vangare na yammacin qasar, bai yarda da sakamakon ba da hujjar cewa 'yan arewa sun tabka maguxi. Tafawa Valewa ya amince da a kafa Gwamnatin haxin kan qasa, don a shirya sabon zave wanda zai karvu ga dukkan sassan qasar, musamman yankin yamma da ba su yarda da cewa **UPGA** ce ta lashe zaven ba. Daga qarshe dai an yi watsi da matsalolin yamma.

A wannan shekarar dai ne 'yan Tibi suka yi boren da a cikinsa har suka hana zirga-zirgar jiragen qasa. Lokacin da aka yi sanarwar sakamakon wannan zaven, sai rikici ya tashi a yankin yamma, aka yi ta kashe 'yan hamayya. Har ya kasance tafiye-tafiye sun gagara a

wasu wurare na yamma. Waxannan rikice-rikice na qabilanci da kuma kallon da ake yi cewa ‘yan arewa ne suka kankane sha’anin mulki, sai aka samu gungun wasu hafsoshin soji suka yi juyin mulki ranar 15 ga Juanairu, 1966. Shugaban wannan juyin mulkin shi ne, Manjo Chukuma Kaduna Nzeogwu. A wannan juyin mulkin ne aka kashe Farayim Minista Sir Abubakar Tafawa Valewa da Ministan Kuxi Cif Festus Okotie Eboh da Firimiyan Arewa Sir Ahmadu Bello da Firimiyan Yamma Cif S.L Akintola da hafsoshin Soja da yawa da ba su ba da goyon bayan juyin mulkin ba, waxanda yawancinsu ‘yan arewa ne.

Masu juyin mulkin sun samu kame Kaduna. A ranar 17 ga Janairu, 1966, babban hafsan soja na wannan lokacin, Manjo Johnson Aguyi Ironsi ya qwace gwamnatin, ya tsare hafsoshin da suke da hannu a juyin mulkin 15 ga wata. Ya kuma naxa Manjo Hassan Usman Katsina a matsayin mataimakinsa. Ironsi ya yi qoqarin haxe kan ‘yan qasa ta kauce wa tsarin vangarori. Ya kuma dakatar da tsarin mulki. Wannan ne ya kawo qarshen jamhuriya ta xaya, wadda jam’iyyar **NPC** ce ke da rinjaye (Daure, 2000 :49).

2.4.3.2 Jamhuriya Ta Biyu

Wannan jamhuriya ita ce lokacin siyasa na biyu. Wannan zamanin siyasa ya kama daga 1979 zuwa 1983 (Birniwa 1987:16). Bayan da aka yi juyin mulkin 15 ga watan Janairu, 1966, wanda ya kawo qarshen jamhuriya ta xaya, sojoji sun ci gaba da jan ragamar mulkin qasar.

Sai dai, wannan sojoji da suka yi juyin mulki na farko, ba su yi qarko ba. Domin kuwa bayan wata shida ne aka samu wasu hafsoshin soja suka tunkuxe su daga karagar mulki. A ranar 29 ga watan Yuni, 1966, wasu gungun hafsoshin soja ‘yan arewa suka yi juyin mulki, inda aka kashe Ironsi da gwamnan yamma, Fajuyi. Haka kuma an kashe wasu sojoji da yawa musamman ‘yan qabilar Igbo. An xora Laftanar Kanar Yakubu Gowon a kan kujerar shugaban qasa. Ya kuma naxa Awolowo a matsayin mataimakinsa. Wannan ne ya fara shuka gyauron siyasa a harkar soja. Gowon ya bayyana cewa zai miqa mulki ga ‘yan siyasa ba da daxewa ba. Ya kuma mai do da tsarin shiya-shiya na da.

Wannan gwamnati ta Gowon ita ma ta haxu da qalubale iri-iri, musamman abin da ya shafi tsaron qasa da yawan rikice-rikice. Waxannan rikice-rikice sun taso daga gabacin Nijeriya, watau qasar Inyamurai. Laftanar Kanar Odumegwu Ojukwu ne ya fara bayyana tunanin Igbo na rashin amincewa da gwamnatin Gowon. Ojukwu yana da tunanin cewa ba Gowon ne yake da haqqin jagorancin qasar ba. Kuma ba zai yafe ‘yan uwansa da aka kashe a juyin mulkin ba. Qabilar Inyamurai qarqashin jagorancin shi Ojukwu, suka yi ta tanadin makamai. Suna ganin cewa suna da arziqin man fetur a gabas. Don haka suke tunanin idan suka valle, za su iya zama da gindinsu. Ranar 30 ga watan Mayu, 1967, sai Ojukwu ya sanar da shiyyar gabas ta zama jamhuriyar Biyafara.

Ganin haka, gwamnati ta xauki mataki ta tura jami’an tsaro a yankin domin a daidaita al’amura. A 12 ga Agusta aka samu rahotannin hare-hare da bama-bamai. Sannan kuma sojojin Biyafara suka dinga ta’addanci ga duk wanda ba xan shiyyar ba. Sai gwamnatin

tarayya da fara yaqi. Qasa ta sami kanta cikin halin qaqa-ni-ka-yi da rashin abinci da gurguncewar tattalin arziqi saboda yaqin. Qasashen waje suna ganin gwamnati tana yi wa Inyamurai kisan gilla. Wasu kuma na da tunanin cewa faxa ne tsakanin arewa da Inyamurai.

Biyafara ta samo goyon bayan qasashen duniya da dama. Ingila da Amerika da Faransa da Jamus da Isra'ila da Tanzaniya da Zambiya da Aibiri Kos da sauransu (Daure 2000:51). Bayan an xauki tsawon lokaci ana gumurzu tsakanin sojojin gwamnati da na Biyafara, sojojin gwamnati sun ci nasarar yaqin. Ranar 11 ga Janairu, 1970, sai Ojukwu da manyan magoya bayansa suka tsallake zuwa Aibiri Kos.

Duk da cewar Nijeriya ta samu bunqasa ta fuskar tattalin arziqin qasa daga albarkatun man fetur, an sami hauhawar farashi da lalacewar darajar naira. Akwai kuma handamar dukiya da ta zama ruwan dare. Saboda matsaloli da yawa da qasar ta faxa ciki, sai aka sami wani juyin mulki a ranar 29 ga watan Yuni 1975. A nan Birgediya Murtala Ramat Muhammed ya xare karagar mulki, tare da Birgediya Olusegun Obasanjo a matsayin mataimaki.

Gwamnatin Murtala ta kawo sauye-sauye da dama na ci gaban qasa. Daga ciki akwai xauke Hedikwatar qasa daga Legas zuwa Abuja da qirqiro qarin jihohi bakwai suka zama 19. Ya kuma vullo da shirin ba da ilimin Firamare na bai-xaya a 1976. Sannan ya farfaxo da tattalin arziqin qasa.

Sai dai, wannan gwamnati ba ta xore ba, domin a ranar 13 ga Fabrairu, 1976 aka kashe Murtala a wani yunqurin juyin mulki Lt Kanar B.S Dimka da wasu qananan hafsoshi suka shirya. An murqushe juyin mulkin, inda Majo Janar Olusegun Obasanjo ya haye karagar mulki. Majo Janar Shehu Musa 'Yar'aduwa ya zama mataimaki. Wannan gwamnati ta xage takunkumin siyasa. Sannan ta kafa hukumar zave ta **FEDECO** a qarqashin shugabancin Cif Michael Ani.

A ranar 14 ga watan Satumba, 1976 ne Cif Rotimi Williams, wanda Murtala ya naxa a matsayin shugaban kwamitin rubuta sabon kundin tsarin mulki ya miqa wa Obasanjo rahotansa. An samu qungiyoyn jam'iyyu da dama da suka nemi rejista, amma dai guda biyar kawai aka yi wa rijista. Waxannan jam'iyyu su ne:

i. Jam'iyyar Ciyar da Mutanen Nijeriya Gaba (**GNPP**)

ii. Jam'iyyar Qasar Nijeriya (**NPN**)

iii. Jam'iyyar Mutanen Nijeriya (**NPP**)

iv. Jam'iyyar Ceton Talakawa (**PRP**)

v.Jam'iyyar Haxe Nijeriya (**UPN**) (Daure, 2000:54) da (Birniwa, 2010:14), (Funtua, 2003).

A wannan tsari na siyasa ta biyu, gwamnati ta sa wa jam'iyyun dokar cewa kada wadda ta sa wata sifa ta addini ko qabilanci. Jam'iyyun da suka yi fice a wannan jamhuriya su ne **NPN** da **PRP**. Waxannan jam'iyyun su ne aka fi tsara wa waqoqi.

Jam'iyyar **PRP** ita ce babbar jam'iyyar hamayya ta **NPN**. Waxannan jam'iyyu suna da manufofi da qudurorinsu ga 'yan qasa. Babbar manufar jam'iyyar **NPN** ita ce wadata qasa da abinci da kuma samar da mahalli ga 'yan qasa (Birniwa, 2010:14). Sauran manufofinta sun haxa da:

i. Haxin kan Nijeriya.
ii. Tabbatar da Ingantacciyar qasa mai qaqqarfan tattalin arziqi.
iii. Bayar da haqqi ga kowane xan Nijeriya kamar yadda tsarin mulki ya shimfixa (Mashi, 1986:64).

Haka ita ma jam'iyyar **PRP**, tana da nata manufofi da qudurori kamar haka:

i. Babbar manufarta ita ce qwato haqqin talakawa daga waxanda suke ganin sun danne musu.
ii. Hana zalunci a tsakanin talakawa
iii. Inganta mutuncin al'umma
iv. Neman haqqin xan Adam kamar yadda tsarin mulki ya tanada
v. Yaxa ilimi
vi. Yin aiki tuquru domin ciyar da qasa gaba
vii. Ganin an haxe kan al'ummar Nijeriya (Mashi, 1986:65) da (Birniwa 2010:19).

A wannan jamhuriya ta biyu an shirya zave a tsakanin jam'iyyun siyasa guda biyar a 1979. Kowace jam'iyya ta tsayar da xan takararta suka goga da juna a zaven shugaban

qasa. Jam'iyyar **NPN**, wadda ita ce babba musamman a arewa ta tsayar da Alhaji Shehu Shagari. **PRP,** babbar jam'iyyar adawa ga **NPN,** ta tsayar da Malam Aminu Kano. **UPN** ta tsayar da Cif Obafemi Owolowo, **GNPP** kuma Alhaji Waziri Ibrahim ta tsayar, a yayin da **NPP** ta tsayar da Nmandi Azikiwe.

Duk da cewar dai an qalubalanci sakamakon wannan zave, an bayyana Alhaji Shehu Shagari a matsayin wanda ya lashe zaven. Owlowo ya ce **NPN** ba ta samu rinjayen xaya bisa uku ba na quri'un da aka kaxa a jahohi 19 na qasar. An rantsar da shugaban qasa Alhaji Shehu shagari, kuma shugaba mai cikakken iko. Dr. Alex Ekwueme shi ne mataimakinsa. Wannan gwamnatin shagari ta **NPN,** ba ta samu rinjaye ba a majalisa. Wannan ya sa ta yi haxin gwiwa da jam'iyyar **NPP.** Sauran gwamnoni da ba na **NPN** ba, ba su ba da haxin kai ga gwamnati ba.

A shekarar 1983 ne, kuma aka gudanar da zave a karo na biyu a jamhuriya ta biyu. Shi ma wannan zave jam'iyyar **NPN** ce ta lashe shi. A ranar 1 ga October, 1983, aka sake rantsar da Shagari a matsayin shugaban qasa. A cikin wannan zamanin siyasa ne tattalin arziqin qasa ya yi ta samun ci baya. Cin hanci da tashe-tashen hankula suka yawaita. A wannan shekara ce ta 1983 aka yi rikicin Maitatsine a Kano.

Sakamakon tattaruwar ximbin matsalolin qasa da kwashe dukiyar qasa ya zama tamkar 'yan siyasa na gayyatar sojoji ne. wannan ya sa kwatsam a ranar 31 ga Disamba, 1983, sojoji suka yi juyin mulki da ba a zubar da jini ba. Shugaban qasa da aka aza a wannan juyin mulki shi ne Manjo Janar Muhammadu Buhari, da kuma Manjo Janar Tunde

Idiagbon a matsayin mataimaki. Wannan shi ya kawo qarshen siyasar jamhuriya ta biyu. Jam'iyyar **NPN** mai rinjaye daga arewa ita ce ta mamaye harkokin mulki a jamhuriya ta biyu.

Tafiya ta yi tafiya a harkar siyasar Nijeriya. Harkokin siyasa suna ci gaba, sai dai ana samun tsoma baki daga sojoji. Wannan yake kawo koma baya a harkokin mulki da ci gaban tattalin arziqi. Siyasar jamhuriya ta uku ta kama daga 1993 zuwa 1998.

Bayan juyin mulkin da aka yi da ya kawo qarshen jamhuriya ta biyu, sojoji sun ci gaba da mulkin qasa qarqashin Janar Muhammadu Buhari. Wannan gwamnati ta yi yaqi da 'yan kasuwa masu voye kayan masarufi, kuma ta samar da su a wajen sayarwa ga ma'aikata. An kama wasu 'yan siyasa da suka wasashe dukiyar qasa. Haka kuma an kafa dokar xauri ga duk wanda aka kama da laifin buga kuxin jabu. An kawo yaqi da rashin xa'a duk faxin qasa. Da haka ne ake ga wannan gwamnati ta cika tsauri.

A ranar 27 ga watan Agusta,1985, kwatsam sai wasu sojoji suka yi juyin mulki aka murqushe gwamnatin Buhari. An xora Janar Ibrahim Badamasi Babangida a matsayin shugaban qasa, Birgediya Ebitu Ukiwe mataimaki.

Jamhuriya ta uku ta sha bamban da sauran da suka gabata. Domin zamanin siyasa ne da aka yi a tsarin angulu-da-kan-zabuwa. Watau siyasar da ta haxa da sojoji da kuma farar hula. Saboda sojoji ne suke riqe da ragamar mulkin qasa, amma a wasu matakan gwamnatoci kamar na Qananan Hukumomi da gwamnoni da 'Yan majalisa farar hula ne.

2.4.3.3 Jamhuriya Ta Uku

Wannan Jamhuriya an fara samun jirwayenta tun a shekarar 1987 lokacin da Babangida ya shirya zave a matakin qananan hukumomi, amma ba bisa tsarin jam'iyyu ba. Haka kuma an qaddamar da zaven 'yar tinqe. Bayan wannan kuma, an ba 'yan siyasa damar kafa qungiyoyin siyasa. A ranar 26 ga Maris, 1990, Babangida ya kafa hukumar zave mai suna **NEC,** aka ba Farfesa Humphrey Nwosu shugabancinta. Qungiyoyin siyasa da suka nemi rijista, duk ba a yi musu ba. A maimakon haka, sai gwamnati ta qirqiro nata jam'iyyun guda biyu, watau **NRC** da **SDP.**

Gwamnati ta xauki nauyin waxannan jam'iyyu ta gina masu ofisoshi a dukkan Qananan Hukumomi. A shekarar 1990, sai gwamnati ta shirya zaven qananan hukumomi, sannan zaven majalissar dattijai a 1992. Sannan kuma an yi zaven share fage na takarar kujerar shugaban qasa a watan Yuni. Jam'iyyar **SDP** ta tsayar da Manjo-Janar Shehu Musa 'Yar'aduwa, a inda **NRC** ta tsayar da Adamu Ciroma. Sai dai gwamnati ta rusa zaven a dalilin cewa an yi amfani da kuxi.

Bayan nan gwamnati ta vullo da wani tsarin zave na "option" A4, inda sai an zavi mutum tun daga matakin unguwarsa har zuwa qaramar hukuma da jaha sannan a zave shi a matsayin xan takara. A karo na biyu sai **SDP** ta tsayar da Cif Moshood Abiola, ita kuma **NRC** ta tsayar da Alhaji Bashir Usman Tofa a matsayin 'yan takarar shugaban qasa. An gudanar da zave a ranar 12 ga Yuni, 1993 na shugaban qasa. Sai dai an soke zaven duk da cewa Abiola yana da yaqinin cewa ya lashe shi, da kuma rinjayen da ake buqata.

Sakamakon soke zaven, sai Abiola ya shigar da qara yana qalubalantar gwamnati da ta fito da sauran sakamakon zave; kuma a rantsar da shi. Kotu dai ba ba da hukuncin a fito da sauran sakamakon ba. Don haka ta ce ta soke shi. Abiola dai ya yi ta neman agajin qasashen duniya. Ya kuma yi tsaye kai-da-fata cewar shi ya ci zave.

Kasancewar zungurar da Babangida yake ta sha daga gida da waje, sai ya yada qwallon mangoro ya huta da quda. Ya kafa gwamnatin riqon qwarya, inda aka rantsar da Cif Earnest Shonekan a matsayin Shugaba a ranar 26 ga Agusta, 1993. Sai dai wannan gwamnatin ba ta yi qarko ba, kwana 83 da kafa ta, kwatsam sai Janar Abacha ya qwace mulkin 17 ga Nuwamba, 1993.

A shekarar 1995 ne, aka kafa hukumar zave ta **NECON,** inda aka naxa Cif Sumner Dagogo Jack a matsayin shugaba. Sannan kuma aka yi wa jam'iyyun siyasa guda biyar rijista. Jam'iyyun kuwa su ne: **DPN** da **CNC** da **UNCP** da **GDM** da kuma **NCPN.**

A shekarar 1997 ne aka gudanar da zaven qananan hukumomi a qarqashin waxannan jam'iyyu guda biyar. Sannan kuma aka quduri yin zaven gwamnoni da na shugaban qasa a shekarar 1998. Sai dai a wannan shekarar ce, ranar 8 ga watan Yuni, kwatsam aka bayyana rasuwar Abacha a Asoko Rok. Wannan rasuwa ta Janar Abacha ta dagula lissafi a sha'anin siyasa da ma mulkin qasar nan.Wannan kuma shi ya kawo qarshen Jamhuriya ta uku wadda ba ta samu nasarar kafa gwamnati ba. Wannan zamanin siyasa gaba xaya ya kasance cikin tarnaqi da kama-karya na sojoji.

2.4.3.4 Jamhuriya Ta Huxu

Haqiqa akwai ka-ce-na-ce da kuma ra'ayoyi mabambanta dangane da yadda ake kallon wannan jamhuriyar ko zamanin siyasa da ake ciki. Watau dangane da lokacin da za a ce shi ne jamhuriya ta huxu. Misali, akwai masu ra'ayin cewar duk lokacin da aka gudanar da zave aka rantsar da shugaban qasa, to jamhuriya ce mai zaman kanta.[1] Ke nan, ga masu wannan ra'ayin, a iya cewa yanzu ana cikin jamhuriya ta bakwai. To sai dai kuma, kamar yadda 'yan magana ke cewa 'ra'ayi riga ne'. Saboda haka wasu na ganin cewar a jamhuriya ana la'akari ne da lokacin da farar hula suka karvi mulki ba tare da tsoma bakin sojoji ba, watau tun daga shekarar 1999 zuwa yau, (Paden, 2008 : 15) da (Birniwa, 2013 : 339) da (Bello, S. da Yusuf M.M. 2012:41-42). Ke nan, idan an xauki wannan mazahabar, to yanzu ana cikin jamhuriya ta huxu ne. Alal haqiqa a wannan bincike, an xauki ra'ayin masu ganin wannan jamhuriya ta huxu ce ake ciki, tun daga 1999, zuwa yau. Saboda dalilin cewar har yau dai tsarin mulkin 1999 ne ake amfani da shi. Kuma kamar yadda aka sani, duk lokacin da soja ya zo, yana jingine tsarin mulki ya yi amfani da doka irin tasa. Idan farar hula sun zo, su yi amfani da tsarin mulki. To har yau wannan tsarin mulkin, shi dai ne. Kuma ba a sami katsalandan ko tsoma bakin sojoji ba. Watau ba a sami wani givi ba a tsakani. Sai dai kawai, a iya cewa an sami zango zubi na kaza, dangane da zavuvvuka da lokutan da aka gudanar da su. Misali, zaven farko a wannan

[1] Hira da Dr. Aliyu Muri, Sashen Tarihi Da Harkokin Tsaro, Jami'ar Umaru Musa Yar'adua, Katsina, da kuma, Farfesa Aminu Isiyaku Yanxaki, Sashen Tarihi, Jami'ar Usmanu Xanfodiyo, Sakkwato, ranar 17-11- 2013.

jamhuriyar shi ne na 1999, sai na biyu 2003, sai na uku 2007, sai na huxu 2011, wanda cikin wannan zubin ne ake a halin yanzu.

Wannan jamhuriya ta faro tun daga shekarar 1999 zuwa yau. Bayan rasuwar Janar Sani Abacha an xora Janar Abdussalam Abubakar a kan karagar mulki. Hawansa ke da wuya ya saki fursunonin siyasa kamar tsohon shugaban qasar, Janar Obasanjo da Beko Ransome Kuti da Bola Ige da Chris Anyanwu da sauransu.

Shugaban qasa Janar Abdussalam Abubakar ya soke duk jam'iyyun siyasa da Hukumar Zave da duk zavavvukan da ta gudanar. Sannan ya yi alqawarin miqa mulki ga farar hula a ran 29 Mayu, 1999. A watan Agusta aka kafa hukumar zave mai zaman kanta (**INEC**), a qarqashin shugabancin mai Shari'a Ephrain Akpata. Aka kuma ba 'yan siyasa damar kafa jam'iyyu. Bayan an yi zaven qananan hukumomi a Disamba, 1998, sai aka zavi jam'iyyu uku da suka cancanta, aka yi musu rijista. Waxannan jam'iyuun su ne: **AD** da **APP (**wadda daga baya ta koma ANPP**)** da kuma **PDP** (Umaru, 2003:31- 32)**.** Sai kuma a 2002 aka yi wa wasu jam'iyyun rajista. Ita dai Jam'iyyar PDP, daga cikin manufofinta, sun haxa da:

i. Gyaran qasa gaba xaya

ii.Ba da hasken lantarki

iii.Samar da ruwan fomfo da sauransu (Xangulbi, 2003: 118).

Wannan Jamhuriya ga alama tana da tsawon rai. Domin kuwa an yi zubi har guda uku, ga kuma na huxu an yi 2011. A zubin farko jam'iyyun sun tsayar da 'yan takararsu inda aka kara. A zaven gwamnoni da aka yi, **PDP** ita ce ta lashe zaven da rinjaye. Jam'iyyun **APP** da **AD** suka zama 'yan hamayya. Jam'iyyar **PDP** ta tsayar da Cif Olusegun Obasanjo a matsayin xan takarar shugaban qasa. Ita kuma **APP** ta tsayar da Dr. Ogbonnaya Onu, ita kuma **AD**, ta tsayar da Cif Olu Falaye. A wannan zaven ma **PDP** ce ta lashe shi. An rantsar da Obasanjo a ran 29 ga Mayu, 1999, a matsayin shugaban qasa, Atiku Abubakar mataimaki.

Wannan jamhuriya alal haqiqa tana da sauye-sauye da salailai daban da na zamunan siyasa da suka wuce.Sannan kuma, tana da yawan jam'iyyu da salon waqoqin siyasa da na 'yan takara da sauransu. Domin zuwa shekara 2006, jam'iyyun da suke da rijista sun kai hamsin. Daga cikin waxanda suka sami rijista a wannan shekarar, akwai **DPP** ta Attahiru Xalhatu Bafarawa, gwamnan Sakkwato, da kuma **AC,** ta mataimakin shugaban qasa Alhaji Atiku Abubakar wanda ya fice daga jam'iyyar **PDP** (Paden, 2008).

Zaven 2003 shi ne zubi na biyu a inda **PDP** ta sake tsayar da Obasanjo **APP** kuma ta tsayar da tsohon shugaban qasa Janar Muhammadu Buhari a matsayin xan takarar shugaban qasa. Shi ma dai wannan zave, **PDP** ce ta lashe kujerar shugaban qasa. A wannan zubin ne Obasanjo ya so a gyara kundin tsarin mulki ta yadda zai ba shi damar

xarewa karagar mulki karo na uku. Watau an yi ta badaqalar *tazarce*,[2] a inda dai daga qarshe Obasanjo bai samu cin nasarar zarcewa ba. Saboda haka, a 2007, sai **PDP** ta tsayar da Alhaji Ummaru Musa 'Yar'adua a matsayin xan takarar shugaban qasa, tare da Goodluck Jonathan a matsayin mataimaki. Ita kuma **ANPP** ta sake tsayar da Janar Buhari.

Bayan an yi zave aka bayyana cewa Umaru Musa 'Yar'adua na jam'iyyar **PDP** ne ya lashe shi. Amma dai jam'iyyar hamayya ta **ANPP**, ba ta amince da sakamakon ba. Saboda ana ganin an tafka maguxi kuma yana cike da kura-kurai. Daga qarshe dai kotu ta tabbatar da wannan sakamakon.

Kasancewar shugaban qasa Alhaji Ummaru Musa 'Yar'adua yana fama da laulayin jiki, an yi ta kai shi qasashen waje don neman magani. A cikin shekarar 2010 aka kai shi Saudiya, inda kuma aka bayyana rasuwarsa a fadar shugaban qasa ranar 5 ga watan Mayu, 2010. Wannan ya kawo ce-ce-ku-ce a siysar Nijeriya, domin a tsarin jam'iyyar **PDP**, ana amfani da karva-karva ne. Da shirin cewar idan kudu sun yi shekara takwas, arewa ma za su yi haka. To amma sai aka karya wannan qa'ida, aka ba Jonathan mulkin qasa a ran 8 ga watan Mayu 2010, duk da cewa mulki a arewa yake, bayan Obasanjo ya yi shekara takwas wanda a kudancin qasar nan yake.

[2] Kalmar *tazarce* tana nufin hanqoron cigaba ko kasancewa a kan karagar mulki a karo na biyu. Domin qarin bayani, a duba Ngu, (2003: 111).

Zuwa 2010, jam'iyyun siyasa sun kai 63.[3] Sai dai, cikin waxannan jam'iyyun 63, huxu ne kawai aka fi jin xuriyarsu a arewaci, watau **PDP** da **CPC** da **ACN** da kuma **ANPP**. Sabuwar jam'iyyar **CPC**, Janar Muhammadu Buhari ne ya kafa ta. Wannan jam'iyyar yanzu ita ce babbar jam'iyyar hamayya a Nijeriya, musamman a arewa. Ta kuma tsayar da Janar Buhari ya yi mata takarar Shugabancin qasa a 2011. **ACN** ta tsayar da Malam Nuhu Ribaxo, **ANPP** kuma ta tsayar da Malam Ibrahim Shekarau. Ita kuwa **PDP**, ta tsayar da Goodluck Jonathan da Namadi Sambo a matsayin mataimaki (Jaridar "Leadership" Litinin 21 ga Fabrairu, 2011). Duk kuwa da rashin yardar mafi yawan 'yan arewa, musamman qungiyar Dattawan Arewa ta faxi rashin yardarta da babbar murya, wanda Adamu Ciroma yana daga cikin shugabaninta. Haka ma sauran jama'a suna ta bayyana wannan ra'ayi. Wannan zave zubi na huxu ke nan a wannan jamhuriya.

Hukumar zave ta qasa ta shirya manyan zavuvvuka a watan Afirilu na shekera ta 2011 qarqashin jagorancin Farfesa Attahiru M. Jega. Ganin irin shirin da wannan hukuma ta yi na gudanar da waxannan zavuvvuka, talakawa da 'yan qasa sun sakankance za a yi gasskiya. Saboda ganin irin sharuxxa da dokokin zave da aka gindaya. Sai dai, daga qarshe an sami kura-kurai masu yawa da zargin tafka maguxi a zavuvvukan da aka gudanar. Wanda daga qarshe, bai haifar wa qasar xa mai ido ba. Saboda rikice-rikice da qone-qone da hakan ta haifar a Nijeriya, musamman vangaren arewacin qasar, domin

[3] A duba rataye domin samun jerin sunayen jam'iyyun.

suna ganin cewar an yi masu murxiya. Waxannan rikice-rikice sun haifar da asara mai yawan gaske, ta dukiyoyi da rayukan jama'a.

An gudanar da zavuvvukan a ranaku daban-daban a cikin watan Afirilun 2011. Da farko, an shurya zaven 'yan majalissar Dattawa da na majalissar Wakilai ta tarayya ran 2 ga watan Afirilu, 2011. Har masu zave sun je rumfuna an ci gaba da zave, sai kwatsam da rana tsaka ka sami sanarwar dakatar da zaven daga Hukumar Zave ta Qasa, a kan dalilin cewar 'wai' babu 'form EC 8A 1 wanda cikinsa ne ake rubuta sakamakon zave na kowace rumfa. Wannan sanarwa ta xaure wa 'yan qasa da yawa kai. Amma dai aka tafi a haka. Sakamakon haka, sai aka tura wannan zave makon gaba, watau 9 ga Afirilu, 2011. Wannan zave ana ga shi ne mafi kyau saboda tsarin da aka yi da yadda aka gudanar da shi salin-alin. Mako da ya zagayo, sai aka gudanar da zaven Shugaban Qasa, watau 16 ga Afirilu, 2011. Jam'iyyun ACN da ANPP da CPC su ne manyan jam'iyyun adawa a wannan zaven. Duk kuwa da cewar jam'iyyun CPC da ACN, sun so qulla qawance a wannan zave, amma abin ya ci tura. An bayyana Goodluck Jonathan na PDP a matsayin wanda ya lashe wannan zave da gaggarumin rinjaye.

Kamar yadda aka saba, jam'iyyun adawa ba su amince da wannan sakamakon zave ba. Dalili kuwa, shi ne suna zargin an yi maguxi, musamman a kudu-maso-gabas da kudu-maso-kudu. Kamar dai yadda Farfesa Sagay ya bayyana ran 14 ga watan Mayu, 2011, a shafin yanar gizo (www.saharareporters.com/news) na Sahara Reporters' cewar ba zave aka yi ba a waxannan yankuna da aka ambata a sama. An dai rantsar da Goodluck

Jonathan a ranar 29 ga Mayu, 2011. Duk da cewar jam'iyyar CPC ta Janar Buhari, ba ta amince da sakamakon ba. Don haka ne ma ta garzaya kotu domin qalubalantar sakamakon zaven. Amma dai daga qarshe, kotun qoli ta tabbatar wa Goodluck da kujerar shugabancin qasar. Wannan zave da aka yi, shi ne ya kawo kafuwar zango ko zubi na huxu a qarqashin jamhuriya ta huxu.

Jam'iyyar **CPC** ita ce ta zama babbar jam'iyyar hamayya ta **PXP,** Wadda take so ta qwace mulki daga hannun jam'iyya mai mulki. Daga cikin manufofin wannan jam'iyyar ta CPC sun haxa da:

i. Kafa mulki ta hanyar Dimukaraxiya bisa kundin tsarin mulki na qasa, domin samar da kyakkyawan yanayin rayuwa da tattalin arziqi ta yadda za a zaburar da 'yan qasa su zama masu amfani da ci gaban qasa.

ii. Ciyar da tsarin dimukaraxaya gaba a dukan matakan gwamnati. Da yaqinin cewa mutane su ke da 'yancin kafa gwamnati bisa kundin tsarin mulkin Nijeriya.

iii. Xaukar nauyin 'Yan takara a zavuvvuka a dukan matakai na gwamnati.

iv. Bin duk wasu hanyoyi da suka dace don cim ma dukkan manufofi da qudurorin jam'iyya.[4]

[4] An sami wannan bayani a kundin tsarin manufofi na jam'iyyar CPC wanda ba a buga ba.

A qoqarin da jam'iyyu hamayya ke cigaba da yi na ganin sun karve mulki daga hannun jam'iyyar PDP, musamman a zave mai zuwa na 2015, ba su yi qasa a gwuiwa ba. Domin kuwa sun cigaba da wannan gwagwarmaya. Jam'iyyun da suke wannan qoqarin haxewa wuri guda, su ne: ANPP da CAN da APGA da kuma CPC. Daga qarshe dai a ranar 11 ga watan Mayu, 2013, an yi babban tao wanda waxannan jam'iyyu suka haxu, suka kuma amince da qawancen dunqulewa wuri guda a matsayin jam'iyya guda mai suna APC (All Progressives Congress). Kaxan daga cikin waxanda suka halarci wannan taro sun haxa da: Janar Muhammadu Buhari, wanda kuma shi ne jagoran Jam'iyyar CPC da Asiwaju Bola Ahmed Tinibu da Cif Bisi Akande da Alhaji Layi Muhammad dukansu na Jam'iyyar ACN da Dr. Ogbonnaya Onu da Alhaji Attahiru Bafarawa da Malam Ibrahim Shekarau da Sanata Sani Yariman Bakura daga Jam'iyyar ANPP da kuma Owelle Rochas Okorocha daga Jam'iyyar APGA. Ga ma abin da Janar Muhammadu Buhari ya faxa a jawabinsa a taron qasa na jam'iyyar CPC a Abuja, game da burinsu na yin qawancen:

"Dole ne mu fahimci cewa, mu kuma yarda taronmu na yau zai shiga cikin tarihin qasar nan. Ko dai mu yi qoqarin kawo gyara ko kuma mu kasa a yi tir da mu daga yanzu har zuwa wani tsawon lokaci. Mafi yawan masu fashin baqin siyasa a qasar nan sun daxe da bayyana cewa, mafita kawai ga wannan qasa ita ce jam'iyyun hamayya su dunqule wuri guda domin su fattataki PDP! "[5]

Kamar dai yadda aka sani ne cewar al'amuran siyasa cike suke da gwagwarmaya ta neman 'yanci da neman mulki da sauransu. Sannan kuma kasancewar mai rai bay a rasa

[5] Jawabin Janar Muhammadu Buhari a taron qasa na jam'iyyar CPC a Abuja, ranar 11 ga watan mayu, 2013, shafi na 4.

motsi, Wannan shi ne ya sa ita ma jam'iyya mai mulki ba a bar ta a baya ba wajen wannan gwagwarmaya da 'ya'yanta (PDP) ke yi. Dalilin haka ne a cikin 'yan jam'iyyar aka yi ta samun rigingimu , inda aka samu jam'iyyar da dare gida biyu; sabuwa da tsowar PDP. Tsohuwar it ace ta Shugaban Qasa Goodluck Jonathan, qarqahin jagorancin jamiyya na Alhaji Bamanga Tukur. Sabuwar kuwa, tana qarqashin jagorancin Alhaji Abubakar Kwu Baraje. Wannan jam'iyya dai ta samu farraqa a wajen taron qasa ta shirya a inda Alhaji Atiku Abubakar da wasu gwamnoni biyar suka ja daga a gefensu dabam. Daga qarshe dai bayan da dangantaka ta yi tsami, duk da tarurruka da aka yi da manyan jam'iyya da suka haxa da Shugaban Qasa kansa da Janar Olusegun Obasanjo da Janar Babangida da sauransu, abin ya ci tura. Waxannan gwamnoni sun valle daga jam'iyyar PDP suka koma APC a ranar 26 ga watan Nuwamba, 2013.[6] Waxannan gwamnonin kuwa su ne: Dr Rabi'u Musa Kwankwaso (Kano) da Aliyu Magatakarda Wamakko (Sakkwato) da Alhaji Murtala Nyako (Adamawa) Chibuiki Rotimi Amaechi (Rivers) da Alhaji AbdulFatah Ahmed (Kwara). Waxannan gwamnoni dai sun bar jam'iyyar PDP ne saboda rashin gamsuwa da suka yi da shugabancin Alhaji Bamanga Tukur. Da kuma buqatar su ta cewar Shugaban Qasa ba zai yi takara ba a shekara ta 2015 da dai sauran matsaloli na jam'iyyar. 'Yan iya magana na cewa 'qarshen tika-tika tik!' Alhaji Bamaga Tukur shi ma dai bayan al'amura sun yi ta tafarfasa, ya yada qwanllon mangoro, a inda ya yi murabus daga shugabancin jam'iyyar a ranar 15 ga watan Janairu, 2014. Duk da

[6] Shirin Dimukuraxiya Adon Qasa, shirin safe na Rediyon VOA, Laraba 12 ga watan Fabrairu, 2014.

haka dai, an yi ta samun ficewar ‘ya’yan jam’iyyar PDP zuwa APC. A inda ake ta samun ‘Yan Majilisun Tarayya da Majalissar Dattawa da magoya bayan PDP da yawa , suna ta barin ta suna komawa APC . Misali, an sami Sanatoci goma sha- xaya da ‘Yan Majalissar Wakilai talatin da bakwai gaba xaya sun koma APC. Haka Alhaji Atiku Abubakar shi ma, ya bar PDP ya koma APC.[7] Daga cikin dalilan da Atiku ya bayar na barin jam’iyyar PDP ya koma APC, sun haxa da cewar yana so a qwace mulki daga hannaun PDP saboda ‘yan Nijeriya sun gaji da mulkinta.

Don haka, ana buqatar canji a 2015. Alhaji Atiku Abubakar dai ya yi rajista da jam’iyyar APC ne, ranar 5 ga watan Fabrairu, 2014.[8] Haka kuma Atiku yakan faxa cewar jam’iyyar PDP ta mayar das hi saniyar ware, duk kuwa da kasancewarsa daga cikin ‘yan Kwamitin Amintattu na jam’iyyar (PDP).

Haka dai wannan guguwar neman canji take ta kaxawa a wannan a lokaci a cikin wannan Jamhuriya ta huxu. Ana ta samun ‘yan siyasa na canza sheqa daga wannan jam’iyya zuwa wannan. Domi kuwa har daga APC ana samu wasu na komawa PDP. Misali, tsohon gwamnan Kano, Alhaji Ibrahim Shekarau da tsohon gwamnan Jihar Sakkwato, Alhaji Attahiru Xahatu Bafarawa, sun bayyana komawarsu jam’iyyar PDP daga APC. Ana ta samun rigingimu a tsakanin ‘yan wata jam’iyya da wata, da ma tsakanin ‘ya’yan jam’iyya guda. Ba a dai san ma ci tuwo ba, sai miya ta qare.

[7] Domin qarin bayani a duba Jaridar *Leadership* ta ranar Talata 4 ga watan Fabrairu, 2014, shafi na biyar (5) da na talatin da takwas (38).

[8] An duba Jaridar *Dailytrust* ta ranar 6 ga watan Fabrairu, 2014, shafi na takwas (8).

Haka kuma, Shugaba Goodluck Jonathan ya shirya Babban Taro na Qasa (Sovereign National Conference) wanda a cikinsa ne za a tattauna makomar qasar Nijeriya . Shugaba Goodluck Ebele Jonathan ya naxa tsohon Babban Jojin Nijeriya Mai Shari'a Idris Kutigi ya jagoranci taron, a inda Farfesa Akinyemi zai zama mataimaki, Dr Azinge kuma Sakatare (Dailytrust, Tuesday, March 4, 2014, p3).Taron zai tattauna a kan muhimman batutuwa da suka shafi qasa da gano matsalolin da ke addabar ta domin ba da shawarwarin yadda za a warware su. Muhimman batutuwan da taron zai duba sun haxa da maganar tsarin gwamnati da rabon arziki da tafiyar da dukiyar qasa da maganar qirqiro sababbin jahohi da qananan hukumomi da maganar 'yan sandan jihohi da zaven qananan hukumomi da maganar zama xan qasa da haqqoqi da 'yancin qananan yara da dai sauransu (Dailytrust ta Litinin 17 ga Maris, 2014). Shugaban Qasa Goodluck Ebele Jonathan ya qaddamar da wannan taro a ranar Litinin 17 ga Maris, 2014. Za a xauki tsawon wata uku ana yin sa. Taron ya qunshi wakilai 492 daga sassa daban- dabam na qasar nan da qungiyoyi da wakilan addinai da sauransu. Taron dai zai yi zaman muhawara da tattaunawa don samo wa qasar nan alqibla kan matsalolin da ke damun ta. Jama'ar qasa dai suna t ace-ce-ku-ce game da taron. Domin wasu suna ganin ba shi da wani muhimmanci,kasancewar a sha yin makamancinsa a lokutan baya amma ba a yi amfani da sakamakon tarurrukan ba. Wasu kuma suna goyon bayan taron da tunani cewar zai warware matsalolin da suka dabaibaye qasar. Abin yi dai, shi ne a jira a gani watakila, ko kwalliya za ta biya kuxin sabulu.

2.5 Samuwar Waqoqin Siyasa

An sami waqoqin siyasa kama tun daga na siyasar Musulunci, har zuwa na siyasar jam'iyya. A qarni na 19 ne aka fara samun waqoqin siyasa a lokacin jihadin Shehu Usmanu Xandofiyo. Misali, "waqar Tsarin Mulki na Musulunci," da "Waqar Murnar cin Birnin Alqalawa" dukkansu na Shehu Abdullahi Fodiyo. Misali a cikin "Waqar Tsarin Mulki na Musulunci," Abdullahi Fodiyo na cewa:

"Ku saurara gabatan musulumina,
Ku bi ta ku bar sarautak kafirina.
Musulmi manya-manya da salihansu,
Ka zaven mai gabatat musulmina.
Su taru su xauki alwashi na xa'a,
Ga foron nan na alqur'ani da sunna."
(Yahaya, 1988:58).

A waxannan baitoci ana bayyana yadda ya kamata musulmi su zavi shugabanni tare da yi masu biyayya.

Haka ma a qarni na 20, Sarkin Musulmi Attahiru na I ya yi waqa mai suna: 'Waqar Zuwan Annasara Qasar Hausa," wadda ya yi a 1903 don nuna bijirewa ga Turawan mulkin mallaka. Ga misalin abin da yake cewa a baiti na 1-5 cikin waqar:

1. *"Bismillahi na nufi za ni waqa,*
Bisa maqiya Muhammadu Annasara.
2. Muna roqo ga sarki mai sarauta,
Mu samu fita mu bar jama'an Nasara.
3. Mutane sun xime wasu sun makabta,
Yawaici sun zamo jama'an Nasara.
4. Idan Allahu ka nufi sai mu zauna,
Muna roqo ka vata nufin Nasara.
5. Idan mun samu iko munka tashi,

Ka kai mu Madina nesa ga Annasara."

(Yahaya,1988:88).

Shi ma Muhammadu Tukur ya rubuta "waqar Baqin Mari," wadda a cikinta ne yake suka ga sarakuna kan irin zaluncin da suke yi wa talakawa (Dangulbi, 2003:82). Jagoran Jihadi Shehu Usmanu Xanfodiyo, ya rubuta "waqar Tabban Haqiqan" don yin gargaxi da faxakar da 'yan'uwa musulmi kan turbar da ya kamata su bi domin samun tsira duniya da lahira. Ga misalin abin da yake cewa a cikin waqar:

" Kui nazar 'yan'uwa ku samu ku duba,
Don nasiha ku zam faxi don muhibba,
Mui ta bin gwadabe mu tsere azaba,
Duk mu saurari za ni waqa ku tuba,
Don ku samu ku tsira tabban haqiqan.
Ko mutum ya zamo mutum mai muqami,
Ko sarauta gare shi koko adini,
Ko ganiyyi morawaci k o karimi,
Wanda bai girgiza ma Sarkin Musulmi,
Shi ka mutuwa da jahalu tabban haqiqan."

(Yahaya,1988:54).

Idan aka lura, dukan waxannan waqoqi sun shafi siyasa ce ta Musulunci, ba ta jam'iyya ba. Waqoqin suna bayani ne na yadda ya kamata shugabanci ya kasance a Musulunci. Watau suna fayyace haqqoqi da 'yancin talaka da kuma amanar talaka da take kan shugabanni. Wannan shi yake fahimtar da mu yadda zamantakewa ta kamata ta kasance tsakanin masu mulki da mabiyansu a tsari na Musulunci.

Duk da cewa waqoqin qarni na 19 a kan siyasar addinin Musulunci suka dogara, sun ba da haske ga marubuta waqoqin siyasa a qarni na 20. Abin da za a fahimta a nan, shi ne

waqoqin qarni na 19, ba a gina su a kan jam'iyyun siyasa ba. Sai a qarni na 20 ne aka fara samun waqoqin siyasa na jam'iyya sakamakon samuwar jam'iyyun siyasa a Nijeriya. Waxannan jam'iyyu kuwa sun samo asali ne daga qungiyoyin siyasa daban-dabam da suka haxa da na neman 'yancin kai da na fafutukar ciyar da yankunan al'ummar qasar nan gaba ta fuskar mulki da tattalin arziki. (Birniwa, 1987) da (Hiskett, 1975).

A tsakanin shekara ta 1946 zuwa 1966 ne aka sami vullowar alfijirin siyasar jam'iyya a qasar Hausa (Hiskett, 1975:4). A wannan lokacin ne aka yi zamanin siyasar farko. An sami waqoqi da dama da aka yi na siyasa. Misali, "*Waqar Siyasa Zamanin Salama*". Ta Bello Gixaxawa da "*Waqar Yabon Sardauna*", ta Shekara Sa'ad da *"Waqar Tauraron Zamani*," da "*Waqar Jiya Da Yau*," na Aqilu Aliyu, da sauransu.

Haka ma a jamhuriya ta biyu wadda ta yi zamani daga 1978 zuwa 1983, (Birniwa, 1987:16) an ci gaba da samun waqoqin siyasar jamhuriya. Misali, an sami waqoqi da yawa da suka haxa da "Waqar A Zavi 'Yanfi' Yan, "ta Malam A. Yabo da "*Waqar Ya Allah Ka Ba Mu Aminci*", ta Musa Madugu da "*Waqar Fi'arfi Maganin Zamba*," da *"Waqar Varawon Akwati*," na Auwalu Isah Bunguxu.

A jamhuriya ta uku ma wadda ta yi zamaninta daga 1990 zuwa 1993 (Daure, 2000: 61-64), duk da cewar ba ta xore ba, an sami waqoqin siyasa a lokacinta. Jam'iyyun siyasa biyu rak ne suka yi yayi a duk faxin Nijeriya a wannan zamanin siyasa, watau "N.R.C" da "S.D.P an yi waqoqin siyasa da yawa a wannan jamhuriya. Misali, akwai "*Waqar SDP Nasiha*" ta Auwalu Isa Bunguxu. Akwai kuma *"Waqar Dokta Kabiru Gaya Kai Ka Ci*

Zave," da "*Waqar Ina Gizon Yake,"* na Garba Gashuwa na jam'iyyar NRC (Funtua, 2003:62).

A jamhuriya ta huxu kuwa wadda ta fara daga 1999 zuwa yau (Paden, 2008:10), an sami kakar waqoqin siyasa da baje kolinsu da suka xauki salo iri daban-dabam, da kuma jigogi iri-iri.

Waxannan waqoqi an same su da yawa ta yadda sai wadda hannun mutum ya kai kanta, ko kuma kunnensa ya jiye masa. Misali, akwai "*Waqar Shegiyar Uwa*" da ta "*Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba,* " na Haruna Aliyu Ningi da *"Waqar Mu Mun Yi Maraba,"* ta Auwalu Ibrahim Gwam Gwammaja Kano da "*Waqar PDP Power Yanci,"* ta Shu'aibu Zakari 'Yanmedi duk kansu na PDP. Sannan akwai *"Waqar Ba Ma Shakka Cikin Qasa Ita Ce Jagaba PDP*, " ta Aminu Ibrahim Dandago Kano da "*Waqar Nijeriya Riqo Sai Mai Gaskiya*," da "Waqar Nijeriya A Yau An Mana Murxiya" na Ibrahim Yala Hayin Banki, dukkansu na Jam'yyar APP. Haka kuma akwai "*Waqar Mu Kasa Mu Tsare Mu Raka"* ta Mohammed Aminu Musa Dako, da "*Waqar Yakubu Lado,* " ta Ibrahim Xanraka na Jam'iyyar CPC. Da dai sauransu da yawa.

Waqoqin siyasar jamhuriya ta huxu suna da jigogi iri daban-dabam, kama tun daga waxanda aka tsara domin tallata manufofin jam'iyya da masu tallata 'Yan takara, har ya zuwa waqoqin da ke bayyana manufofin gwamnati da dai sauransu. Kuma mafi yawan waxannan waqoqin, an shirya su ne ga manyan jam'iyyu watau PDP da APP (Funtua, 2003:81-83).

Xangulbi, (2003:93) ya karkasa waqoqin siyasa gaba xaya zuwa manyan rukunoni guda biyu; waqoqin Tallata jam'iyyu da kuma waqoqin yabon shugabanni, waxanda dukansu ya bayyana cewa sun qunshi faxakarwa da zambo da Habaici domin jawo hankalin masu saurare.

Saboda haka, idan an lura, za a ga cewar waqoqin siyasa na wannan jamhuriya na da rassan jigogi da dama, wanda ya bambanta salonsu da waqoqin siyasar farko da na biyu. Domin mafi yawan waqoqin siyasa ta farko, sun fi ba da qarfi ne a kan yaxa manufofi da tallata jam'iyya. A wannan jamhuriya kuwa sun fi karkata ga tallata 'yan takara (a yawancin waqoqin).

2.6 Dalilan da Suka Haifar da Sabon Salo a Waqoqin Siyasa a Jamhuriya Ta Huxu

Zamani goma, Sarki goma" in ji Hausawa. Wannan batu zai iya zama abin lura da irin yanayin da waqoqin siyasa suka shiga a yau. Ko kuma a ce sabon salon da suka xauka. Kowane zamanin siyasa da irin rawar da ya taka ta fuskoki daban-dabam, kamar salon yaxa manufofi da yaqin neman zave da makamantansu.

Babbar hanyar da 'yan siyasa suke bi wajen yaxa manufofi da tallata 'yan siyasa, ita ce amfani da "waqa". Wannan kuwa ba ya rasa nasaba da cewar waqa ita ce mafi saurin karvuwa da kuma son saurare ga jama'a. Haka kuwa, shi ne ya sa mafi yawan ayyukan malaman Jihadi waqoqi ne (Sa'id, 1978:66).

A kan haka su ma 'yan siyasa kan yi amafani da waqoqi a mafi yawan lokuta. Waxannan waqoqi sun xauki salailai daban-dabam tun daga zamanin siyasar farko har zuwa yau.

Idan aka yi la'akari da waqoqin siyasar farko da ta biyu, za a ga cewar babban jigonsu, shi ne yaxa manufofin jam'iyyun siyasa da tallata su. A cikin waqoqin ne suke bayyana aqidun siyasun da kuma shugabanninsu. Waqoqin sukan qunshi yabo da zuga da habaici a tsakanin jam'iyyun. Ta haka ne ake garza shugabannin siyasa da kambama jam'iyyun ta yin yabo da zuga gare su. Haka kuma suna kushe abokan hammayya ta yin amfani da habaici da zambo da dai sauransu. Misali, a "Waqar 'Yan Sawaba" ta Gambo Hawaja inda ya ce:

"NEPU ta kai ga Sakkwato,
Har wajen Yerwa taf fito,
Duniya mu ka ambato,
NEPU jirginta na fito,
Masu son tsai da gaskiya."

(Birniwa, 1987:178)

A nan mawaqin yana kambama jam'iyyarsu ne tare kuma da yabo a gare ta. Sannan kuma a "Waqar Jiya Da Yau" ta Aqilu Aliyu, yana cewa (baiti na 6-7):

6. *"Ga abin ajabi a Yarwa,*
Mun ga qato ba muruwa,
Ai shirim ne babu inuwa,
Mun wuce mun bar shi baya.
7. Ya aro bakin hukuma,
Ya yi qarya don shi koma,
Sai shi zauna shi ta hamma,
Kaico! Ango ba amarya."
(Birniwa, 1987:149).

A waxannan baitoci za a lura da cewar habaici ne ake yi wa wani xan jam'iyyar NPC. Duk dai idan aka duba waqoqin siyasar farko cike suke maqil da irin waxannan jigogi.

Amma savanin waqoqin wannan zamanin siyasa da suka xauki wani sabon salo da ya fi raja'a a kan tallata 'yan takara kacokam, maimakon bayyana manufa ko yaxa aqida ko nuna bijirewa ga 'yan siyasa. Misali shi ne a waqoqin Haruna Aliyu Ningi na "*Waqar Shegiyar Uwa*" da "*Waqar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba*," lokacin da ubangidansa Atiku Abubakar ya bar PDP ya koma AC. Da kuma waqar Dauda Kahutu Rarara da ya yi inda ya bar ubangidansa Shekarau, wanda ya yi waqa ta habaici gare shi mai suna "*Da Wa Da Wa Ta Vare.*"

Hausawa na cewa idan kixa ya canza, to rawa ma sai ta canza. Wataqila, za a iya cewa wannan karin maganar, ta yi daidai da abin da yake faruwa yanzu a fagen waqoqin siyasa. Kasancewar a da, aqida ce aka fi yaxawa, amma yanzu, talla ta fi yawa a mafi yawan waqoqin. Don haka, a nan za a iya hango wasu daga cikin dalilan da suka haifar da wannan sauyi da aka samu. A jamhuriya ta huxu an sami sauye-sauye da dama, musamman ga su kansu 'yan siyasar da kuma yanayin yadda suke gudanar da ita, da kuma yadda suke kallonta (suka xauke ta). Daga cikin dalilan da ake da su, za a iya fahimtar su da ra'ayoyin da wasu suka bayar. Misali, Xalladi, (2003:68) ya bayyana cewa siyasa kasuwanci ne, wanda kuma akwai riba akwai faxuwa a cikinsa. Haka ma, Muri (2011)[9] na ganin cewar irin wannan sauyi na salon waqoqi ya samu ne dalilin halin da qasa ta sami kanta na cin hanci da son kuxi, saboda haka maimakon aqida, sai a yi

[9] Hira da aka yi da Dr. Aliyu Muri na Sashen Tarihi Da Harkokin Tsaro, Jami'ar Umaru Musa Yar'adua, Ktsaina ranar Alhamis, 24/11/2011.

waqoqin tallata ‘yan takara. Ya bayyana ‘yan Nijeriya da cewar “kamar kumbo, kamar kayanta” watau dai ‘yan Nijeriya yawanci, kuxi kawai ake so.

Haka shi ma Xan Bilki Kwamanda ya bayyana siyasar yanzu da: “Siyasar a samu, ba ta aqida ba”[10] Watau ‘yan siyasa na yin ta ne don abin da za su samu, ba don aqida ba. Haka kuma kowane zamanin siyasa yana zuwa da mawaqansa da kuma irin waqoqinsa daban da sauran jamhuriyoyin da aka yi a baya. A jamhuriya ta uku (3), an sami waqoqi da suke da yanaye-yanaye daban da na lokutan siyasar da suka gabata. Misali a Jamhuriya ta farko an gina siyasa ce a kan aqida da kuma kishin qasa da gwagwarmayar neman ‘yanci ga talakawa da masu mulki. (Funtua, 2003:67).

Saboda haka, daga waxannan dalilai da aka ambata a sama, lallai za a iya cewar kamar yadda kowace jamhuriya take zuwa da irin waqoqinta, to haka ma a jamhuriya ta huxu aka samu sauyin salo a waxannan waqoqi, musamman saboda halin fatara da talauci da ake ciki. Sannan kuma da kishin qasa da ya yi qaranci a mafi yawan zukatan ‘yan Nijeriya, na daga cikin dalilan da suka sa aka rasa aqida a zukatan mafi yawan ‘yan siyasa. Don haka maimakon yaxa aqida, sai suke fafutukar neman abin da za su saka aljihunsu, ba abin da talaka zai amfana daga mulkinsu ba. To haka waqoqin siyasar, mafi yawa ana shirya su ne don a tallata wani xan takara, maimakon jam’iyyarsa, don kawai a sami xan abin hannunsa.

[10] Hira da aka yi da Xan Bilki Kwamanda a shirin Sashen Hausa na Rediyon VOA na ranar 20/06/2012.

Wannan shi ya haifar da sabon salo a waqa, wanda ya rinjaya a kan tallata ‘yan takara.Watau dai ana samun waqoqi da ake yi wa wasu xaixaikun ‘yan siyasa . Savanin waxancan lokutan, musamman na jamhuriya ta xaya da ta biyu, da aka shirya waqoqi da suke tallata aqida da bayyana manufofi jam’iyyun siyasa. Kamar yadda ‘yan siyasar wancan lokacin suna da aqida da kuma tausayin talaka a zukatansu. Ba kwaxayin abin da za su samu ba suke. Shi ya sa su kansu masu shirya waqoqin sukan ba da qarfi ga tallata aqida. Saboda ‘yan siyasar kansu, sun sa aqida da kishin qasa a gabansu.

A halin yanzu an sami sauyin salon waqoqin siyasa saboda wasu dalilai da suka haxa da:

i. Salon siyasar kanta ya canza salo ta yadda sai an ba dakuxi a zavi xan takara. Ke nan a wannan zamanin siyasa kusan a ce ba a siyasar aqida sai ta ubangida da kuma masu gida rana (kuxi).

i. Qarancin aqidar siyasa, hatta ga su kansu ‘yan siyasar, ya haifar da wasa da ‘ya’yan banki (kuxi) da amfani da ‘yan banga a fagen yaqin neman zave. Ta haka ma masu shirya waqoqin za a ga cewar ba suna yi ne don aqida ba, a’a, suna yi ne don abin da za a ba su a mafi yawan lokuta.

ii. Su kansu mafi yawa ‘yan siyasa suna shigar ta ne kawai don hangen irin lagwadar da za su samu. Don haka ne wasu ba su fahimci mene ne siyasa ba. Don haka ba su yaxa manufofin jam’iyyunsu, sai dai su mai

da hankali ga tallata kansu. A kan haka, akan shirya masu waqar da za ta tallata su.

iii. Su kansu masu shirya waqoqin siyasa na yanzu, sun bambanta da na zamanin siyasar farko irin su Mudi Sipikin da Aqilu Aliyu da Gambo Hawaja da sauransu, waxanda su ‘yan aqidar siyasa ne.

Don haka, aka samu waqoqqin da tallar ‘yantakara suke yi. A cikin waqoqin yana da wuya su bayyana manufofin jam’iyyun. Wani lokaci ma sunan jam’iyyu kawai suke ambatawa.

2.7.0 Jigogi da Salon Waqoqin Siyasa.

Masu shirya waqa mutane ne fasihai da Allah ya hore wa basira da zurfin tunani kan al’amarin rayuwa. Don haka ne masu waqoqin siyasa suke faxin albarkacin bakinsu dangane da abubuwan da suke faruwa yau da kullum a duniyar siyasa. A cikin waqoqinsu, sukan faxakar ko su tallata da yin yabo ko habaici, ko ma a wasu lokuta su nuna bijirewa ga wasu siyasu ko shugabanninsu. Sukan yi hakan ne kuwa ta amfani da salo iri daban-daban don ganin sun isar da saqonsu ga jama’a.

Dangane da wanann ne ake so a wannan babi a yi bayanin wasu daga cikin jigogin waqoqin siyasa da suke isarwa da ya shafi jama’a ko jam’iyyun siyasa ko kuma masu jan ragamarsu. Irin waxannan saqonni sukan qunshi yabo ko habaici ko faxakarwa ko kushewa da sauransu. Haka ma sukan yi amfani da salo a cikin waqoqin kamar siffantawa ko jinsintarwa ko kwatantawa da sauransu.

2.7.1 Jigon Faxakarwa

Jigo dai masana da dama sun tofa albarkacin bakinsu game da shi. Misali Yahaya da Xangambo (1986:103) da Mukhtar (2004:33) da Xangambo (2008:12) da sauransu, duk sun bayyana jigo da saqon da mawallafi ke son isarwa ga jama'a.

Faxakarwa hanya ce da mawaqa ke bi wajen wayar wa jama'a kansu dangane da muhimmanci ko amfanin wani abu sabo da ya zo ga jama'a ko qasa baki xaya (Xangulbi, 2003:109). Don haka, a iya cewa faxakarwa hanya ce da mawallafa ke amfani da ita don nuni ga jama'a game da wani abu da ko dai ba su fahimce shi ba, ko kuma sun shantake game da abun domin su falka su fahimci abun domin su amfana da shi.

Dangane da jigogin faxakarwa kuwa a iya cewa ana samun waqoqi da yawa da suke faxakar da jama'a ga manufofin jam'iyyu da na gwamnatoci daban-dabam. Wannan faxakarwa kuwa ana yin ta ne kamar yadda aka ambata a baya domin jama'a su fahimci alfanun da waxannan jam'iyyu suke da shi ko kuma a faxakar da su ga amfanin mulkin dimokaraxiya ya qunsa. Misali: Auwalu Isa Bunguxu a waqarsa "*Waqar Mulkin Santsi*" a baiti na 11 – 13 yana cewa:

11. "*Santsi ba hanya ta bi ba,*
Ba kuma hanyar lafiya ba,
Duk mai bi in bai sani ba,
To ya sani in bai bari ba,
Ba zai qare lafiya ba.

12. Ku jama'a da kun kiyaye,
Santsi cuta ne a voye,
Domin shi ke vata yaye,

'Ya' yaye su qi bin iyaye,
Ba ma girmama maluma ba.

13 Mu fa Aminu Kano muke bi,
Domin kau shi ne muhibbi,
Mai yaqi ko ba takobi,
Shi ne kyakkyawan marabbi,
Mu ba za mu bi Xangiya ba ."
(Shehu, 2005:5)

A waxannan baitoci Auwalu Bunguxu yana faxakar da mutane cewar su gane fa santsi, watau vangaren Abubakar Rimi na jam'iyyar P.R.P, ba hanyar bi ba ce ba. Domin kuwa duk wanda ya bi ta, ba zai gama lafiya ba. Sannan kuma suna vata tarbiyyar 'ya'yan mutane. Don haka kar a bi su.

Haka ma dai Auwalu Isa Bunguxu a waqarsa mai suna "*Fi'arfi Maganin Zamba,*" yana cewa a baiti na 1 – 2 da na 4:

1. "*Jama'a ku tsaya ku saurara,*
Ku ji zancena ku ko lura,
Magana ce za ni tsattsara,
Kowanenku ya bi ni ba tara,
Daga yaro har zuwa babba.

2. *Ita fi'arfi muradinta,*
Ta ga ta hana dukkanin cuta,
Tai adalci a mulkinta,
Ba ta bar kowa zalama ba.

4. *Mu bi fi'arfi mu bar wasa,*
Kowa zai sami 'yancinsa,
A riqe shi a ba shi hakkinsa,
Daga shi har ma iyalinsa,
Ba za su zaman talauci ba."
(Birniwa, 1987:446).

A waxannan baitoci, Auwalu Bunguxu yana faxakar da jama'a game da buqatar fi'arfi idan ta hau mulki, za ta hana zalunci kuma ta tsai da adalci domin talakawa su huta, watau su samu sauqin rayuwa. Sannnan kuma talakawa kowa zai sami 'yancinsa, a kuma ba shi hakkinsa.

Haka ma Haruna Aliyu Ningi a waqarsa "*Shegiyar Uwa"* ya faxakar da al'ummar Nijeriya kan, illolin jam'iyyar PDP. Misali: baiti na 24 da 26.

24. "*Ka sayar da dukkan qadarar qasarmu,*
Ga shi ba ruwan sha a maqogaronmu,
Babu magani don jama'ar qasarmu,
Me kake nufi? Ka facalar da mu kamar raga.

26. Ga abinci tsada da ya gagare mu,
Ga baqin talauci da ka sa qasarmu,
Ga rashin tsaro, har a cikin gidanmu,
Har Abuja, an saba fashi cikin garin goga.
(Tsoho, 2013:366- 367).

Haruna Ningi a nan yana faxakar da al'umma a kan matsalolin da gwmnatin PDP ta haifar wa qasar, kamar cefanar da qaddarorin gwamnati da matsalar rashin ruwan sha da tsadar kayayyaki ta yadda abubuwan more rayuwa na gagarar talaka. Ga kuma rashin tsaro da ya addabi qasa wanda har ta kai ga a babban birnin tarayya Abuja ma, fashi ake yi. Don haka mutanen Nijeriya su farga, su bar wannan jam'iyya domin a samu mafita ga waxannan matsaloli.

2.7.2 Jigon Yabo

Masu shirya waqa musamman ta siyasa, suna amfani da yabo yadda za su fito da darajar wani ko wata jami'yya. Waqoqin siyasa don haka, cike suke da yabo ta fuskoki daban-daban. Xangulbi ya bayyana ma'anar yabo da cewa;

> "*Yabo shi ne faxar wasu abubuwa ko kalmomi nagari game da wani mutum ko wata qungiya ta mutane waxanda idan aka ji su za a so mutumin ko mutanen ko a qara ganin girmansa da kwarjininsa*."
> (Xangulbi, 2003:132).

A wannan bincike za a iya bayyana yabo da cewar:

> *"Yabo shi ne faxar kalmomi nagari a kan mutum ko wani abu don fito da darajarsa ta yadda jama'a za su so shi, ko kuma su qara son sa*."

Kamar yadda aka bayyana a baya, mawaqa na amfani da kalmomi da kalamai na yabo a cikin waqoqinsu. Ana amfani da waxannan kalamai domin xaga darajar abu ko mutum don kwarzanta shi. Ga wasu misalai na yabo:

Ibrahim Hayin Banki a waqarsa, "*Nijeriya Riqo sai Mai Gaskiya",* a baiti na 14, yana cewa:

> 14. "*Lallai Daura kin yi xa wanda yake da kyau,*
> *Wanda idan na gan shi ni ba na zud da yau,*
> *Ku jama'a ina kira sai ku riqe da kyau,*
> *Sannu Buhari shugaban 'yan Nijeriya*."

A nan yana yabon Janar Buhari ta fuskar asali na gari da halitta (qirar jiki) domin kwarzanta shi da kuma tallata shi ga jama'a, su zave shi a matsayin shugaban qasa.

Haka kuma, Shu'aibu Zakari 'Yanmedi a waqarsa "*Tarayya Muke Magana: Manufofin Gwamnatin Mutawalle*" yana cewa"

"Da Sardauna na nan da rai, na rantse ba zan kafara ba,
Da ya ba ka goyon baya ba zai adawa ba,
Da Malam Aminu Kano na nan ba zai adawa ba,
Halayensu na halinka muna shaida mazanmu da mata." "[11]

A nan 'Yanmedi yana yabon shugaban qasa Umaru Musa yar'adua dangane da kyawawan halayensa na qwarai ta yadda har ya kwatanta shi da halayen Sardauna da Aminu Kano a matsayinsu na 'yan kishin qasa. Don haka yana yabon 'Yar'adua ne kan manufofinsa na alkhairi.

Haka ma Muhammadu Xan Musa ya yabi jam'iyar A.P.P a baiti na 36, inda yake cewa:

36. "*Mutan Kano kun sami madafa,*
Tun da kun xauki Umar Tofa,
Baba da ma ka sai min besfa,
Don ina waqar talakawa."
(Xangulbi, 2003:136).

A nan yana yabon kanawa saboda zaven Umar Tofa halin qwarai da taimakon jama'a. wato ba su yi zaven tumun-dare ba.

Ta haka ne dai masu shirya waqoqin siyasa suke tallata jam'iyya ko mutanen cikinta ta fuskar yabon asali ko mulki ko kyauta da kuma halaye na qwarai, domin a zave su ko a ba su goyon baya a jagorancinsu.

2.7.3 Jigon Habaici

[11] An samu waqar a kaset

Habaici wani zance ne na hikima da Hausawa suke amfani da shi domin faxakar da al'umma game da wasu miyagun halaye na wani. Xangambo (2008:72), ya bayyana habaici da cewa:

> "*Habaici, magana ce mai voyayyiyar manufa. A kan yi magana da niyyar nufin wani abu ga wanda aka yi maganar dominsa."*

Wato Habaici hanya ce da ake zagin mutum a fakaice ta bayyana wasu miyagun halayensa. Haka kuma ana amfani da shi don zagin wata qunigya ta wasu mutane da suka kasance cikin wani mugun hali. (Xangulbi, 2003:147).

Don haka ana iya bayyana habaici da cewar wata maganar hikima ce da ake bayyana wasu miyagun halaye na mutum ko wata qungiya da nufin faxakar da shi cewar al'umma ta farga da halin da yake ciki. A cikin habaici ana amfani da wasu kalmomi ko siffofi, waxanda da an ji su, za a iya fahimtar da wanda ake. Sai dai, ba lallai ne a fahimci hakan ba, sai idan an san wani abu daga cikin dalilin yin maganar. Kasancewar waqa qunshe take da hikima da sarrafa harshe, za a iya samun habaici a cikin waqoqi don nuna qwarewa a cikin harshe.

Haka ma cikin waqoqin siyasa ana samun jigogin habaici domin bayyana wasu miyagun halaye na abokan hamayya ko kuma domin muzgunawa ko vata masu suna ta yadda jama'a za su qyamaci 'yan wannan jam'iyyar su kuma qi zaven su. Waqoqin siyasa cike suke danqam da habaice-habaice da ake yi wa abokan hamayya. Misali a cikin waqarsa "*Nijeriya Sai Mai Gaskiya*." Ibrahim Hayin Banki a baiti na 13, yana cewa:

13. *"Wanda ya ja da kai Buhari zai sha wuya,*
Domin ka fì wane mai halin 'yan giya,
Mai huska kamar ana murjin taliya,
Kai hango shi ba ya qaunar Nijeriya."

A wannan baiti, ga alama, ana ganin cewar habaici ne ga abokin hamayyar Muhammadu Buhari. Haka ma, Shafi'I Zakari 'Yanmedi, a waqarsa "*Tarayya Muke Magana: Manufofin Gwamnatin Mutawalle*," ya yi amfani da habaici inda ya ce:

"Wai kashi a moxa ko haka ne tsabtar biri ke nan,
Mai shelar a dole a bai wa arewa shugabncin nan,
Yau ga xan arewan mun zava ya xau adawar nan,
Qarshen hassada da nufin Allah kunya mazanmu da mata."

A nan ya nuna cewar hassadar da 'yan kudu ke yi ta ganin 'yan arewa ba su hau shugabancin qasa nan ba, to yau ga shi Allah ya nufa Umaru Musa ya zama shugaban qasa, don haka sun ji kunya. Haka dai ake samun habaici a waqoqin siyasa da ake bayyana wasu halaye miyagu na abokan hamayya da nufin goga masu kashin kaji.

2.7.4 Jigon Talla

Duk wani abu da mutum yake da shi da yake so mutane su so shi, ko ya samu karvuwa gare su, lallai ne ya yi amfani da hikima don tallata shi. A kan haka ne ake amfani da duk wata hanyar hikimar magana da jawo hankali don gamsar da mutane ga abin nan da ake son tallatawa. A cikin talla ne ake koxa abu ko a zuguguta shi da kwarzanta shi ta yadda jama'a za su ji suna ra'ayin wannan abu. Haka ma kuma a jam'iyyance akan tallata jam'iyya ko xan takara ko kuma shugabannin wata jam'iyya da nufin nusar da jama'a su so wannan jam'iyyar ko xan takara.

Saboda haka, ana samu sau da yawa masu shirya waqoqin siyasa su tsara waqoqi domin cusa wa mutane son wata jam'iyya ko wani xan takara. Kasancewar duk lokacin da mai talla yake tallarsa, yana amfani da hanyoyi daban-dabam na jawo hankali, to ta haka suke yabon jam'iyyar da suke tallatawa su fito da ita fili ga jama'a. sannan kuma su nuna cewa kada su zavi wata jam'iyya idan ba wannan ba. A cikin tallar suke nuna yadda jam'iyyar da ake tallatawa za ta ceto talakawa daga halin qaqa-ni-ka-yi da suke ciki, kuma su nuna zalunci da illar jam'iyyar abokan hamayya, musamman ta fuskar mulki da tattalin arziki da 'yanci da dai sauransu. Ana samun talla a dukan jam'iyyu da ake da su kamar P.D.P da C.P.C da ANPP da ACN da dai sauransu domin jama'ar qasa su rungumi jam'iyyar da ake son xagawa a san ta. Ga qaxan daga cikin misalai na talla a waqoqin siyasa: Misali, Aqilu Aliyu a waqarsa *"Baqi Uku sharrin NPC*," (baiti na 2 – 3) yana cewa:

"Ku zo talakawa in ba mu, Abin da yake amfaninku,
Mazanku da mata taronku, Ku zavi sawaba ce taku,
Ku yada zalama NPC.

Haba jama'a ku qi zavarta, Saboda mu taru mu kashe ta,
Ta faxi da bayan bayanta, Mu yarada da NEPU mu zaveta,
Mu huta masifar NPC " (Kafin Hausa ,1983:34).

A nan Aqilu Aliyu yana tallata jam'iyyar NEPU domin talakawa gaba xayansu maza da mata su zave ta, saboda ita ce za ta amfane su. Don haka su yi watsi da jam'iyyar NPC azzaluma.

Haka ma a waqar *"Inuwar Sawaba*." A baiti na 5 da na 7, aqilu Aliyu yana cewa:

5. “*Fa mu ‘yan arewa mu lura mu gane,*
Mu zazzage dantse mu nemo sawaba,
Mu tashi mu miqe kamar za mu yaqi,
7. Mu bayar da rayi mu fanso sawaba.
Mu tashi da niyya da qarfi da himma,
Mu taru mu xaru a birnin sawaba.”
(Kafin Hausa (1983:12)

Aqilu Aliyu a nan yana so ya faxakar da mutane su yi tururuwa cikin jam’iyyar NEPU. Yana nuna masu cewar fa su yi da gaske bakin-rai, bakin-fama wajen samo fansa da ‘yanci a jam’iyyar.

Haka Auwalu Isa Banguxu a waqarsa “Waqar Fi’arfi Maganin Zamba,” yana tallata jam’iyyar misali inda yake cewa (a cikin baiti na 1 – 2 da na 4):

1.“ *Jama’a ku tsaya ku saurara,*
Ku ji zance na ku ko lura,
Magana ce za ni tsatssara,
Kowanku ya bi ni ba tara,
Daga yaro har zuwa babba

2. Ita fi’arfi muradinta,
Ta ga ta hana dukkanin cuta,
Tai adalci a mulkinta,
Talawaka du su huhhuta.
Ba ta bar kowa zalama ba.

4. Mu bi fi’arfi mu bar wasa,
Kowa zai sami ‘yancinsa,
A riqe shi a ba shi hakkinsa,
Daga shi har ma iyalinsa,
Ba za su zaman talauci ba (Birniwa, 1987:446).

A nan idan aka lura, Auwalu Bunguxu yana tallata jam'iyyar P.R.P ne a faifai ga jama'a domin kuwa, yana jawo hankalinsu ne da faxakar da su cewar ita jam'iyyar P.R.P burinta shi ne ta ga ta hana yin zalunci, kuma ta tsai da adalci a cikin mulkinta ta yadda kowa zai huta. A kuma ba kowane talaka yancinsa da haqqinsa da na iyalinsa gaba xaya. Sun kuma rabu da talauci ke nan.

Sannan kuma har wa yau, Auwalu Isa Bunguxu cikin waqarsa ta jam'iyyar SDP, *"Waqar SDP Nasiha*", yana tallata jam'iyyar ne da kuma nuna kyawawan manufofinta. Misali yana cewa tun a farkon waqar ya fara da amshinta.

"*SDP Nasihar qasarmu muna maraba"*

Tun a nan ya gabatar da jam'iyyar ne ga al'ummar qasa su marabce ta, su karve ta hannu bibbiyu. Sannan a cikin waxannan baitoci yana cewa:

"*SDP Nasiha fiyayyar jam'iyya ce,*
Jam'iyyarmu mai son a taimaki al'uma ce,
Duk mutumen da ya xau Nasiha ya yi dace,
Wasu sun xauki shaho a yau ya bar su kwance,
Ba zai masu fa'ida ba. X 2

Za ta tsaya ta inganta asibiti da makarantu,
Don yaranmu sui qoqari ciki sui karatu,
Kuma su qware da ilimin karatu ko rubutu,
Za a tsaya a koyar da su sai sun fahimtu,
Ba za sui bargada ba.

Za mu tsaya mu inganta tarbiyya ga yara,
Don mu ga sun zamo haziqai kuma masu qwazo,
Sui ladabi da xa'a da alkunya da kara X2

Su ka riqe qasar nan watan wata ran a mora"[12]

A nan idan aka lura za a ga cewar Malam Auwalu Isa Bunguxu yana nuna wa talakawa cewar matuqar suka zavi jam'iyyar SDP ta kafa gwamnati, to za ta taimaki al'ummar qasa ta yadda za ta kula da haqqin karatun 'ya'yansu. Za ta tsaya tsayin-daka ta ga cewar ta inganta asibitoci da makarantu a sami ilimi da qwarewa, kuma za a inganta tarbiyyar yara kasancewarsu manyan gobe. Duk waxannan, yana wayar da kan talakawa ne game da qudurori da manufofin jam'iyyar SDP na inganta rayuwar talaka.

A qarshe dai za a fahimci cewar ana tallata jam'iyyar da 'ya'yansu dangane da kyawawan manufofi da qudurorinsu ga jam'iar qasa idan aka zave su, suka xare a kan gadon mulki. Ta haka ne ake jawo ra'ayin mutane su shiga jam'iyya su yi mata aiki don a zave ta a mori waxannan qudurori da take da su ga talakawa.

2.8.0 Salo a Cikin Waqoqin Siyasa

Salo kamar yadda yake zuwa a cikin ayyukan fasihai ko ma a maganganun yau da kullum, abu ne muhimmi da yake fito da saqo a sarari ga jama'a, ta hanyar wata dabara ko hikimar magana. Don haka ne ma ake samun salailai iri-iri cikin waqoqin siyasa domin yin kwalliya da adon magana wajen isar da saqonninsu. Masana daban-daban sun bayyana ma'anar salo. Misali. Yahaya (2001:3) ya bayyana salo da cewar:

[12] An samu waqar a kaset

> "*Salo yana nufin duk wata dabara ko hanya a cikin waqa wadda aka bi domin isar da saqo. Ita wannan dabara ko hanya tana yi wa waqa kwalliya ta yadda saqon waqar zai isa ga mai saurare ko karatun waqar*."

Shi kuwa Xangambo (2008:34) ya bayyana cewar"

> "*Salo wani yanayi ne da ya qunshi zavi a cikin rubutu ko furuci*."

A taqaice dai, a iya cewa salo kwalliyar magana ce da ake isar da saqo a hikimance. Don haka, za a lura da cewar ana amfani da salo daban-dabam a cikin waqoqin siyasa ta hanyar sarrafa harshe cikin hikima domin isar da saqo. Saboda da haka, a iya cewa salo tamkar magi da gishiri ne a cikin miya. Wato kamar yadda suke gyara ta (miya) ta ba da xanxano mai daxi, haka ma salo yake gyara waqa. Saboda haka salo wani babban abu ne a cikin waqa da yake qara mata qima.

2.8.1 Kwalliya

Kwalliya tana daga cikin nau'o'in sarrafa harshe da ake amfani da su a cikin waqa. Haka ma ana samun sa a cikin waqoqin siyasa domin bayyana wata jam'iyya ko mutum ta yadda jama'a za su fahimce shi. Akwai ma'anoni da dama ta bakin masana. Misali:

Yahaya (2001:59) ya ce:

> *"Salon siffantawa faffaxan salo ne da ya tara surori ko siffofin da mawaqi ya bayyana abu; salo ne da ake kawo hoton abu yadda mawaqi ke buqatar mai karatu ko sauraren waqarsa ya kalle shi da idon zuciyarsa ko tunainsa, salon siffantawa hoto ne da kalmomi suka kawo da ma'anoninsa".*

Shi kuwa Xangambo (2008:39) ya bayyana siffantawa da cewa kwatance ne na kai tsaye, wanda a yayin kwatancen akan xauki darajar wani abu ko halayyarsa, a xora wa wani kai tsaye. Ya bayyana wasu daga cikin hanyoyin siffantawa inda akan yi amfani da kalmomi irin su "shi ne" ko a ce "kaza" ko "kaza kaza ne." Ya ba da misalin yadda Aqilu Aliyu ya siffanta "ilimi" da wata babbar inuwa a waqar "*Kadaura*" inda ya ce:

"*Shi ne kadaura ilmu babbar gayya".*

Wato dai ke nan, za a iya cewa siffantawa salo ne a cikin waqa da ake suranta abu cikin kalmomi domin a ga hotonsa a zuciya domin a fayyace shi qarara. Ga misalin siffantawa a cikin waqoqin siyasa: Nazifi Asnanic a waqarsa ta PDP ta "Kwankwaso Dawo-Dawo" yana cewa:

"*Sawun giwa vadda na raqumi kwankwaso,*
Vauna mai tafiyar qasaita sai kwankwaso,
Bijimi namijin fama sai Rabi'u kwankwaso,
Wani kaya sai amale ke xauka kwankwaso,
Gamji sha sassaqa kake Rabi'u kwankwaso,
Qwarya kin zarce qetara Rabi'u kwankwaso,
Gugan qarfe garnaqaqi Rabi'u kwankwaso."
(Abbas, 2011:8).

A nan mawaqin ya yi amfani da salon siffantawa domin ya nuna matuqar shahara da kwarjinin gwaninsa. Domin kuwa ya siffanta shi da wasu dabbobi da suke sun kai matuqa ga shahara a qarfi da kwarjini. Misali, ya kamanta shi da giwa da vauna a cikin dabbobin dawa, haka kuma bijimin sa da amale a dabbobin gida waxanda suka shahara a fagen

qarfi da kwarjini. Haka ma ya abuntar da shi ta kamanta shi da qwarya da guga da kuma gamji.

Don haka, abin fahimta a nan, shi ne ana samun siffantawa a cikin waqoqin siyasa inda ake amfani da adon harshe domin siffanta wani ko wata jam'iyya a kambama shi ta hanyar nuna kwarjininsa da kuma shahararsa a fagen siyasa. Ta haka ne ake iya jan ra'ayin jama'a su zavi wannan mutume ko kuma jami'yya.

2.8.2 Tamka

Tamka dabara ce ta kamantawa a cikin waqa ta yadda ake kwatanta wasu abubuwa guda biyu ko fiye, masu halayya iri dabam. Akwai kwatantawa ta daidaito da ake amfani da kalmomi irin su: 'kamar' 'da awa' da 'ka ce' da 'tamkar' da sauransu. Akwai kuma kwatantawa ta fifiko da ake amfani da kalmomi irin su: 'wane' da 'ya zarce' da sauransu. Akwai kuma kwatance na nuna gazawa inda akan yi amfani da kalmomin korewa. Misali: "bai kai ba". (Dangambo, 2008:39).

Ke nan, a iya cewa ana amfani da kamantawa ne a cikin waqa domin yin kamancen wasu abubuwa da nufin kwatanta su a fito da matsayin wani ko wani abu ga jama'a. ta haka ne jama'a za su fahimci cewa ashe "ruwa ba tsaran Kwando ba ne," ta yin la'akari da fifiko ko gazawar wani a kan wani.

To, haka ma a cikin waqoqin siyasa ake samun wannan nau'i na adon harshe da nufin nuna fifikon wani ko wata jam'iyya, ko kuma kasawar wata jam'iyya ko wani a cikin

siyasa. Domin ta haka ne jama'a za su yi wa kansu qiyamul-laili, su zavi na zave, su yarvar da na yadawa. Ga misalin wannan kamance kamar yadda yakan zo a cikin waqoqin siyasa.

2.8.2.1 Tamkar Fifiko

Misali, Malam Muhammadu Xan Musa a waqarsa ta jam'iyyar A.P.P yana cewa:

"Tun da zakanya tai qara,
Ba ni shakkar ta murguxe kura,
Naja'atu zo ki yi mana gyara,
Nan Kano sai maixankwali." (Xangulbi, 2003:170)

A nan an kamanta Naja'atu da zakanya inda aka nuna fifikon cancatarta a kan abokan takararta, waxanda aka kwatanta su da kura wadda ba ta kai qarfin zakanya ba. An yi haka ne domin a yi qoqarin gamsar da jama'a su zavi Naja'atu domin ita take da qarfin qwato masu haqinsu, don haka ita ta fi cancanta a kan sauran 'yan takara. Haka ma Ibrahim Yala a waqarsa ta "C.P.C Taimako Ga Kowa" yana cewa:

"Mai alqalamin da kaifinsa ya wuce takobi" (Abbas, 2011:8).

Ya kwatanta kaifin alqalami da na takobi domin nuna fifikon jam'iyya mai alqalami.

2.8.2.2 Tamkar Kashi

A nan kamar bayani ya gabata, ana amfani da kalmomin korewa ne "ba....ba" domin nuna kasawar wani. A kan sami wannan saudayawa a cikin waqoqi domin kushe wani ko wani abu ta hanyar nuna gazawarsa. Don haka ne ma ake samun wannan a cikin waqoqin

siyasa kasancewar a cikinta akwai takara a tsakanin jam'iyyu ko kuma mutanen cikinsu. Misali, Aminu Ibrahim Xandago a waqarsa ta A.P.P yana cewa:

" *Shi kunun zaqi yai kaxan ya wa koko barazana,*
Xan akuya bai kama da giwa ba ta ko'ina,
Gorar ruwa ga buhun qarfe jinjina,
Kowa yal lashi garwashi zai xanxana,
Ba a shara da yatsa sai dole da tsintsiya".
(Xangulbi, 2003:172)

A nan ana kwatanta jam'iyyar A.P.P da sauran nuna gazawarsu. Domin an yi amfani da "koko" wanda ya fi "kunun zaqi". An kuma nuna gazawar xan akuya ga giwa a wajen qarfi da girma. Don haka yana nuna cewar sauran jam'iyyu da magoya bayansu, ba su kai na A.P.P ga kwarjini da kuma cancanta.

Saboda haka za a fahimci cewar ana amfani da kamance na gazawa domin kushe abokan hamayya da kuma jam'iyyunsu ta nuna gazawarsu ga iya mulki ko ma cancantarsu ga jagorancin jama'a. Sannan kuma an lura da cewar ana yin wannan kamace na kasawa ta amfani da duk wata kalma da ke nuna gazawa kamar: "bai yi kamar.... ba" ko "bai kai...ba" ko "ya yi kaxan" "ba ya kama da" "bai wuce... ba" da sauransu.

2.8.2.3 Tamkar Daidaito

A kamancen daidaito kamar yadda bayani ya gabata, ana amfani ne da kalmomi irin su: "kamar" da "awa" da "tamkar" da "ka ce" da sauransu domin kwatanta wasu abubuwa biyu ko fiye domin a nuna daidaito a matsayinsu. A iya cewa ana yin haka ne a cikin waqa domin nuna yadda muhimmancin abin ya kai matuqa. Don haka ne ma a cikin

waqoqin siyasa ake samun irin wannan kamance domin a nuna matsayin wata jam'iyya ko wani mutum da muhimmancinsa a cikin al'umma don a zave shi. Misali, Dauda Kahuta Rarara, a cikin waqarsa ta *"Deputy Gwamna"* ya ce:

" *Ka zamo kamar namijin goro gun iyaye,*
Dole ne a neme ka idan gari ya waye"
(Abbas, 2011: 8)

A nan mawaqin ya yi amfani da goro saboda ya nuna muhimmancin gwaninsa da kuma matuqar buqatarsa da ake yi a wajen harkokin gudanar da mulki. Domin kuwa a al'adar Bahaushe, goro wani abu ne muhimmi da yake dole a neme shi a wasu al'amura da dama, kamar baiko ko xaurin aure ko raxin suna da sauransu. Haka ma an kwatanta goro da iyaye. A nan yana nuna muhimmancin goro ga tsofaffi. Domin da zarar gari ya waye, abin da za su fara nema ke nan domin su xan tauna.

To, haka dai ake amfani da kamance na daidaito a cikin waqoqin siyasa domin nuna daidaituwar matsayin wani ko wasu a cikin jami'yya ko cikin al'umma bisa ga rawar da suke takawa a cikin jami'yya ko al'umma da rawar da nufin bunqasa rayuwar talakawa da kuma xaukaka darajar jam'iyyarsu.

2.8.3 Jinsintarwa

Wannan shi ma wani salo ne na kamantawa da mawaqa ke amfani da shi a cikin waqoqinsu. Don haka a cikin waqoqin siyasa ma, ana samun wannan salon. Xangambo (2008:41), ya bayyana jinsirtarwa da cewar wata dabara ce ta nuna yin kwatance ta fuskar jinsi, inda ake xaukar halayyar wani a ba wani jinsin dabam. Akwai salon jinsintarwa

guda biyar; mutuntarwa da dabbantarwa da abuntarwa da abuntarwar abuntarwa da kuma alamantarwa.

2.8.3.1 Mutuntarwa

Wannan dabara ce ta xaukar darajar mutum a xora wa dabba ko wani abu. Wato dai duk wasu xabi'u da aka san mutum da su, sai a ba wanda ba mutum ba a ce ya yi su. Misali, Muhammadu Xan Musa a cikin waqarsa ta A.P.P yana cewa:

" *Jan biri na gane nufinka,*
Da ca nake mai son jama'a ne,
Ashe kiranka kiran jama'a ne,
Ja'irin aka ba ka ministà,
Sai ka karvi ka mance na baya."
(Xangulbi, 2003:180)

A wannan baiti mawaqin ya yi amfani da salon mutuntarwa inda ya xauki darajar mutum wanda shi ne aka sani da yin magana ya xora wa biri. Sannan kuma da xabi'ar mutum, inda akan samu wasu idan sun sami shugabanci, sai su manta da waxanda suke tare da su. Haka ma Shu'abu Zakari Yarmedi a waqarsa ta P.D.P yana cewa:

"*Vauna saniyar sake mai 'yar laya ba ya nuna ki,*
Balle ma yay tunanin kamawa tilas ya qyale ki,
Tauraro Turakin Adama ya zan abin xoki,
Ga Bamanga ga Atiku kwashe kayanka xan jaki P.D.P akwai
Jibril Farfesa masu gyara qasata."

A nan ma za a lura cewar 'Yarmedi ya yi amfani da salon mutuntarwa domin nuna qasqanci da dakushe darajar abokan hamayya na su Atiku na jami'iyyar PDP. Ya mutuntar da jaki wanda jinsi ne na dabba, inda ya nuna yana halayya ko aikin da mutum

ne kawai aka san shi da ita, wato kwashe kaya. Domin an san jaki ba shi da hannuwa balle ya kwashe wani abu.

Haka kuma, Aqilu Aliyu a cikin waqarsa, "Baqi Uku Sharrin N.P.C." (baiti na 5 da na 6) inda ya ce:

"Kashedi fa kadda ku zave ta, saboda mutuntar halinta,
Da munanan xabi'o'inta, Tsaya ka ji mugun halinta,
Mu ce Allah tsine NPC.
Halinta tsiya da munafunci, Da qin jama'a da walaqanci,
Da karya mutum mai adalci, Da haddace kundin zalunci,
Waxannan su ne NPC." (Kafin Hausa, 1983: 34)

A nan an mutuntar da jam'iyyar N.P.C inda aka bayyana halayenta da mai mugunta da wulaqanci da munafunci da zalunci da dai sauransu, wanda duka halaye ne da xan Adam aka sani da su. Idan aka lura, za a ga cewar ya yi amfani da wannan salon ne domin ya vata ita kanta jam'iyyar da kuma mutanen cikinta don kada jama'a su zave ta.

Saboda haka, idan aka lura, za a ga cewar mawaqa kan yi amfani da kamancen jinsirtarwa, a mutuntar da wani abu domin kushe abokan hamayya ko dakushe darajarsu, a fifita wasu da ake ba goyon baya a cikin waqa.

2.8.3.2 Dabbantarwa

Wannan dabara ce da ake xaukar wata halayya ko xabi'a ta dabba a xora wa mutum ita. Mawaqa sukan yi haka ne domin kwarzanta wani ko wata jam'iyya, ko kuma su qasqantar da jam'iyyar adawa ko abokan hamayya da nufin cin fuska ko munana masa. Misali:

Har wa yau dai, Shu'aibu Yarmedi a waqarsa ta P.D.P a baiti na xaya yana cewa:

> "*Vauna saniyar sake mai 'yar laya ba ya nuna ki, Balle yay tunanin kamawa tilas ya qyale ki,*
> *Tauraro Turakin Adamawa y azan abin xoki,*
> *Ga Bamanga ga Atiku kwashe kayanka xan jaki,*
> *P.D.P akwai Jibril Farfesa masu gayara qasata."*

'Yarmedi a nan ya yi amfani da salon dabbantarwa ya kamanta Turakin Adamawa da Vauna, kuma ya abuntar da shi a matsayin tauraro tauraro domin ya kambama shi, ya kuma nuna shahararsa yadda ya gagari kowa. Kuma yana nuna cewar mutum sai ma isa ya tunkare shi ko ya zo kusa da shi ba kamar yadda ba za a iya tunkarar vauna a kama ta cikin sauqin ba. Haka kuma ya yi amfani da tauraro domin nuna yadda yake haskawa, ya yi zara a cikin al'umma.

Haka ma Mudi Sipikin (1971:58) a waqarsa mai suna: "*Nasiha ga 'yan siyasa*" ya yi amfani da salon dabbantarwa inda ya ce:

> "*Mun sanya haja ta mujiya,*
> *Don mu tsinkayi gaskiya,*
> *Ba nifaqa kaza riya,*
> *Allah tsare mu da tankiya,*
> *Kaza da aikin ma'asiya"*

A nan mawaqin ya yi amfani da wata sifa ta mujiya, wadda an san ta da manyamanyan idanu. Ya danganta wannan sifa ga mutane domin jawo hankalinsu da idanunsu qwala-qwala, domin su ga gaskiya, su aikata, kuma su bi ta.

2.8.3.3 Abuntarwa

Abuntarwa wani salo ne cikin waqa da mawaqa ke bai wa mutum ko wani abu daraja ko xabi'a ta wani abu maras rai wanda ba ya cikin mutane kuma shi ba dabba ba. A irin wannan salo, mawaqan siyasa su ma ba a bar su a baya ba. Don haka sukan yi amfani da shi a cikin waqoqinsu domin bayyana wata manufarsu. Misali: Aqilu Aliyu a waqarsa, "Inuwar Sawaba" ya yi amfani da irin wannan salo a baiti na 10 da na 12, inda ya ce:

"*Ganinmu da jinmu zamanmu da tashi,*
Wuninmu da kwana mu nemo sawaba,
Manoma, fatake da 'yan kasuwarmu,
Mu xau garkuwa don mu qwato sawaba."
Kafin Hausa (1983:13)

A cikin waxannan baituka mawaqin ya abuntar da jam'iyyar NEPU, inda ya nuna ta a matsayin wani abu ne da za a iya nemowa, har a kama shi, kuma a qwato. Manufarsa a nan, ita ce jam'iyyar NEPU ita ce 'yancin talakawa. Don haka, dare da rana kowa-da-kowa ya duqufa wajen nemo shi a kuma qwato shi daga azzalumai, wato 'yan jam'iyyar adawa. Idan an yi haka ne, kowa zai sami wadata da walwala a cikin shugabancin 'yan NEPU.

2.8.4 Aron Kalmomi

Shi ma wannan salo ne da mawaqa ke amfani da shi. Mawaqa, ciki har da na siyasa sukan aro wasu kalmomi daga wani harshe domin su burge jama'a (Xangulbi, 2003:191). Aqilu Aliyu a waqarsa ta "*Jiya da Yau*," baiti na 9, ya yi amfani da wannan salon inda ya ce:

9. *"Borno "yus" NEPU "alayans,"*
Yarwa "Nos" har Yarwa "sawus,"
Mu muke magana a "Hawus",

Babu shakka babu qarya."

(Kafin Hausa,1983: 7)

A nan Aqilu Aliyu ya yi amfani da aron kalmomi daga Ingiilshi. Kalmomin da ya yi amfani da su, su ne: yus (youth) – matasa

Alayans (alliance) – gamayya

Nos (North) – arewa

Sawus (South) – kudu

Hawus (House) – majalisa

Mawaqin yana nuna yadda Yarwa ta kudu da ta arewa suka haxe kansu, don a majalissa suke da rinjaye. Sai abin da suka ce shi za a yi. A wasu lokuta mawaqa sukan yi haka ne domin nuna qwarewarsu ko burgewa a cikin harshe. Sannan kuma ta haka ne suke fito da saqonsu cikin sauqi ta yadda za su burge mai saurare.

Haka ma a baiti na 49 a waqar "*Jiya da Yau"* ta Aqilu ya yi amfani da salon aron kalmomi inda ya ce:

"*Da kana wata farfangada,*
Wai ka ce kai indifenda,
Yanzu ta ruva ta yi bindi,
Mun gane ka ka daina vuya."
(Kafin Hausa, 1983:12)

A nan ma Aqilu ya yo aron kalmomi daga Turawan Ingilish inda ya yi amfani da farfaganda (Propaganda) da kuma indifenda (Independent). Manufarsu ita ce an gano

wanda yake ta yaxa maganganu da qarairayi cewa ya tsaya da qafarsa, to ta tonu qarya ce yake yi.

A nan za a fahimci cewa mawaqa siyasa kan yi amfani da salon aron kalmomi domin qawata waqoqinsu ko kuma bayyana wata manufarsu. Wannan aro ba daga Turanci ne kawai suke yin sa ba. A'a har ma daga wasu harsuna kamar su Larabci da Fulatanci da Barbarci da dai sauransu.

2.8.5 Karin Magana

Shi ma wannan salo ne na sarrafa harshe da nuna qwarewa da naqaltar harshe. Mawaqa suna amfani da wannan salo don burgewa ko qawata waqoqinsu domin bayyana wata manufa. Karin magana dabara ce ta dunqule magana mai yawa a cikin zance ko 'yan kalmomi kaxan cikin hikima (Xangambo, 2008:67). Mawaqa siyasa kan yi amfani da karin magana a wasu lokuta domin su yi wa abokan hamayya habaici ko kuma su kushe su, ko su qasqantar da darajarsu dangane da yadda suke takara a tsakaninsu. A wasu lokuta kuma mawaqa kan yi amfani da karin magana ne domin yin gargaix ko hannunka maisanda ga jama'a dangane da wani al'amari da suke so a lura da shi. Ta nan ne jama'a za su tantance tsakanin aya da tsakuwa domin su zavi na zave. A nan a iya cewa karin magana a cikin waqoqi ciki har da na siyasa, abu ne da ya mamaye su. Don haka, ana

samun karin maganganu bi-la-adadin a cikin waqoqin siyasa. Misali: Dauda Kahuta Rarara a cikin waqarsa, "Sauran Qiris Deputy", ya ce:

"*Duk kuricyar da ba ta da gashi,*
Ku kira ta 'ya kawai 'yan amshi"[13]

A nan idan an lura, za a fahimci cewar Kahutu Rarara ya yi amfani da karin maganar da Hausawa ke cewa "*Duk kurciyar da ba ta da gashi, xiya ce"* domin yin habaici ga abokan hammayar gwaninsa, wato Abdullahi Gwarzo. Domin ya nuna masu cewa ba su isa komai ba. Ke nan yana nuna muhimmancin Ubangidansa, da kuma nuna gazawar 'yan adawa.

Haka ma Aqilu Aliyu a cikin waqarsa, "Jiya Da Yau," a baiti na 41, ya yi amfani da karin magana inda ya ce:

"Kai varin kaya da farko,
Yanzu sun maishe ka soko,
Babu tsuntsu babu tarko,
Ga sa gaba babu baya."

(Kafin Hausa, 1983:11)

Aqilu Aliyu ya yi amfani da karin maganar da Hausawa ke cewa "*Ka yi vatan vakatantan, ba ka ga tsuntsu ba ka ga tarko"* domin yin habaici ga wani xan takawa na jam'iyyar adawa. Sannan kuma ya faxakar da jama'a cewa wannan xan takara fa ya saki reshe ya kama ganye, wato ya yi biyu babu ke nan. Ba shi ga takarar, ba shi ga mulk,i kuma jama'a yanzu sun ga gazawarsa. Saboda haka ba su mai da shi bakin komai ba.

[13] An samu waqar a kaset

Haka kuma Aqilu Aliyu a waqarsa ta “Inuwar Sawaba” ya yi amfani da karin magana inda ya ce (baiti na 42):

“Akwai albasata da nib barta baya,
Cikin wagga tuya ta wainar sawaba”

A nan Aqilu ya yi amfani da karin maganar nan da ake cewa, “An yi tuya, an manta da albasa.” Wannan karin maganar tana nuni ne ga wani muhimmin abu wanda saboda muhimmancinsa, bai kamata a ce an manta da shi ba. Kamar dai yadda idan za a toya mai sai an sa albasa domin ya qara ba da qanshi da daxin xanxano. A cikin wannan karin maganar, mawaqin yana so ne ya nuna mana cewar akwai wani mutum muhimmi a cikin jam’iyyar NEPU da ya bari, wanda kuma bai kamata a ce ya manta da shi ba. Wannan mutumen, shi ne Abubakar Barnawayi, kamar yadda ya ambata a baiti na gaba (na 43) inda ya ce:

“Fa shi ne Abubakari; Barnawayi,
Fa miskinu ya taimaka wa sawaba,”
(Kafin Hausa ,1983:15).

2.9 Naxewa

Wannan babi ya qunshi gabatarwa da dalilin bincike da waiwayen ayyukan da suka gabata. Haka kuma an duba taqaitaccen tarihin samuwar siyasa da waqoqinta. An duba ma’anar siyasa da ire-irenta da kuma irin dalilan da suka haifar da sabon salo a waqoqin siyasa na jamhuriya ta huxu (4). Mai bincike ya xauki wannan batu ne domin cike givi da kuma fito da sabon salon waqoqin siyasa da aka samu tare da taskace wasu daga cikinsu don amfanin gaba. Kamar yadda aka san waqoqin siyasa na zamunan da suka gabata

musamman, jamhuriya ta xaya da ta biyu, sun fi mayar da hankali ne ko karkata ga yaxa manufofin jam'iyyun da kushe abokan hamayya da jam'iyyunsu. To, amma a wannan zamanin siyasa, saboda wasu dalilai da ake so a gano nan gaba cikin wannan bincike, ya sa salon waqoqin ya sauya. Ire-iren waqoqin da a yanzu, mafi yawa 'yan takara ne suke tallatawa maimakon a ce sun duqufa kan wayar da kan jama'a game da nanufofinsu da abubuwan da za su yi wa al'umma idan sun kafa gwamnati. Ke nan mafi yawa waqoqin, suna tallata hajojin jam'iyyun siyasa ne, maimakon yaxa manufofinsu.

Sannan kuma an duba salo da yadda ya kasancewa a cikin waqoqin siyasa. Kamar yadda bayanai suka gabata na yadda masana suka bayyana salo, yana da kyau a fahimci cewa salo a cikin waqa abu ne da yake tamkar gishiri da magi a cikin miya da yake gyara ta, ta yi zaqi zaqwai. Haka ma salo yake inganta waqa, ta kuma isar da saqonta cikin armashi da burgewa.

Haka kuma an ga cewar salo ya qunshi yadda mawaqi yake amfani da harshensa ya sassarqa tunaninsa cikin hikima da nuna qwarewarsa a harshe. Waxannan hikimomi ko dabaru sun haxa da siffantawa da aron kalmomi da karin magana da jinsirtarwa da dai sauransu. Duka, waxannan hanyoyi ne da mawaqi ke amfani da su ya dunqule wata magana cikin hikima domin isar da wani saqo.

Haka ma an ga cewar su ma mawaqan siyasa suna jejjefa waxannan salailai a cikin waqoqinsu a gavovin da suka dace. Suna yin haka ne domin nuna qwarewa ga harshen da kuma qoqarin faxakar da mutane wani abu da ba su fahimta ba dangane da jam'iyyun

siyasa da kuma mutanen cikinsu. A cikin waqoqin ne, ta hikima suke kushe abokan gaba, su kuma xaukaka martabar waxanda suke mara wa baya. Sukan yi amfani da zambo da habaici da zuga da kirari a matsayin kayan cikin waqoqinsu da suke yabon jam'iyyu ko kushe abokan hamayya.

BABI NA UKU:

SHARHI A KAN WASU WAQOQIN SIYASAR JAMHURIYYA TA HUXU

3.0 Gabatarwa

A wannan babi za a yi nazarin wasu zavavvun waqoqin siyasar Jamhuriya ta huxu. Za a duba waxannan waqoqi ta fuskar jigonsu da salo da kuma tsari. An xauki wasu waqoqi daga jam'iyyar PDP da ANPP da kuma CPC, kasancewarsu fitattu a qasar Hausa.

Waqoqin siyasa cike suke da hikimomi da fasaha wajen bayyana wasu manufofi da qudurorin jam'iyyun siyasa, da ma 'yan siyasar kan su. Sai dai kamar yadda aka gani a

babin da ya gabata, an sami sauyi a salon waxannan waqoqi a wannan jamhuriyya (ta huxu).

3.1 Sharhin Waqar " *Adon Gaskiya Ba Ya Vata* ," ta Alhaji Ibrahim Aminu Xandago wadda ya yi wa Alhaji Aliyu Magatakarda Wamakko

3.1.1 Tarihin Alhaji Ibrahim Aminu Xandago

Alhaji Ibrahim Aminu Xandago an haife shi a (1964) a qwaryar birnin Kano (Kano Municipal) a unguwar Marmara. Kamar yadda al'adar Hausawa, shi ma Ibrahim Xandago ya fara da karatun allo na Islamiyya da ilimin littattafan addini. Ya shiga makarantar firamare a 1973. Ya fara karatun firamare a Xandago, daga baya, ya koma Gwale a inda ya gama a 1979. Daga nan ya wuce makarantar Sakandare ta Ringim a 1979, amma ya dawo Gwammaja inda ya gama sakandare a 1983. Bayan kammala sakandare ya xan tava kasuwanci tsawon shekara biyu. Da ya bar kasuwancin ya wuce kwalejin zurfafa ilimi ta Horon Malamai ta Gumel (Advanced Teachers College), inda ya samu takardar shaidar koyarwa ta qasa (NCE) a 1989. Daga nan ya xan tava koyarwa ta wani xan lokaci a Shehu AbdulWahab Special Primary School, Gwarzo, amma daga baya ya bari ya shiga harkokin siyasa. A shekarar 1999 Xandago ya koma Sakkwato saboda harkokin siyasa. Sannan kuma, har zuwa yau, yana shirya waqoqin siyasa da kuma rera su a jahohin Sakkwato da Zamfara.

Dangane da lokacin fara harkar waqa kuwa, tun yana qaraminsa ne ya tashi da hazaqar shirya waqa, kuma sha'awa ce da yake da ita a kan waqa ta sa shi tsunduma cikin harkar

tun yana makarantar firamare. Da farko ya fara da waqoqin yabon Annabi, kafin ya shiga shirya waqoqin siyasa. Duka baiwar da Allah ya ba Xandago yana fara rubuta waqoqinsa kafin ya rera su. Wato ke nan duka waqoqinsa rubutattu ne. Waqar farko ta siyasa da ya fara yi, ita ce wadda ya yi wa Injiniya Magaji Abdullahi Tatarawa a qarqashin Jam'iyya mai doki (S.D.P), wato lokacin Jamhuriya ta uku ke nan. Wannan waqar sunanta "Injiniya Allah ya ba ka ka yi mulkin Kano". Wannan fasihi dai, ya rubuta waqoqin siyasa da dama. Haka kuma yakan xan yi waqoqi a kan aure da sarauta da kuma yabon Annabi.

Dangane da waqar da aka nazarta kuwa, wato "Adon Gaskiya Ba Ya Vata". Ya yi wa Alhaji Yala Magatakarda Wamakko ne a 2006. a lokacin Magatakarda yana cikin Jam'iyyar ANPP, amma daga baya ya bar ta, ya koma Jam'iyyar PDP wadda a qarqashinta ya yi takarar gwamnan Jihar Sakkwato a 2007. Wannan waqar gaba xaya, da ita aka yi wa Yala Magatarkada Wamakko yaqin neman zave a qarqashin PDP. Dangane da dalilin wallafa wannan waqar ya bayyana cewa matuqar qauna ce da soyayya da ke tsakaninsa da Yala Magatakarda, ita ta sa ya yi masa wannan waqar domin ya xaga shi duniya ta san shi, a kuma zave shi. Haka kuma ita wannan waqar, ita ce bakandamiyarsa, domin ita ce ta fito da sunansa Jama'a suka san shi.

Alhaji Ibrahim Aminu Xandago, kamar yadda duk mutum cikarsa, ita ce ya kasance da iyali. Haka shi ma yana da aure, mata uku da 'ya'ya goma sha huxu da kuma jikoki biyar. Daga cikin 'ya'yan huxu maza; Abubakar da Bukar da Yusuf da kuma Aminu (wanda

suke wa laqabi da Alhaji, saboda sunansa Babansa). Duka iyalinsa suna zaune a Kano. Shi kuma yana zama a Sakkwato domin harkokin siyasa.

Game da ma'anar waqar siyasa kuwa, Xandago ya bayyana cewa ita ce wadda ta ginu a kan yadda mutum yake bayyanar da ra'ayinsa game da abin da yake so. Kuma tana qunsar habaici da zambo da kirari da zuga da shaguve da sauransu. Waxannan abubuwa da su ne ake kushe abokan hamayya da Jam'iyyunsa a kuma kwarzanta Jam'iyya ko xan takara, a tallata shi. Haka kuma Xandago ya bayyana cewar suna amfani ada amshi, domin shi ne gishiri a cikin waqa. Haka ma, kayan kixa na tasiri saboda ba da amo da zaqin waqa. Daxin-daxawa, suna amfani da kayan kixa na zamani saboda sun fi samun sauqi wajen rera waqa.[14]

Wannan waqa an yi wa Alhaji Aliyu Magatakarda Wammako ne, xan takarar gwamnan jihar Sakkwato a shekara ta 2007. Waqar tana da baitoci da amshi kamar haka:

Amshi:

Sakkwatawa suna bayanka,
Sarkin Yamma Allah saka ma.

3.1.2 Taqaitaccen Tarihin Jam'iyyar PDP

Wannan jam'iyya tana xaya daga cikin jam'iyyu tara da aka fara yi wa rijista a Jamhuriya ta huxu. Waxannan jam'iyyun kuwa su ne: AD da APP da DAM da MDJ da ita PDP da PRP da UDP da kuma UPP. An zuba waxannan jam'iyyu a matsayin zakarun gwajin dafin siyasar Jamhuriyya ta huxu. Bayan an gudanar da zaven Qananan Hukumomi a

[14] Hira da Alhaji Ibrahim Aminu Dandago Ranar Juma'a 21 ga Watan Fabrairu, 2014

Disamba 1998, sai aka xauki jam'iyyu uku rak daga cikin tara, aka ce su ne suka fi cancanta su zama jam'iyyu. Sai aka xauki AD da APP da kuma PDP (Daure, 2000:79) da (Umaru, 2003:31-32).

Wannan Jam'iyya ta PDP, ita ce ta mamaye harkokin shugabancin qasar tun daga kafuwar Jamhuriyar daga 1999 zuwa yau. Ba ta canza suna ba, kuma ba ta canza alamarta ba (ta lema). 'Yan Jam'iyyar ma na yi mata kirari da cewar ita ce jam'iyya mafi girma a Afirka, kuma suna iqirarin sai ta yi mulki tsawon shekara 60 (Jaridar Leadership, Juma'a 13 ga Disamba, 2013, shafi na 42).

Jam'iyya kamar yadda yake a al'ada takan fara da qungiyoyi da za su kafa ta. To, haka ma abin yake a Jam'iyyar PDP. Daga cikin qungiyoyin da suka kafa ta akwai K34 daga Katsina, wadda ta qunshi mutane irin su Marigayi Alhaji Umaru Musa 'Yar adua da Sanata Abdu 'Yandoma da Alhaji Shehu Inuwa Imam da dai sauransu jiga-jigan da suka kafa wannan Jam'iyyar sun haxa da Janaral Yala Gusau da Alhaji Sani Zangon Daura da Alhaji Iro Xan Musa da Alhaji Lawal Kaita da Alhaji Atiku Abubakar da Cif Tom Ikimi da Alhaji Abubakar Rimi (marigayi) da Alhaji Amadi Kurfi da Alhaji Yahaya Kwande da Cif Solomon Lar, wanda kuma shi ne shugabanta na farko da aka zave shi a babban taron jam'iyyar PDP da aka yi a Jos, Pilato a ranar 13 da 14 ga watan Fabrairu, 1999. Wannan Jam'iyyar tun da aka kafa wannan Jamhuriyya, ita ce ke da shugaban qasa. Ta yi shuwagabannin qasa guda uku; Janar Olusegun Obasanjo wanda ya yi mulki har sau biyu (1999-2003 da kuma 2003-2007) da marigayi Malam Umaru Musa 'Yar adua wanda ya

fara daga 2007, amma Allah bai qaddara ya gama mulkin ba ya rasu a watan Mayun 2010. sai mataimakinsa Gooddluck Ebele Jonathan ya qarasa zuwa 2011, wanda kuma yanzu haka, shi ne Shugaban Qasa daga zaven 2011 zuwa yau. Kaxan daga cikin manufofin Jam'iyyar PDP, sun haxa da:

(i) Gyaran qasa
(ii) Samar da tsaro ga qasa
(iii) Jin daxi da walwalar talakawa
(iv) Yin adalci ga 'yan qasa don samun cigaba
(v) Samar da kayan more rayuwa kamar su lantarki da ruwan sha mai tsabta da sauransu[15].

Sai dai, duk da kasancewar Jam'iyyar PDP mai mulkin qasa, a yanzu tana cikin hayaniya da rikice-rikice a tsakanin su kan su 'yan Jam'iyyar. Wannan ya fara ne inda ta kai har jam'iyyar ta dare gida biyu; da Sabuwa da Tsohuwa. Wannan rikici ne da ke faruwa da wasu gwamnoni biyar, waxanda daga sun fice daga Jam'iyyar zuwa Jam'iyyar APC a shekara ta 2013. Gwamnonin su ne: Murtala Nyako na Adamawa da Rotimi Amaechi na Rivers da Yala Magatakarda Wamakko na Sakkwato da Dr. Rabi'u Musa Kwankwaso na Kano da kuma Abdulfatah Ahmed na Jihar Kwara (Leadership, Juma'a 13 ga Disamba, shafi na 7). Haka ma an sami wasu Sanatoci 11 da suka koma APC (Leadership, Talata 4 ga Fabrairu, 2014 shafi na 5). Haka dai ake ta samun jiga-jigan jam'iyyar na ficewa saboda da iqirarin da suke cewa babu adalci da kuma maganar tsayawar Jonathan takara a

[15] Hira da Alhaji Mamman Magaji (Easy),wani Dattijo xan Jam'iyyar PDP, xan shekara sittin (60) a Qaramar Hukumar Mashi, Jihar Katsina, ranar Alhamis 20 ga Fabrairu, 2014.

2015 da maganar shugabancin Jam'iyyar na Bamanga Tukur da dai sauransu. Daga qarshe dai Bamanga ya sauka daga shugabancin Jam'iyyar 15 ga watan Janairu, 2014 a taron qasa da ta yi. Sakamakon haka aka zavi Alhaji Ahmed Adamu Mu'azu a matsayin Shugaban PDP, wanda shi ne shugabanta har zuwa yau.

3.1.3 Yadda Ake Tallata Xan Takara a Cikin Waqoqin Siyasa

Babu shakka, dangantakar mawaqa da 'yan siyasa ta jini da tsoka ce. Domin kuwa ba a raba su. Wato duk inda ka ga Zara, to za ka ga wata. Haka ma al'amarin yake tsakanin siyasa da kuma waqoqin siyasa. Dalili kuwa, shi ne cewar ita waqa ga 'yan siyasa da kuma siyasar tamkar gishiri ne a cikin miya, wanda idan babu shi, to ta zama lami. Wannan na nufin cewar waqoqi a wajen tallata Jam'iyyar siyasa da kuma 'yan takara. Saboda ita siyasa tana tafiya tare da farfaganda, wadda kuma mawaqan siyasa ke bayar da muhimmiyar gudunmuwa ta amfani da hikimominsu da kuma basirarsu a cikin waqoqinsu.

Masana da dama sun yi magana game da talla. Sun kuma bayyana cewa xan Adam na yin ta ne domin neman biyan buqatun rayuwa. Talla dai ana gudanar da ita ne ta yadda ake gabatar da abun sayarwa ga jama'a. Sannan kuma ana yin ta ne ta amfani da maganganun hikima da zaven lafuzza da kalmomi masu jawo hankalin mutum don ya sayi abin sayarwa. Har ma a kan yi amfani da karin magana da kirari da habaici da zambo da sauransu (Abdulmumini, 2009:168-169).

Dangane da salon da ake bi a tallata xan takara ma, abin haka yake. Domin kuwa an ji waqa daga bakin mai ita, a hira da aka yi da Alhaji Ibrahim Aminu Xandago. Ya bayyana cewa ana tallata Jam'iyya ko xan takara ta hanyar amfani da yabo da kirari da zuga da dai sauran dabaru domin a kwarzanta Jam'iyya ko xan takara a fito da kyawawan halayensa domin a zave shi. Sannan kuma, ana amfani da zambo da habaici da shaguve da sauransu domin a kushe Jam'iyya ko xan takara ta yadda mutane za su qi shi.

A wannan bincike an gano cewar su ma waqoqin siyasar Jamhuriya ta huxu cike suke da waxannan dabaru na amfani da hikimomin magana irin su yabo da habaici da zambo da kirari da dai sauransu, domin su tallata xan takara da su kamar yadda za a ga misalai daga waqoqin da aka zanarta.

3.1.3.1 Talla ta Fuskar Yabo

Yabo yana xaya daga cikin hanyoyin da mawaqa suke amfani da shi su tallata 'yan takara. Masana sun bayar da ma'anar wannan kalmar ta yabo. Tsoho (2002:143) ya yi bayanin cewar ana amfani da kalmomin aikatau da kuma siffanta mutum da wasu abubuwa da bayyana halinsa domin a danganta shi da wasu mutane da suke da halin kirki da za a iya danganta shi da su. Shi kuma Xangulbi, (2003:132), ya bayyana yabo da cewar "Yabo shi ne faxar wasu abubuwa ko kalamai nagari game da wani mutum ko wata qungiya ta mutane waxanda idan aka ji su za a so mutumin ko mutanen ko a qara ganin girmansa da kwarjininsa".

Sannan ya kuma, Xangulbi ya bayyana cewar yabo yana da shika-shikai da suka haxa da:

(i) Yabon Asali

(ii) Yabon Kyauta

(iii) Yabon Addini

(iv) Yabon Hali

(v) Yabon Jarumta

(vi) Yabon Mulki/Siyasa

Saboda haka, bisa bayanin da ya gabata, a nan za a iya cewa yabo ya qunshi bayyana mutum ta halayensa ko asalinsa da nufin nuna shi ga jama'a don su so shi ko kuma su qara ganin qimarsa. Haka kuma yabo jigo ne a cikin waqoqi, domin da shi ake bayyanar da halayen mutum. Don haka babbar hanya ce da ake tallata xan takara da ita a cikin waqoqin siyasa. Ga yadda mawaqa suke amfanar da yabo a cikin waqoqinsu. Misali:

Aminu Ibrahim Xandago a waqarsa "Adon Gaskiya Ba Ya Vata" ya yi amfani da yabo a wurare da dama domin kwarzanta gwanin nasa; wato, Sarkin Yamma, Alhaji Yala Magatakarda Wamakko. Ga misalai da waqar misali a baiti na 70, Xandago yana cewa

70 *"Mukhtari assalamu alaikum,*
Maigona za mu yo takenka,
Jarumi ne da ba ya shakka,
In ka ja dole ne a sakar ma".

A nan Xandago yana yabon Mukhtari, wanda xaya ne daga cikin abokan tafiyar Sarkin Yamma. Yabon da yake masa, shi ne ta fuskar jarumtaka. Domin ya nuna ba mai iya ja da Mukhtari, ko ya ja ma, to dole ya saki. Wato shi jarumi yake wanda bai mai iya jayayya da shi.

Haka kuma, Xandago a baiti na 71, ma ya yi amfani da yabo, inda ya ce:

71. "Allah ya qara xaukaka qadari,
Mukhtari mai dubun alkhairi,
Maigona kai nake ma kirari,
Baitin yabo nake qara ma."

A wannan baiti Xandago yana yabon Mukhari ta fuskar kyauta. Yana nuna cewar duk inda zai yi kyauta, to ba ya yin 'yar kaxan. Wato shi ya sa ya ce masa mai dubun alkhairi, domin idan zai yi kyauta, to da yawa yake yi.

Haka shi ma Ibrahim Yala Hayin Banki, a waqarsa "Nijeriya Riqo Sai Mai Gaskiya". Wannan waqar alal haqiqi yabo ya mamaye ta. Sai dai, an xan tsakuro misali daga wasu 'yan baitoci. Misali; tun a baiti na 6, Hayin Banki ya yi amfani da yabo inda ya ce:

6. "Ni na san ka tun kana mulkin gaskiya,
Kun ga a lokacin Buhari bai duniya,
Duk ya kau da wanda ke halin murxiya,
Sannu Buhari kai muke so Nijeriya".

A nan Hayin Banki yana yabon gwaninsa ne, wato Janar Muhammadu Buhari ta fuskar gaskiya da riqon amana. Domin yana nuna cewar a lokacin da Buhari ya yi mulki, to ya yi mulki na gaskiya, wanda kuma babu danne haqin 'yan qasa ko dukiyarsu.

Haka kuma a baiti na 14, Yala Hayin Banki ya yabi Buhari, inda ya ce:

14. "Lallai Daura kin yi xa wanda yake da kyau,
Wanda idan na gan shi ni ba na zudda yau,
Ku jama'a ina kira sai ku riqe da kyau,
Sannu Buhari. Shugaban 'yan Nijeriya."

Ibrahim Yala Hayin Banki ya yi amfani da yabo a cikin wannan baiti ta fuskar asali. Yana nuna asalin Buhari xan Daura ne, kuma mutum ne mai fasali da cikakkar qira, ta yadda kowa zai so shi. Saboda haka ne ma yake kira ga jama'a da su riqe shi da kyau.

Haka ma a baiti na 22, mawaqin ya yabi Buhari ta fuskar gaskiya da riqon amana, inda ya ce:

22. "PTF da kar riqe ai duk mun gani,
Kai ciki da gaskiya ai ni na gani,
Asibitocinmu ko'ina mun san magani,
Hanyoyinmu sun yi kyau duk Nijeriya."

A nan ma, idan an lura, za a ga cewar mawaqin yana yabon gwaninsa ne ta fuskar gaskiya da riqon amana. Domin kuwa har ya tabbatar da gaskiyar Buhari ta amfani da karin maganar nan da ke cewa "ciki da gaskiya, wuqa ba ta huda shi. Sannan kuma ya yabe shi da cewar lokacin da ya riqe PTF ya yi gaskiya kuma an samar da magani a asibitoci. Haka kuma an gyara hanyoyi a duk faxin Nijeriya. Maqasudin mawaqin a nan, yana tallata Buhari ne domin a zave shi, saboda gaskiyarsa.

Haka ma a baiti na 26 Ibrahim Yala ya yabi Buhari inda ya nuna cewar mutum ne wanda ba ya yin murxiya. Ga abin da ya ce a baitin :

26. ' Sannu fiya – fiya da ba ka yin murxiya,
Zo ka kawar da Tanko mai fuskar saniya,
Har da na Babalola mai halin 'yan giya,
Wanda suke ta vata tsarin Nijeriya.'

A Yala yana yabon gwaninsa ne ta fuskar kyawawan halayensa, waxanda suka sa ba ya yin murxiya.

Haka ma Aminu Musa Dako, a waqarsa "*Mu Qasa Mu Tsare Mu Raka*" shi ma, ya yi amfani da yabo domin tallata xan takararsa. Misali, a baiti na 9 da na 11 da kuma na 12, inda ya ce :

9. "Don bai yarda da zalunci ba,
Kuma bai yarda da shashanci ba.

11. Don bai yarda da zalunci ba,
Kuma bai yarda da makirci ba.''

A waxannan baitocin mawaqin yana so ne ya tallata xan takararsa ta hanyar yaba halayensa, cewar mutum ne wanda bai yarda da zalunci da cin hanci ba. Haka kuma mutum ne wanda ba a qulla makirci da shi, kuma bai yarda da makirci ba. Saboda kyawawan halayensa ne ma a baiti na 12, mawaqin yake kira ga jama'a da su riqe Buhari da qarfi kar su bari damar da suka samu ta kuvuce masu domin idan jama'a suka riqi Buhari, to zai kai su tudun- mun- tsira. Ga abin da ya ce :

12. Ku zo mu riqe kata-maqui,
Kun ga ya kai mu tudun tudun-mun tsira.''

Haka ma a baiti na 27 mawaqin ya yabi Buhari inda ya nuna cewar yana burge shi, ba don kamai ba kuwa sai domin halayensa. Mawaqin ya ce :

27. ' Baba Buhari kana burge ni,
Duw wannan aikin sai dai kai."

A wannan baitin mawaqin yana nuna cewar fitar damutane daga qqangin da suka shiga, sai dai Buhari ne kawai zai iya yin haka. Saboda haka, jama'a su zave shi.

3.1.3.2 Talla ta Fuskar Habaici

Masana sun bayyana ma'anar habaici da dama a cikin ayyukansu. Misali, XanHausa (2012:13), ya bayyana ma'anar habaici da cew:

> *"Habaici magana ce da ake yi cikin*
> *hikima da nufin gaya wa wani saqo*
> *amma ba kai tsaye ba, a fakaice*
> *wato a voyayyar manufa."*

Shi kuwa Xangambo, (2008:72), ya bayyyana cewa:

> *"Habaici, magana ce mai voyayyiyar*
> *manufa. Akan yi magana da niyyar*
> *nufin wani abu ga wanda aka yi*
> *maganar dominsa."*

A wannan bincike an fahimci habaici da cewar magana ce da ake yi da wani a kaikace. Mawaqa siyasa suna amfani da habaici ne domin su aibanta abokan hamayya. Dalilin yin haka kuwa, shi ne domin su sa jama'a su qyamace su, su guje su, ko su qi zavarsu, saboda wani mugun hali nasu da aka bayyana a fakaice. Ga misalai na yadda habaici yake kasancewa a cikin waqoqin siyasa.

A cikin wannan waqar "Adon Gaskiya" Ibrahim Aminu Xandago ya yi amfani da habaici a wurare da dama. Sai dai, za a xauko wasu baitoci a matsayin misali don nuna yadda ya

yi amfani da habaici ya aibanta abokin hamayyar gwaninsa. Misali, tun a baiti na 4, inda mawaqin ya ce:

4. *“Allonmu ya cike da rubutu,*
Saura kaxan mu fara karatu,
O’o ko za ya hau sambatu,
Za ya koma kwatancen kurma.”

A nan mawaqin yana habaici ga abokin hamayyar Sarkin Yamma domin ya yi amfani da kalmar o’o ya saya sunan abokin hamayyar. Ya nuna cewar zai fita hayyacinsa, domin kuwa ya kusa ya fara sambatu.

Haka kuma a baiti na 17, xandago ya yi amfani da habaici, inda ya ce

17. *“Mai tunanin ba za mu iya ba,*
Ban san a inda kai ka qware ba,
Ba kwalliya ka wa Allah ba,
Mulkinsa ne ya xan gutsura ma.”

A nan ma ya yi amfani da habaici ya nuna wa abokin hamayyar gwaninsa cewar kada ya yi taqama da mulki, domin Allah ke bayarwa. Kuma idan ma yana tunanin Sarkin Yamma ba zai iya ba, to, ai shi ma ya sani ba kwalliya ya yi wa Allah ba ya ba shi mulkin. Don haka Allah na iya qwacewa ya ba Sarkin Yamma.

Har wa yau, mawaqin ya yi amfani da habaici a baiti na 21, inda ya ce:

21. *“Shi in ka je gun sa bai maka fara’a,*
Yaya za ai nai maka xa’a?
Yau rundunarka na ce a’a,
Na bi wannan da kai ke qyama.”

A nan mawaqin yana habaici ne ga abokin hamayyar Sarkin Yamma, Yala Wamakko. Yana nuna cewar shi ba mutum ba ne mai sakin fuska. Don haka yake sanar da mutane su san halinsa tare da qin yi masa xa'a.

Misali a cikin waqar "'*Yau Nijeriya Riqo Sai Mai Gaskiya*" ta Ibrahim Yala Hayin Banki; ita ma wannan waqar an yi amfani da habaici a cikinta. Misali a na baiti na 13, inda ya ce:

9. *"Wanda ya ja da kai Buhari zai sha wuya,*
Domin ka fi wane mai halin 'yan giya,
Mai fuska kamar ana murjin taliya,
Kai! Hango shi ba ya qaunar Nijeriya."

Mawaqin a wannan baiti yana habaici ne ga abokan hamayyar Buhari. Yana son ya nuna wa jama'a cewar 'yan hamayya fa ba qaunar Nijeriya suke yi ba. Don haka, kada a zave su, a zavi Buhari, domin shi ne yake qaunar 'yan Nijeriya.

Haka kuma a baiti na 5, ma mawaqin ya yi wa abokan hamayyar Buhari habaici, inda ya ce:

5. *"Allah wadan ku tun da ba kwa qaunan mumu,*
Tun da kuna ta mulkinku ba ku kula da mu,
Don Allah Buhari mu zo ka fitar da mu,
Yau kai ne muke so a nan Nijeriya."

Mawaqin yana nuna cewar yana tir da halin abokan hamayya tun da ba su kula da talaka. Saboda haka, Buhari ne suke so ya yi mulkin Nijeriya. Wannan yana nuna cewar mawaqan siyasa suna amfani da habaici su tallata 'yan takararsu ta nuna miyagun

halayen abokan hamayya a fakaice, don jama'a su fahimci hakan, su kuma guje su. Sannan su zavi 'yan takarar da mawaqan ke son tallatawa.

Bugu da qari a baiti na 26, Ibrahim Yala ya yi amfani da habaici, domin ya tallata xan takararsa ta hanyar kushe abokan hamayya inda ya ce :

26. ' Sannu fiya – fiya da ba ka yin murxiya,
Zo ka kawar da Tanko mai fuskar saniya,
Har da na Babalola mai halin 'yan giya,
Wanda suke ta vata tsarin Nijeriya.'

A Yala yana ya yi amfani da habaici domin ya vata abokan hamayyar Buhari doin ya tallata gwanin nasa. Su kuwa abokan hamayya ya kushe su, domin a kaikaice ya nuna su murxiya suke yi.

3.1.3.3 Talla ta Fuskar Zambo

Kamar yadda Xangambo, (2008:73) ya bayyana, shi ne a zagi mutum kai tsaye, inda ake siffanta mutumin da ake zagi da duk wani abu da ya shafe shi wanda zai taimaka a gane da shi ake.

Mawaqan siyasa suna amfani da zambo domin su nuna tsananin gaba da ke akwai tsakanin waxanda suka yi wa waqa da kuma abokan hamayyarsu. Haka kuma sukan yi zambo don cin fuska ga abokan hamayya. Duk wannan ma hanya ce da suke bi, su tallata 'yan takararsu. Domin kuwa, suna vata abokan hamayya ne, su fifita xan takararsu, wato su nuna nasu ne na kirki.

A waqar “Adon Gaskiya Ba Ya Vata” ta Ibrahim Aminu Xandago mawaqin ya yi amfani da zambo a cikin waqarsa a wurare da dama. Ga misali a baiti na 14 da na 39:

14. *“Kai kwaxo ma-sha ruwa ya yi wanka,*
Zahiri gobe za kai hauka,
Tun da ka qetare usulinka,
Ga shi danginka sun bijire ma.”

39. *“Ina ka ga qadangare bi-bango?*
Na ga an ba shi sabon bargo,
Ka kusa ka fara kwanan shago,
Yau ga tsiyarka ta koma ma.”

A waxannan baitocin Xandago yana zambo ne ga abokin hamayyar Magatakarda. A baiti na 14, yana faxa masa cewar ya bar asalinsa har ma danginsa sun guje shi. A baiti na 39, ya nuna cewa halin tsiya da yake ya koma masa. Wato fitsarin faqo ke nan. Abin da ya yi, ya koma masa. Burin mawaqin dai, shi ne ya vata duk wani da yake hamayya da Magatakarda. Domin a zavi shi Magatakarda.

Haka ma an yi amfani da zambo a waqar “*Yau Nijeriya Riqo Sai Mai Gaskiya*” ta Ibrahim Yala Hayin Banki misali, shi ne a baiti na 13, inda ya ce:

10. *“Wanda ya ja da kai Buhari zai sha wuya,*
Domin ka fi wane mai halin ‘yan giya,
Mai fuska kamar ana murjin taliya,
Kai! Hango shi ba qaunar Nijeriya.”

Mawaqin a cikin wannan baitin yana zambo ne ga abokin hamayyar Buhari. Ya nuna cewar duk wanda ya ja da Buhari, to a qasa yake. Yana son ya nuna cewar ba mai iya ja

da Buhari, domin idan ma ya ja, zai faxi. Don haka, yana ganin gwaninsa ne ya kamata a zava.

Bugu da qari Ibrahim Yala ya yi amfani da zambo a baiti na 13 domin ya kushe abokin hamayyar Buhari, sannan kuma, ya fifita nasa xan takarar. Ga abin da ya ce:

13. "*Wanda ya ja da kai Buhari zai sha wuya,*
Domin ka fi wane mai halin 'yan giya,
Mai fuska kamar ana murjin taliya,
Kai ! hango bay a qaunar gaskiya. "

A wannan baitin Yala ya yi wa abokin hamayyar Buhari zambo domin ya kushe shi.

Hakan kuma ke nuna cewar Buhari shi ne ya fi cancanta a zava.

Haka ma a baiti na 26 Ibrahim Yala Hayin Banki ya yi wa abokan hamayyar Buhari zambo inda y ace:

26. "Sannu fiya – fiya dab a ka yin murxiya,
Zo ka kawar da Tanko mai fuskar saniya,
Har da na Babalola mai halin 'yan giya,
Wanda suke ta vata tsarin Nijeriya."

A wannan baitin Yala ya yi wa abokan hamayyar Buhari zambo saboda ya vata su a idon jama'a, kuma ya tallata xan takararsa (Buhari), domin shi ne wanda ba ya murxiya.

3.1.3.4 Talla ta Fuskar Kirari

Masana sun bayyana cewar kirari fitaccen nau'i ne a adabin Hausa da ake samu a cikin zube da kuma waqa. (Amin, 2005). Kirari wasu lafuzza ne da a kan yi na hikima domin nuna qwarewa a harshe, domin koxa wani abu (XanHausa, 2012:13). A kan haka ne ake samun wurare da yawa a cikin waqoqin siyasa, inda mawaqan ke koxa gwanayensu. Su

na yin haka ne kuwa, domin su tsima waxanda suke wa waqar don su yabe su. Misali, Ibrahim Aminu Xandago a waqarsa "*Adon Gaskiya Ba Ya Vata*," ya yi amfani da irin wannan hikimar a baiti na 63 da kuma na 64, inda ya ce:

63. *"Shugaban Jam'iyya Haji Tsalha,*
Yaqi da ku abin ba arha,
Babanku shi ya qwallanta jaha,
Sidi Mamman mafi alfarma.

64. *Jam'iyya yau tana hannunku,*
Alhaji Tsalha ba mu da shakku,
Ka ga mai maganin 'yan tsurku,
Jam'iyya ta zame gogarma."

A nan Xandago ya yi amfani da kirari domin ya kuranta xaya daga cikin 'yan Jam'iyya. Ya yi amfani da kirari a baiti na 63, domin ya koxa Alhaji Tsalha, inda ya nuna cewar karawa fa da shi ba abu ne mai sauqi ba. Don haka, 'yan adawa su bi shi a hankali. Haka ma a baiti na 64, mawaqin ya bayyana cewar ba su da shakka, Alhaji Tsalha zai yi maganin 'yan tsurku.

Haka Ibrahim Yala Hayin Banki a waqarsa '*Yau Nijeriya Sai Mai Gaskiya*," ya yi wa Buhari kirari domin ya garza shi tare da kwarzanta shi a baiti na 26 inda ya ce :

26. Sannu fiya –fiya da ba ka murxiya,
Zo ka kawar da Tanko mai fuskar saniya,
Har da na Babalola mai haslin 'yan giya,
Wanda suke ta vata tsarin Nijeriya. '

Mawaqin a nan ya ya yi Buhari kirari ne ta fuskasr jaruntaka domin ya nuna cewar Buhari ya fi qarfin 'yan adawa.

Haka a baiti na 32 ya yi amfani da wannan salo ya tallata xan takararsa inda ya ce :

32. ‘ Ka zama jinjirin wata kai ne ake jira,
Rana ka riga ka fito ka gagara,
Dutse ka wuce bugu koko tokara,
Har mai gatari Muhammad zai juriya.”

A wannan baiti mawaqin yana qoqarin nuna wa jama’a tare da jawo hankalinsu ta hanyar kirari cewar Buhari fa yana da farin jini kamar yadda jinjirin wata ke da shi ; kowa shi yake so da gani. Sannan kuma ya gagari kowa idan dai maganar takara ce. Don haka mutane su sallama da al’amarinsa, su zave shi.

3.1.4 Jigon Waqar “*Adon Gaskiya Ba Ya Vata”*

Manufar wannan waqa ta “*Adon gaskiya Ba Ya Vata*”, ita ce tallata Alhaji Aliyu Magatakarda Wammako a matsayin xan takarar gwamna a shekara ta 2007 a qarqashin Jam’iyyar PDP. Alhaji Ibrahim Aminu Xandago, mawaqin bayan godiya ga Allah da salatin Annabi a cikin addu’ar buxewa, ya gabatar da qudurinsa a baiti na uku (3) inda ya ce:

3. “*Na yi niyyar in qyanqyashe qwaina,*
Don muradi na nunin qauna,
Allah ka qara jin tausaina,
Yadda waqar ta zan shane ma”.

A nan Xandago ya gabatar da nufinsa na tallata sarkin Yamma a cikin wannan baitin, inda ya nuna cewa nufinsa, shi ne ya warware zare da abawarasa game da wannan xan takara ta yadda waqar za ta haska shi, ta fito da shi.

Daga baiti na biyar (5) zuwa na bakwai (7), mawaqin ya bayyana goyon bayan da xan takarar yake da shi tun daga birni har qauye. Sannan kuma ya nuna cewar duk wanda ya qi shi, to shi ne wahalalle. Kuma ya gargaxi abokin hamayyarsa da cewar ya shiga taitayinsa, domin shi gwaninsa ya shirya inda ya ce a baiti na biyar (5):

5. *"Mai kare maza ka kama karenka,*
Na ga zaki yana sausaka,
Sakkwatawa suna bayanka,
Baba Allah ya yarda ka kama".

Haka ma a baiti na tara (9), mawaqin ya ci gaba da fito da manufarsa ta tallata xan takaransa a baiti na inda ya ce:

9. "*Sarkin Yamma kai muka zava,*
Mulkin Jaharmu ko za ka karva,
Albishir har mutanen Rava,
Kai suke so su sami salama".

Daga baiti na goma har zuwa na sha-huxu yana nuna cewa gwaninsa na da jama'a, mulki kuma na Allah ne, shi ke bayar da shi ga wanda ya so. Haka kuma mulki ba batun naira ne ke bayar da mulki ba.

A baiti na 14 da na 15, mawaqin ya kushe abokin hamayyar ubangidansa inda yake cewa:

14. "*Kai kwaxo ma-sha ruwa ka yi wanka,*
Zahiri gobe za kai hauka,
Tun da ka qetare usulinka,

Ga shi danginka sun bijire ma.

15. “Mai ganin sai da kai za a iya,
Qaryarka o’o ta sha qarya,
Yau da Allah kake jayayya,
Yin xagawarka ta jawo ma.”

A nan ana cewa abokin hamayyar duk danginsa sun bijire mai saboda girman kansa. Kuma saboda yana jayayya da ikon Allah, to tashi ta qare, har ma zai yi hauka domin idan an yi zave na gaba, ba zai ci nasara ba. Daga baiti na 16 zuwa na 19, Xandago na nuna cewa, mulki da arziqi duk na Allah ne, kuma idan ya ba mutum, babu mai qwace masa. A baiti na 23, mawaqin ya nuna jajircewarsa a kan Sarkin Yamma, ko da kuwa za a kashe shi ne. Ga abin da ya ce:

23. “*Qoquwar qi ka sa a kashe ni,*
Na sani Jalla zai kare ni,
Ko za ka sa a yau a dafa ni,
Ban barin Ali zakin fama”.

A baiti na 26 kuwa, yana kururuta jam’iyyarsu saboda ya nuna ta xaukaka, ta fi sauran jam’iyyun sakamakon gata da Sarkin Yamma ya yi mata. Duk da dai cewar a cikin baitin bai ko ambaci sunan jam’iyyar ba a waqar gaba xaya. Ga abin da ya ce:

26. “*Jam’iyyarmu yau ta fifita,*
Sarkin Yamma yai mata gata,
Sakkwatawa suna kwaxayinta,
Wancan yana ta hauma-hauma”.

Haka kuma, idan aka duba a baiti na 47, za a qara tabbatar da cewa Xandago yana tallata Aliyu Magatakarda ne domin a zave shi. Ga abin da mawaqin ya ce:

47. "Ku matasa ku bar jin tsoro,
Zaven da za a je nai horo,
Ran da za ai ku rarraba goro,
Ba gudu babu tsoron fama".

A nan mawaqin na qara jaddada cijewarsa da cewar sai an zavi Magatakarda, bakin rai-bakin-fama. Saboda haka ne ma yake umurtar matasa su raba goron gayyata ranar zave kowa ya fito ba-gudu ba-tsoro a zavi Sarkin Yamma. Daga baiti na 54 zuwa na 61, Aminu Xandago na bayyana goyon bayan da gwaninsa yake da shi a Sakkwato baki xaya kowa shi yake so. Saboda haka, a 2007, kowa shi zai zava, wato ya zarta kowa. Daga qarshe a baiti na 48 ya bayyana qarara cewar talla yake yi, inda ya ce:

48. *Mai taqama da ikon Allah,*
Wallahi sai da nai ma talla
Yau ga shi ka zame mana fitila,
Tun da qaunarka ta kankama. "

Sannan daga baiti na 62 har zuwa na 84, mawaqin ya kawo baitoci na yabon masoyansa masu taimaka masa, kuma fitattun jam'iyya. Ga abin da ya ce a baiti na 62:

62. "*Yanzu zan zo da baitocina,*
Na masoya da ke gwada qauna,
Su suke tallafa wa zamana,
Ba ni yunwa bare nai rama."

A baiti na 85 zuwa na 87 kuwa, ya rufe waqar ne a inda ya bayyana sunansa (wanda ya yi waqar). Yana cewa a baiti na 87:

87. "Sunan mai waqa ga shi,
Ibrahim nake ba na qyashi,
Baban Humaira 'ya mai goshi
'Yar qanena xiya ga Halima".

3.2 Sharhin Waqar " *Yau Nijeriya Sai Mai Gaskiya*," ta Ibrahim Yala Hayin Banki wanda ya yi wa Janar Muhammadu Buhari (ANPP) :

3.2.1 Tarihin Ibrahim Yala Hayin Banki

An haifi Ibrahim Yala Hayin Banki a 1973 a Kawo cikin Qaramar Hukumar Kaduna ta Arewa, Jihar Kaduna. Sunan mahaifinsa Saleh, wanda xan asalin Qaramar Hukumar Gire ne ta Jihar Adamawa. Ana yi wa Ibrahim laqabi da Yala, wanda mahaifiyarsa ce ta laqaba masa tun yana xan qarami saboda ba ya iya faxin 'yara', sai dai ya ce "yala". Ibrahim Yala ya yi karatun Firamare a Makarantar Firamare ta L.E.A. Kawo daga 1983 – 1989. Daga nan ya wuce makarantar Sakandare a tsohuwar KTC, a yanzu G.S.S., daga 1990 – 1996. A halin yanzu kuma yana karatun Diploma a Fannin Harkokin Mulki (Public Administration) a Makarantar Fasaha ta Nuhu Bamalli da ke Zariya (Nuhu Bamalli Polytechnic).

Malam Ibrahim Yala, kamar kowane yaro da ya tashi qasar Hausa, ya yi karatun Islamiyya, kuma ya koyar a Islamiyya. A yanzu haka yana da xalibai da yawa, wasu ma malamai ne su kansu. Daga cikin xalibansa akwai limamin Juma'a na 'Yan Shinkafa Hayin Banki, Kawo Kaduna. Malam Ibrahim ya yi ilimin addini mai Zurfi, har da ma ilimin harshen Larabci.

Dangane da lokacin fara waqarsa kuwa, tun yana xan qaraminsa, lokacin yana firamare yake da sha'awar waqa. Hakan kuma ya sa tun a wancan lokacin ya fara yin waqa. Duka

waqoqinsa rubutawa yake yi, sannan ya rera su. Waqoqin da ya fara yi su ne na yabon Manzon Allah (SAW) a shekara ta 1990. A lokacin yana karanta waqoqin, kuma ya koyar da su. Ya fara waqa ta hululu bayan da aka kai harin September 11, 2001, a Tagwayen Benaye (Pentagon) na Cibiyar Kasuwanci ta Duniya (World Trade Centre) wanda aka jingina wa Osama. A wannan lokacin ne ya rubuta waqarsa ta farko wadda ba ta addini ba mai suna 'Mubaya'a". Ya tsunduma a cikin harkokin siyasa a 1999. Ya rubuta waqoqi da yawansu ya kai kimanin 200. Waxannan kuwa sun haxa da waqoqin madahu da kuma na siyasa.

Dangane kuwa da waqar "*Yau Nijeriya Riqo Sai Mai gaskiya*", ya yi ta ne a shekarar 2002. Dalilin rubuta ta kuwa, shi ne sakamakon shawarar da wani abokinsa mai suna Abubakar ya ba shi, cewar ya shiga siyasa, kuma ya riqa yin waqoqin siyasa saboda Allah ya ba shi fasahar yin waqa. Dalili na biyu kuwa, shi ne, a lokacin ne (2002) Janar Muhammadu Buhari ya shiga cikin harkokin siyasa gadan-gadan, kuma qarqashin Jam'iyyar APP, wadda ta koma ANPP daga baya. A lokacin Ibrahim Yala ya lura cewar Jam'iyyar APP ta yi sanyi qwarai, ta kwanta. Sannan kuma ga Buhari ya shigo ta da niyar kawo canji. Don haka akwai buqatar a tallata Buhari da Jam'iyyarsa don duniya ta san da shi a siyasa. A cikin wannan guguwar canji ne Yala ya yi wannan waqa, watau "*Yau Nijeriya Riqo Sai Mai Gaskiya"*. Wannan waqar kuma ya bayyana cewar ita ce Bakandamiyarsa, wadda kuma ya fi ji da ita. Saboda kuwa ita ce waqar da ta bazu ta yaxu cikin xan lokaci aka san shi da ita ko'ina a faxin Nijeriya. Sannan kuma ta isar da saqon

tallata Buhari da Jam'iyyarsa. Haka kuma ya bayyana cewar akwai littafi da aka rubuta na tarihin Buhari, wanda said a aka kawo waqar gaba xayanta a cikin littafin domin nuna kwarjininta da kuma kasancewar ta jigo a wajen tallata Buhari. Manufa dai, ita ce da wannan waqar ce aka yi wa Buhari Kamfe a zaven 2003. Bayan zave a 2004 Yala ya sabunta waqar inda ya sa mata suna *"Yau Nijeriya An Mana Murxiya*". A shekara ta 2007 ma, ya sabunta ta, ya sa mata suna "*Ya Allah Muna ta Roqo Baki Xaya Allah Ka Ba Buhari Mulkin Nijeriya*".

Ibrahim Yala dai ba kowa ne yake yi wa waqa ba. A'a, yana yi wa Jam'iyyarsa da kuma 'yan Jam'iyyarsa ne kawai, wato Jam'iyyar adawa. Kuma ya fi yi wa Janar Buhari waqa. Sai dai idan ma zai yi wa xan wata Jam'iyya waqa, to sai ya ba da sharaxin cewar ba zai yabi Jam'iyyar wannan mutum ba, kuma shi Yala ba zai kushe Jam'iyyarsa ba a cikin waqar. Misali wannan ita ce waqar da ya yi wa Atiku Abubakar a 2007 mai suna "*Naka Yanzu Sai Naka Atiku Kar Ka Ja Baya"* Yala ya sami sha'awar rubuta waqoqin siyasa saboda bibiyar waqoqin siyasar baya kamar irin su Mudi Sipikin da Sa'adu Zungur da Auwalu Isa Bunguxu da Garba Gashuwa da sauransu. A shekarar 2011 ma, Ibrahim Yala Hayin Banki ya rubuta waqar "*Mai Alqalami*". Mawaqin ya bayyana waqar siyasa da cewar kamar xan jarida ne, kuma ita ce gishirin siyasa. Sannan kuma ya bayyana dalilin da ya sa suke amfani da amshi da kayan kixan zamani cewar suna qara wa waqa armashi da kuma sa mutane su yi saurin hardace ta. Sakamakon haka saqon waqa zai isa ko'ina cikin lokaci.

Daga qarshe, Ibrahim Yala yana da aure, mata biyu da ‘ya’ya goma; maza biyar, mata biyar. A halin yanzu yana zaune a Hayin Banki Kawo Kaduna da iyalansa da mahaifiyarsa. Mahaifinsa kuwa Allah ya yi masa rasuwa. Allah jiqan sa. Ibrahim Yala a matsayinsa na xan siyasa, a halin yanzu yana takarar kujerar Xan Majalisar Dokoki ta Jaha a mazavar Kawo, qarqashin Jam’iyyar APC. [16]

3.2.2 Taqaitaccen Tarihin Jam’iyyar ANPP

Wannan Jam’iyyar ita ma tana daga cikin Jam’iyyun nan guda tara da Hukumar Zave ta Qasa ta yi wa rijista ta wocin gadi a 1998, wanda bayan zaven da aka yi Disamba 1998, ta zama xaya daga cikin ukun nan da aka amince su zama cikakkun jam’iyyu a farkon jamhuriyya ta huxu. Jam’iyyun su ne AD da APP da kuma PDP (Umaru 2003) da (Daure 2000). Wannan Jam’iyya an fara yi mata rijista da suna APP, amma daga baya ta canza suna zuwa ANPP a shekara ta 2006 (Umaru, 2003:31) da (Paden, 2008:57).

Ita ma wannan Jam’iyyar tana da jiga-jigan da suka kafa ta, qarqashin jagoranta Janar Muhammadu Buhari, wanda kuma ya yi wa Jam’iyyar takarar shugabancin qasa har karo biyu; 2003 da 2007 (Paden, 2008). Daga cikin jagororinta akwai Malam Ibrahim Shekarau, wanda shi ne daraktan kamfe na Janar Buhari, kuma ya yi gwamnan Kano 2007-2011, kuma xan takarar shugaban Qasa na jam’iyyar a 2011. Sauran manyan Jam’iyya sun haxa da Dr. Christopher Ogbunna Onu da Sanata Hadi Sirika da Alhaji Aminu Bello Masari da Honorabul Lawan Shettima da Cif Okey Nwosu, wanda kuma shi

[16] Hira da Malam Ibrahim Yala Hayin Banki Kawo Kaduna ranar Lahadi 23 ga Watan Fabrairu, 2014

ne Shugabanta na farko. Jam'iyyar ta shiga qawance a 2013, inda ta haxe da wasu Jam'iyyun hamayya (CPC da ACN da APGA) inda suka narke suka zama jam'iyya guda wato APC a ranar 11 ga watan Mayu, 2013. Tana da babbar manufa ta ganin cewa an yaqi cin hanci da zalunci sannan kuma da ganin an tsayar da adalci a tsakanin 'yan qasa wajen gudanar da mulki da cigaban qasa. Ita ce babbar Jam'iyyar adawa a arewa kafin kafuwar CPC

3.2.3 Sharhin Waqar "*Yau Nijeriya Riqo Sai Mai Gaskiya"*

Wannan waqar jigonta shi ne tallata Janar Buhari ga kujerar shugabancin qasa ta nuna kyawawan halayensa da suka haxa da riqon amana da gaskiya a cikin al'amuransa. Wannan waqa domin nuna goyon baya ga wannan xan takara, tare kuma da yin kira ga jama'ar Nijeriya gaba xaya da su zave shi. Tun a baiti na farko aka gabatar da manufar waqar. Sannan kuma, mawaqin ya ci gaba da gabatar da manufarsa a baiti na uku (3), inda ya ce:

3. "*Ka zo ka fitar da mu a quncin da muke ciki,*
Don mun sha wuya a kullum kai farmaki,
Ana satan kuxinmu a yau ba shamaki,
Ka ji halin da muke ciki Nijeriya".

A nan farkon abin da mawaqin yake so ya nuna, shi ne halin 'ni-'yasun' da qasa ta shiga na wahalar da talakawa suke sha da yadda masu mulki suke wandaqa da dukiyar qasa. Don haka ne yake kira ga Buhari da ya zo ya ceto Nijeriya daga halin da ta shiga, domin yana ganin shi ne zai iya yin hakan.

Haka ma a baiti na gaba (na 4), yake qara tabbatar da dalilinsa na buqatar Buhari ya yi mulkin Nijeriya, saboda gaskiyarsa. Ga abin da ya ce:

4. "*Tanko da Babalola suna ta halin tsiya,*
Mu da kuxinmu ga shi duk an mana murxiya,
Shi yas sa muk bixa yau Mai Gaskiya,
Wanda idan ya zo, za ya gyara Nijeriya".

Haka dai mawaqin ya ci gaba da zayyana kyawawan halayen gwaninsa a baiti na 5-7.

Sannan kuma a baiti na takwas (8) ya qarfafa dalilinsa na son Buhari ya shugabanci Nijeriya. Ga abin da yake cewa:

8. "*Kun ga a lokacin yaq qi bashin ingila,*
Har da Amerika masu halin baxila,
IMF ya ce ba ya so don mattsala,
Mun gode Buhari mai kishin gaskiya".

A nan Ibrahim Hayin Banki yana bayyana Buhari ne da cewar shi xan kishin qasa, domin ya qi cin bashin IMF a lokacin da ya yi mulkin qasar nan, wanda karvar wannan bashi, ya saka qasa cikin matsala da qangin da fita daga gare shi, sai an sha wuya.

Haka ma a baiti na tara (9) mawaqin ya nuna kishin qasa na Janar Buhari, saboda a lokacinsa ya hana varnata dukiyar qasa. Sannan kuma tattalin arziqin qasa, ya bunqasa. Yana cewa:

9. "*Ya kau dar da 'yan ta'addar da suke qasa,*
Masu kuxin da ba su zakka sun bar qasa,
Kun ji a lokacin tattali ya bunqasa,
Har a qasarmu mun kasance ba ma tsiya."

Duk wannan, mawaqin na nuna halaye ne da Buhari yake da su, waxanda suka cancanta a zave shi domin samun sa'ida a rayuwa. Kan wannan ne ma mawaqin ya nuna yadda azzalumi ba ya zama inuwa xaya da Buhari. Ga abin da ya ce a baiti na sha-xaya (11):

11. "*Wancan lokacin farar hula sun gudu,*
Domin sun yi varna dole su zan gudu,
Yanzu idan ka hau dole wancan nag gudun,
Zai tsere ya bar qasai don bai gaskiya".

Wannan ya nuna yadda azzalumai suke wasan vuya da janar Buhari, kamar dai mage da vera. Saboda duk wanda ya yi zalunci idan bai gudu ba, ya san kashinsa ya bushe. Duk waxannan halaye ne da mawaqin yake tallata Buhari da su domin a zave shi. Domin shi gwanin nasa bai yarda da a fallasa dukiyar qasa ba.

A baiti na sha biyu (12), sai ya nuna cewar PDP azzaluma ce. Don haka, ANPP ta zo ta karvi mulkin Nijeriya don ta ceto ta daga halin mulki irin na PDP. Ga abin da ya ce:

12. "*Ke lema baqar daga kin mana yau tsiya,*
Ba kya maganin ruwa duk mun sha wuya,
Ke lema fa mulkinki ba kya gaskiya,
ANPP zo ki tallafi Nijeriya. "

A nan Ibrahim hayin banki yana kushe mulkin jam'iyyar PDP ne, saboda mulkinta ya saka jama'a cikin halin qaqa-ni-ka-yi. A nan sai ya kwatanta jam'iyyar ANPP, wadda yake ganin ita ce za ta iya yin mulkin gaskiya. Haka dai ya yi ta kawo baitoci masu nuna halin qunci da mulkin Obasanjo ya saka 'yan qasa ciki har zuwa baiti na talatin-da-xaya. A baiti na 32 kuwa, ya kuranta Buhari ne tare da zuguguta shi, inda yake nuna ya gagari

kowa. Daga baiti na 33 har zuwa na 42, mawaqin ya nuna goyon bayan da Buhari yake da shi a duk faxin Nijeriya. Da kuma yabon wasu daga cikin magoya bayan Buhari.

Duk dai idan aka lura, za a ga cewar mawaqin yana tallata janar Buhari ne. domin kuwa dama daga cikin siffofin talla, akwai yabo da kirari da zuga da sauransu ga abin da ake tallatawa. Haka ma akwai kushewa da zambo da habaici da qasqantarwa da sauransu ga wanda yake kishiya ga abin da ake tallatawa. Don a nan ana tallata xan takarar jam'iyyar ANPP, domin an bayyana kyawawan halayensa. An kuma nuna illolin kishiyarsa na saka qasa cikin halin ha'u-la'i. Dama al'adar mai talla ke nan, ya kushe na wani, ya kuranta nasa.

Za a tabbatar da cewar ana tallata Buhari ne domin a zave shi, inda mawaqin ya fito qarara ya nuna hakan a baiti na 27 kamar haka:

27. "*Kun ga siyasarmu mun koma bara,*
Don haka nai kiran mutane kui hattara,
Kan zancen da nay yi walla ba na qirqira,
Sai mu zage mu zavi mai kishin gaskiya. "

Wannan ya nuna halin da 'yan siyasa suka jefa al'ummar qasa na maula da bara da banga da qangin talauci. Don haka, mawaqin yake ankarar da jama'a da su shiga jirgin Janar Buhari. Wato su zave shi, domin ya fitar da su daga qangin da suka shiga.

3.3 Sharhin Waqar "*Mu Kasa Mu Tsare Mu Raka* ,'' wadda Mohammed Aminu Musa Dako ya yi wa Janar Muhammadu Buhari a qarqashin Jam'iyyar CPC .

3.3.1 Tarihin Mohammed Aminu Musa Dako

An haifi Mohammed Aminu Musa Dako a 1982 garin Dako qarqashin Qaramar Hukumar Giwa ta Jihar Kaduna. Ya yi makarantar Firamare a makarantar Firamare ta Pada, Zariya daga shekara ta 1992-1997. Daga nan ya wuce makarantar Sakandaren Gwammati ta Tukur-Tukur, Zariya, daga 1997-2000, inda ya kammala karatun Qaramar Makarantar Sakandare (Junior Secondary School). Daga nan kuma, ya cigaba da karatun Babbar Sakandare (Senior Secondary School) a Barewa Kwaleji, Zariya, a inda ya kammala Sakandare daga 2000-2003. Mohammed Aminu Musa Dako bai gajiya ba, domin a shekara ta 2007, ya je Kwalejin Ilmi ta Tarayya, Zariya ya yi kwas na share fagen karatun Takardar Shaidar Ilmi ta Qasa a fannin Kimiyya (Pre-NCE Science). Bayan nan kuma, a shekara ta 2008 ya wuce zuwa Amir Shehu Idris College of Advanced Studies, a inda ya kammala Difloma a harshen Hausa da Dabarun Koyarwa (Hausa Language Education). Ya sami kammala wannan Difloma a shekara ta 2010. Haka kuma, ta fannin addinin Musulunci, kamar kowa, shi ma Aminu Dako ba a bar shi a baya ba. Domin kuwa ya yi karatun allo da na littattafan fannoni na addini. Ya ziyarci wurare da dama inda ya zauna ya yi karatun Alqur'ani Maigirma. Daga cikin garuruwan da ya halarta, sun haxa da Bakori da kuma garin 'Yar Kasuwa da ke cikin Qaramar Hukumar Xandume dukkansa a cikin Jihar Katsina.

Dangane da harkokin siyasa kuwa, Dako ya shiga cikin harkokin siyasa tsamo-tsamo a shekara ta 1999. Ya shiga Jam'iyyar PDP wadda ya kasance a cikinta har zuwa shekarar 2007 a lokacin da ya canza sheqa zuwa Jam'iyyar ANPP. A cikin wannan Jam'iyyar ne

suka zama ‘yan adawa, suka kuma ci gaba da gwagwarmayar neman canji qarqashin jagorancin Janar Muhammadu Buhari. Daga baya ne, a 2011, Janar Buhari da magoya bayansa ciki har da Aminu Musa Dako, suka bar Jam’iyyar ANPP, Buhari ya kafa Jam’iyyar CPC.

Aminu Musa Dako dangane da lokacin fara waqarsa, sai a shekarar 2011 ya fara waqa. Wannan waqar kuma ta *“Mu Kasa Mu Tsare Mu Raka”* ita ce ta farko da ya yi. Sannan dukan waqoqin da yake yi, rubuta su yake yi kafin ya rera su. Dangane da dalilin rubuta wannan waqar kuwa, shi ne domin ya yi kira ga jama’a su haxa kansu a zaven 2011, su zavi Buhari. Wato yana faxakar da al’umma ne cewar kada su bari wannan damar ta 2011 ta wuce, su yi asarar quri’a. Sannan kuma babban dalili, shi ne domin ya tallata Janar Muhammadu Buhari, mutane su san shi da matsayinsa. Domin su zave shi a matsayin Shugaban Qasar Nijeriya.

Dangane da ire-iren waqoqin da yake yi kuwa, na siyasa ne zalla. Sannan kuma ya na yi wa Jam’iyyar adawa ce kawai. A yanzu yana a Jam’iyyar APC. Akwai waqoqi guda uku da ya rubuta, waxanda bai kai ga rera su ba. Daga ciki akwai wadda ya yi wa Sanata Janar Sani Sale mai wakiltar Kaduna ta Tsakiya qarqashin Jam’iyyar APC.

Kamar dai yadda ake cewa “Waqa a Bakin mai ita, ta fi daxi”, Aminu Dako ya tofa albarkacin bakinsa game da ma’anar waqar siyasa a bisa fahimtarsa. Ya bayyana waqar siyasa kamar haka:

“*Waqar siyasa ta shafi bayani da za a*

gane Jam'iyya da 'yan siyasa don a
gane manufofinta don mutum ya san
siyasar da ya kamata ya yi daga waqoqin
Sannan kuma 'yan siyasa za su sami qarfin
Gwiwa. Sannan kuma, su san wanda ya
Kamata su zava."

Bugu da qari, Aminu ya bayyana cewar ana sanya amshi a cikin waqoqin siyasa domin yana sa waqar ta ba da ma'ana. Sannan kuma mai waqa zai sami damar sararawa da yin tunanin wata manufar da zai bayyana a lokacin da ake yin amshi. Dangane da sanya kixa kuwa, Aminu ya bayyana cewar ana sa shi ne domin ya sa nishaxi. Sannan kuma ya qara sa a ji daxin waqar, har a tsaya a saurare ta. Ta haka ne saqon mawaqi zai sami isa ga jama'a.

Daga qarshe, Mohammed Aminu Musa yana zaune a garinsu, Dako. Yana da aure mata guda da xa guda mai suna Auwal, wanda shi ne xansa na farko. Dangane da sana'ar da yake yi kuwa, ita ce noma da kiwo. Sannan kuma a halin yanzu, Aminu Dako xalibi ne mai karatun Digirin Farko a kan Hausa haxe da Ilmin Koyarwa (B.Ed Hausa) a Kwalejin Gwamnatin Tarayya ta Zariya (FCE), wanda ya fara a shekarar karatu ta 2013/2014.[17]

3.3.2 Taqaitaccen Tarihin Jam'iyyar CPC

Wannan Jam'iyyar an kafa ta a 2009 da nufin shirin zaven 2011 a ga mulki ya baro Jam'iyyar PDP. Ita ce ta zama babbar Jam'iyyar adawa a arewa. A zaven 2011. Wannan Jam'iyya ta samo asali daga qungiya mai suna The Buhari Organisation (TBO) wadda

[17] Hira da Malam Mohammed Aminu Musa Dako ranar Litinin 24 ga Watan Fabrairu, 2014

aka yi a 2006 qarqashin jagorancin Janar Muhammadu Buhari. Ta qara havaqa ne tun lokacin da aka yi zaven 2007, inda ra'ayin 'yan Jam'iyya ya rabu gida biyu. Xaya vangare na Janar Muhammadu Buhari, xaya kuma na Malam Ibrahim Shekarau. Wannan rabuwar kuwa ta samo asali ne sakamakon qarar da aka kai a kotu ana qalubalantar zaven 2007. Sai wasu daga cikin 'yan jam'iyyar ANPP suka zame, suka nuna goyon bayan gwamnati. Wannan na daga cikin abubuwan da suka kawo farraqa a jasm'iyyar ANPP. Buhari da jama'arsa sai suka bar ANPP suka kafa jam'iyyar CPC.

Daga cikin manyan Jam'iyyar sun haxa da jagoranta Janar Muhammadu Buhari da Sanata Hadi Sirika da Honorabul Aminu Bello Masari da Cif Tony Momoh, wanda shi ne shugabanta na farko da Injiniya Buba Galadima Sakataren Jam'iyyar da Sanata Rufa'i Hanga da sauransu. Jam'iyyar CPC da wasu jam'iyyun adawa, kamar su ACN da ANPP da APGA sun so su yi qawance a 2011, amma haqa ba ta cim ma ruwa ba. Sai a 2013 waxannan jam'iyyu wato CPC da ACN da ANPP suka shiga qawance inda suka amince da sunan APC. Janar Muhammadu Buhari dai, shi ya yi wa CPC takarar shugaban qasa a 2011. Kuma shi ne jagoran qawancen da jam'iyyun hamayyar suka yi. An yi wannan qawance, inda aka yi taron qaddamar da shi da sunan Jam'iyyar APC a Dandalin Eagle Square, Abuja ranar 11 ga watan Mayu, 2013. Daga cikin manyan da suka halarci wannan taro, kuma manyan Jam'iyyar qawance ta APC, sun haxa da Asiwaju Bola Ahmed Tinubu da Cif Bisi Akande, wanda kuma shi ne Shugaban Riqo na Jam'iyyar qawance ta APC da Alhaji Layi Mohammed dukansu daga ACN. Da Dr. Ogbonnaya Onu

da Alhaji Attahiru Bafarawa da Malam Ibrahim Shekarau da Sanata Ahmed Sani Yariman Bakura daga ANPP da kuma Owelle Rochas Okorocha daga Jam'iyyar APGA (Jawabin Janar Muhammadu Buhari a taron 11 ga Mayu, 2013, shafi na 2). Haka kuma daga cikin manyan wannan Jam'iyyar akwai Malam Nasiru El-Rufa'i, wanda shi ne Mataimakin Sakatare na riqo na Jam'iyyar ta APC. Manufofin wannan Jam'iyyar ta APC su ne :

i. Tsarin mulki
ii. Samar da tsaro ga qasa
iii. Samar da zaman lafiya da haxin kan 'yan qasa
iv. Samar da aikin yi ga 'yan qasa
v. Ba da muhimmanci ga aikin gona
vi. Raya da samar da masana'antu
vii. Gina hanyoyi
viii. Inganta masana'antun mai da samar da iskar gas
ix. Ba da muhimmanci ga harkokin ilimi
x. Kula da lafiyar 'yan qasa
xi. Inganta rayuwar matasa, wasanni da al'adun gargajiya
xii. Qarfafa mata da ba su damar a dama da su
xiii. Kula da muhalli

xiv. Manufofin qasahen waje[18]

Jam'iyyar ita ma ta yi ta samun raguwa da qaruwa a cikinta. Misali a cikin watan Fabrairun 2014 ne APC ta yi kamun babban kifi inda ta samu Turakin Adamawa, Alhaji Atiku Abubakar ya dawo cikinta (Jaridar Weeklytrust, Asabar 15 ga Fabrairu 2014, shafi na 6). Atiku dai yana gaba-gaba wajen darewar Jam'iyyar PDP zuwa gida biyu. Yana da tarihin gwagwarmayar siyasa, domin ko a 2006, sai da ya bar PDP ya kafa Jam'iyyar AC don tunkarar zaven 2007 (Paden, 2008:57). Sai dai kuma daga baya ya dawo PDP, sai a 2014 ne kuma ya bar ta zuwa APC. Akwai Sanatoci da 'Yan Majalissun Wakilai na Tarayya da yawa da suka baro PDP zuwa APC. Sai dai duk da haka, ita ma Jam'iyyar ta APC ta rasa wasu manyan 'ya'yanta misali Malam Ibrahim Shekarau da Alhaji Attahiru Xalhatu Bafarawa da suka bar APC zuwa PDP. Wannan Jam'iyyar yanzu dai, ita ce babbar Jam'iyyar adawa a Nijeriya a wannan Jamhuriya ta huxu domin tunkarar zaven 2015.

Wannan waqar an shirya ta ne domin nuna Buhari, xan takarar shugabancin qasa a qarqashin Jam'iyyar ANPP a zaven shekara ta 2007. Waqar tana da amshi kamar haka:

"*Yau Nijeriya Riqo Sai Mai Gaskiya,*
Sannu Buhari kai muke so Nijeriya".

3.3.3 Sharhin Waqar "*Mu Kasa Mu Tsare Mu Raka*"

[18] Domin qarin bayani a duba jaridar DailyTrust ta ranar Juma'a 14 ga Maris, 2014, shafi na 16.

Wannan waqar tana da amshi kamar haka:

CPC Canji muka nema,

"Mu ba mu yarda da shashanci ba"

Jigonta shi ne kira ga jama'a su mara wa Janar Buhari baya don ganin ya hau karagar mulki a shekara ta 2011.

Idan aka duba, tun a baiti na biyu (2) ne mawaqin ya fara gabatar da manufarsa inda ya ce:

2. *"Maza da mata dangii guna,*
   Na yi kiran ku, ku xan saurara".

Saboda haka, idan aka lura a wannan baiti, tun farko ana jawo hankalin jama'a ne domin su saurari saqon da waqar take xauke da shi. Haka ma a baiti na 3 da na 5, duk suna yin kira ne da jawo hankali. A baiti na 5 yana cewa:

5. *" ku daina yawan sa- in- sa,*
   Ko kui gane gane nufin manufata."

A wannan baitin Aminu Dako yana faxakar da al'umma cewar su daina tsayawa jayayya, wannan ya ce sai wane, wancan ya ce sai wane. Duk su haxu su zavi Buhari.

A baiti na 6 ne mawaqin ya fitar da maitarsa a fili, inda ya ce:

6. "*Ku zo mu rufa mai baya,*
   Kun ga ya kai mu tudun-mun-tsira".

A nan ya fito fili ya nemi goyon bayan jama'a ga Janar Buhari domin ya ceto su daga halin da suka shiga.

A baiti na 9 da na 10 kuwa, an bayyana wasu daga cikin halayen Janar Buhari ne. misali, a baiti na 9 yana cewa:

9. "*Don bai yarda da cin hanci ba,*
Kuma bai yarda da shashanci ba."

Wannan na nuna cewa Buhari yana qyamar cin hanci da qulle-qullen makirci. Don haka ne mawaqin yake ganin ya cancanci a zave shi. Kan haka ne a baiti na 12 ake kwatanta wa jama'a cewar dama ta samu kada a rasa ta. Ga abin da mawaqin ya ce:

12. "*Ku zo mu riqe kata-maqui,*
Kar mu bari ta vare manufata".

A baiti na 18 zuwa na 20, an yi kira ga jama'a baki xaya, har ma da Malam Shekarau xan takarar shugabancin qasa a jam'iyyar ANPP da Nuhu Ribaxo na jam'iyyar ACN, cewa duk a haxe a zavi Buhari. Ga abin da mawaqin y ace:

18. *"Ya Malam maigirma guna,*
Na yi kira a gare ka do Allah.

19. *Nemi Janar ku haxe manufata,*
Ku kui kai mu tudun- mun – tsira."

20. *Haxa da Ribaxo na Birnin Yola,*
Nemi Janar Mu haxe manufata."

A cikin waxannan baitoci, mawaqin yana jaddada manufarsa ce ta hanyar kira ga kowa- da- kowa a haxe a zavi Buhari.

Tun daga baiti na 22 har zuwa na 27, duk yana kwatanta wa jama'a ne da cewar dama ta samu, idan kuma suka bari ta kuvuce, to sun yi asarar quri'a. Don haka su haxa kansu su zavi Buhari. Ga abin day a ce a baiti na 25:

25. "in kun qi amsa kiran manufata,
To asarar quri'a ce zalla."

A wannan baiti Aminu Dako yana qara kwatanta wa jama'a ne game da muhimmancin amsa kiransa, domin idan sun qi amsa ikiran, to sakamakon haka shi ne asarar quri'a.

3.4 Naxewa

A wannan babi, an bibiyi tarihin mawaqan da aka nazarci ayyukansu da yadda Jam'iyyun ANPP da PDP da kuma CPC suka kafu a Jamhuriya ta huxu. Sannan kuma an yi sharhi a kan hanyoyin da mawaqan siyasa suke bi su tallata xan takara. Waxannan hanyoyin sun haxa da yabo da zuga da kirari, waxanda ake garza xan takara a kwarzanta shi a idon jama'a domin a ga qimarsa, a kuma san halayensa na kirki domin a zave shi. Haka kuma a cikin binciken an gano cewa suna amfani da zambo da habaici da sauransu suna kushe abokan hamayya domin a daqilar da su, ko a muzanta su ta yadda girmansu zai faxi a idon jama'a. Daga qarshe an yi sharhin waqoqin tare da bayyana jigoginsu. Binciken ya gano cewar duka waqoqin tallata xan takara suke yi.

BABI NA HUXU:
SALO DA TSARIN WAQOQIN SIYASAR JAMHURIYA TA HUXU

4.0 Gabatarwa

Xangambo (1981:2), ya bayyana ma'anar salo ta fuskoki guda huxu kamar haka:

i.Salo wani abu ne da ya qunshi zavi a cikin rubutu ko furuci.

ii.Salo wani qari ne na daraja a cikin rubutu ko furuci, wanda ba lalle ba ne a same shi cikin kowane rubutu ko furuci.

iii.Salo ya shafi kauce wa daidaitacciyar qa'ida (misali karya dokar nahawu).

iv.Salo harshen wani mutum ne, wato yadda salon Audu ya bambanta da na Tanko.

4.1.1 Salon Waqar "*Adon Gaskiya Ba Ya Vata*," wadda aka yi wa Sarkin Yamma, ta Alhaji Aminu Ibrahim Xandago:

Kamar dai yadda aka gani a baya, salo babban abu ne a cikin sha'ani na waqa da kuma nazarinta. Masana sun bayyana ma'anar salo da nau'o'insa kamar yadda aka gani. Misali, (Mukhtar, 2004:34), ya bayyana cewa salo na daga cikin abubuwan da ake dubawa domin yanke hukunci game da salon marubuci. Daga cikin abubuwan da ake dubawa, sun haxa da: irin kalmomin da aka yi amfani da su, da kuma adon magana da ya haxa da amfani da karin magana da sauran maganganun hikima.

Ita ma wannan waqar, kamar sauran waqoqi, tana da irin nata salon da mawaqin ya yi amfani da shi domin ganin ya qayatar, ya kuma isar da saqonsa ga jama'a cikin sauqi da kuma armashi.

4.1.2 Kamantawa

Daga cikin irin salon da mawaqin ya yi amfani da shi akwai kamantawa. Kamar dai yadda aka gani a babin da ya gabata, kamantawa iri uku ce; akwai ta daidaito da ta fifiko

da kuma ta kasawa. Ga wasu ‘yan misalai na wuraren da aka yi amfani da wannan salon a cikin waqar:

4.1.3 Kamancen Fifiko

Haka kuma mawaqin ya yi amfani da kamancen fifiko domin ya nuna cewar gwaninsa fa ya fi qarfin duk wani mai ja da shi a wajen takara. Misali, a baiti na 26 da na 44 yana cewa:

*26. “ Jam’yyarmu **ta fifita,***
Sarkin Yamma yai mata gata,
Sakkwatawa suna kwaxayin ta,
Wancan yana ta hauma- hauma.’’

A wannan baitin na 26 Ibrahim Xandago yana fifita jam’iyyar gwaninsa domin ya nuna cewar ta zarce ta ‘yan adawa. Sannan kuma duk al’amuran jam’iyya, suna hannunsa sai abin da ya ce. Wato ya fi kowa faxa- a- ji a cikin jam’iyyar.

44. “ Tauraruwarka ke haskawa,
Ahmed Yarima ka dushe
***Ka fi su** xaukaka ga baiwa,*
Ba a zarta ka, ba a musa ma”.

Haka dai ya ci gaba da amfani da kwatancen fifiko inda yake fifita Ahmed Yarimada a wannan baitin na 44. A nan yana xaukaka shi da nuna cewar yana da farin jinni da kwarjini fiye da kowa.

Haka ma a baiti na 41 mawaqin ya yi amfani da kwatancen fifiko inda yake cewa:

41. “Sau uku Yarima na ban Makka,
Ahmad Sani muna gai da ka,
Gwamna mai sansanin albarka,

Babu gwamnan da yai ka a girma".

A nan mawaqin ya kwatanta Yariman Bakura domin ya nuna cewar mutum ne mai karimci da baiwa, kuma babu wani gwamnan da ya kai shi a girman daraja da kyauta. Ya yi haka ne domin ya fifita ubangidansa a kan abokan hamayya.

4.1.4 Abuntarwa

Wannan salo ne da mawaqa suke amfani da shi a cikin waqoqinsu domin samun sauqin isar da saqonsu. Masana sun bayyana wannan dabara da cewar ana mayar da mutum ko dabba ko tsuntsu ko wani abu mai rai ya zama marar rai (Xangambo, 2008:42). A cijkin wannan waqar ma, ta *"Adon Gaskiya Ba Ya Vata"* Ibrahim Aminu Xandago ya yi amfanui da irin wannan salo a wurare da yawa. Sai dai ga misali. A baiti na 45 da kuma na 52, inda ya ce:

45."Ahmad Yarima babban qyaure,
Mai qin ka ya zame makararre,
Qarshensa zai yi tallar sure,
Jam'iyya gaba ya faxa xamama"

52."Ga gajimare mai rufe hadari,
Ya lulluve dukan taurari,
'Yan adawa ku bar mana kuri,
Rundunar mai dabo ta suma"

A baiti na 45, Xandago ya abuntar da Ahmad Yariman Bakura da babban qyaure domin ya nuna cewar babban jigo ne a jam'iyya. Sannan kuma ya yi qarfi. Don haka abokan

hamayya sun makaro. Wato “Maharba kun yi sake har xan Zaki ya girma”, in ji masu hikimar magana. Haka ma dai a baiti na 52, shi ma an abuntar da Yarima, inda mawaqi ya nuna cewar Yarima ya mamaye ‘yan adawa, kamar yadda hadari yake lulluve taurari. Wato ‘yan adawa ba mai ganinsu ko jin motsinsu idan dai Yarima yana a wuri.

4.1.5 Abuntarwar Abuntarwa

Wannan salo ne shi ma da mawaqa kan yi amfani da shi domin kwatanta wani abu da wani abun. Wato shi ne a xauki wani abu marar rai a kwatanta shi da wani abun daban marar rai (Xangambo, 2008:42). A cikin wannan waqa ta “*Adon Gaskiya Ba Ya Vata*”, an yi amfani da wannan salon a wurare da dama. Misali a baiti na 3 da kuma na 76, inda ya ce:

3. “Na yi niyyar in qyanqyashe qwaina,
Don muradi na nunin qauna,
Allah Ka qara jin tausaina,
Yadda waqar ta zan shane ma.”

76. “Yau ga Baba Ata ya gane,
Wasu sirrukan da shi aka binne,
Daure ka kai mu Baba mu tone,
Da guda-guda mu samu makama.”

A baiti na 3, Xandago ya abuntar da sirrin da ke cikin zuciyarsa da qwai, wanda zai fashe wato zai bayyana maganarsa ta nuna so ko qaunar da yake yi wa gwanin nasa. Haka a baiti na 76, ya abuntar da sirrin da aka samo na abokan hamayya, inda ya kwatanta shi da wani abu wanda za a iya gani har a tone.

4.1.6 Jinsintarwa

Haka kuma an yi amfani da jinsintarwa a wurare daban-daban da ya haxa da mutuntarwa da abuntarwa da dabbantarwa da sauransu. Misali a baiti na 56 Xandago ya yi amfani da dabbantarwa inda ya ce:

56. "*Allahu mai cikakken iko,*
Dubi zakaranmu ya haxa zanko,
Ya Rabbi qara qarfin qarko,
Sarkin Yamma in masa dama".

A nan ya kwatanta Sarkin Yamma da zakara mai zanko saboda nuna cewar ya qasaita, ya kuma sami qima da kwarjini a idon jama'a. Domin ai sai zakaran da ya qasaita ya cika yake yin zanko.

4.1.7 Alamtarwa

Kwatantawa ce da ake bayyana wani abu ta hanyar ba shi wata alama wadda za ta tsaya a maimakonsa (Xangambo, 2008:42).

A baiti na 44 da na 45, ya yi amfani da wannan salo na kwatance ta fuskar jinsintarwa inda ya abuntar da Ahmed Yarima inda yake cewa:

44. "*Tauraruwarka ke haskawa,*
Ahmed Yarima ka dushe kowa,
Ka fi su xaukaka ga baiwa,
Ba a zarta ka, ba a musa ma.

45. Ahmed yarima babban qyaure,
Mai qin ka ya zame makararre,
Qarshensa zai yi tallar sure,
Jam'iyya gaba ya faxa xamamma".

A kwatanta Yarima a inda aka alamta farin jininsa da saboda yadda yake haskawa ga jama'a ya dushe kowa. A baiti na 45 kuma aka kwatanta shi da babban qyaure a inda aka alamta kwarjininsa babban qyauredomin nuna yadda ya zama jigo, kuma ya xaukaka a kan jama'a.

4.1.8 Kambamar Zulaqe

Masana sun bayyana wannan salo da cewar dabara ce ta kambamawa da qarin gishiri don jawo hankali (Xangambo, 1981:6). Masu shirya waqoqin siyasa, su ma suna amfani da wannan salon domin su kambama waxanda suke yi wa waqa don su nuna xaukakarsu da kuma yadda suka kama qasa, wato suka samu digi a cikin siyasarsu. Misali, Ibrahim Aminu Xandago ya yi amfani da wannan salon a waqarsa ta "*Adon Gaskiya Ba Ya Vata*" a baiti na 52 inda ya ce:

52. "Ga gajimare mai rufe hadari,
Ya lulluve dukan taurari,
'Yan adawa ku bar mana kuri,
Rundunar mai dabo ta suma."

A nan Xandago yana kambama Sarkin Yamma ne inda ya kwatanta shi da gajimare wanda yake rufe hadari, kuma ya lulluve taurari. Ya yi haka domin ya nuna wa 'yan adawa cewar qaryarsu ta qare, kuma ba su da wata faffaka da za su yi. Domin kuwa, Sarkin Yamma, ya wuce da saninsu.

4.1.9 Sarrafa Harshe

Masana sun bayyana sarrafa harshe da zcewar shi ne yadda za a yi nazarin harshen waqa, wato abubuwan da suka shafi nahawu a cikin waqar (Xandago, 1981:11).

4.1.9.1 Karin Magana

Karin magana ita ce hanyar da ake auna qwarewar mutum ga harshen Hausa, ta yadda yake amfani da ita a cikin maganarsa (Amin, 2005:168). Wannan dabara ce da ake dunqule magana mai yawa a cikin zance ko ‘yan kalmomi kaxan, cikin hikima (Xangambo, 2008:67)

Daga cikin hikimomin magana mawaqin ya yi amfani da karin magana jefi-jefi don qara wa waqarsa armashi da nuna qwarewarsa a harshen Hausa. Misali, a baiti na 10 da na 60 inda ya ce:

10. “*Sarkin yawa dole yakan fi,*
Mai taqama da tarin qarfi,
Yau ba a qara ci mana zarafi,
Mun yi saqar farar tabarma.

60. Kai *ba ka a tsuntsu ba ka a tarko,*
Sakkwato a yanzu ka zama fanko,
Sauran kaxan ka koma a faqo,
Haqqinmu ba batun yafe ma.”

A cikin baitin farko a sama ya yi amfani da karin maganar da ake cewa, “Sarkin yawa ya fi sarkin qarfi”. A baiti na biyun kuwa, ya yi amfani da karin maganar da ake cewa, “Ba ya ga tsuntsu, ba ya ga tarko”. Domin ya nuna cewa gwaninsa yana da jama’a, saboda

haka idan yana taqama da kuxi ne, to jama'a fa ta fi qarfinsa. Sannan kuma dai abokin hamayyar tasa zai yi biyu babu, wato zai rasa mulkin da yake taqama da shi.

4.1.9.2 Amfani da Kalmomi

Aminu Xandago ya yi amfani da kalmomi masu sauqin ganewa. Duk da haka dai, ya yi amfani da aron kalmomi jefi-jefi. Sannan kuma yana yi, yana jejjefa karin harshen Sakkwatanci a cikin waqarsa. Bayan amfani da Karin harshe da mawaqan siyasa ke yin a cikin waqoqinsu, har way au sukan yi amfani da aron kalmomi jefi- jefi domin su nuna dangantakarsu da wannan harshe. Sannan kuma su nuna cewar su ma masu wannan harshen ana tare da su. Wato dai suna yin haka ne domin neman goyon bayansu. Ga misalin wuraren da Ibrahim Xandago ya yi amfani da aron kalmomi:

Tun a baiti na farko (1) Ibrahim Xandago ya yi amfani da salon aron kalmomi inda ya ce:

1. "*Bismillahi Jalla gwanina,*
***Khaliqi** mai dare mai rana,*
Ba ni iko ka gyara shirina,
In yi waqa ga zakin fama".

A wannan baiti kalmar da ya yi amfani da ita, ita ce **khaliqi** wadda ya aro daga Larabci mai nufin mahalicci.

Sannan kuma a baiti na 3 ma, ya yi amfani da kalmomin aro inda ya ce:

3. *" Na yi niyyar in qyanqyashe qwaina,*
*Don **muradi** na nunin qauna,*
Allah Ka qara jin tausaina,

*Yadda waqar ta zan **shane** ma."*

Ya yi amfani da wannan kalmar **muradi** (daga Larabci) domin ya nuna nufi ko buqatarsa.Ya kuma yi amfani da Kalmar **shane** (daga Ingilishi) mai nuna haskawa.

Haka ma a baiti na 6 ya yi amfani da aron kalma inda ya ce :

*6. Wanda ka qin ka ne **gafalalle**,*
Ya kasance baqin wahalalle,
Soko yana ta faman jele,
Ba ya qaunar mu dunga yaba ma.

A nan ya yi amfani da kalmar **gafalalle** (daga Larabci) mai nufi rafkananne.

i. A baiti na 14 ya yi aron Kalmar usuli daga Larabci inda y ace:

14. " kai kwaxo ma- sha ruwa ya yi wanka,
Zahiri gobe za kai hauka,
*Tun da ka qetare **usulinka,***
Ga shi danginka sun bijire ma. »
*A wannan baiti ya yi amfani da kalmar **usuli** nufin tushe ko mafari.*

A baiti na 30 ga abin da ya ce:

30. "Kai za kai mana handin oba,
Ko ka so ko ba kai niyya ba,
Ba sai abin da ranka ya so ba,
Duk jidalin da kai kan nema."

A cikin waxannan baitoci Ibrahim Aminu Xandago ya yi amfani da aron kalmomi a cikin waqarsa kamar haka:

A baiti na 30 ya aro kalmar *handing over* daga Turancin Ingilishi mai nufin miqa mulki.

Haka kuma Ibrahim Xandago ya yi amfani da wasu kalmomi jefi- jefi, waxanda ma'anar su na iya yi wa wani mai karatun wahalar ganewa. Misali, a baiti na baiti na 6 inda ya ce:

6. " wanda ka qin ka ne gafalalle,
Ya kasance baqin wahalalle,
Soko yana ta faman ***jele,***
Ba ya qaunar mu dunga yaba ma.''

A nan mawaqin ya yi amfani da kalmar **jele** mai nufin waxar ko kaiwa –da- komowa.

Sannan kuma a baiti na 26 Xandago ya amfani da kalmar **hauma- hauma** inda ya ce :

26. 'Jam'iyyarmu ta fifita,
Sarkin Yamma yai mana gata,
Sakkwatawa suna kwaxayin ka.
Wancan yana ta ***hauma- hauma****.'*

A nan Xandago ya yi amfani da Kalmar hauma- hauma mai nufin yin maganganu da abubuwa bak ai ba gindi. Ya yi haka ne domin ya daqilar da abokin hamayyar Sarkin Yamma kuma ya nun tozartawa gare shi.

Haka ma a baiti na 64, mawaqin ya yi amfani Kalmar '**yan tsurku** inda ya ce :

64. "Jam'iyya yau tana hannunku
Alhaji Tsalha ba mu da shakku,
Ka ga mai maganin ***'yan tsurku****,*
Jam'iyya ta zame ***gogarma.''***

A nan mawaqin ya yi amfanin da kalmar '**yan tsurku** mai nufin gutsuri- tsoma ko xaukar magana daga wannan a ka iwa wancan. Mawaqin yana nuna cewar duk wasu 'yan tsugunne- tsugunne da 'yan hamayya za su yi, to ya fi qarfin su. Saboda haka kuma,

jam'iyyarsu ta shahara, kuma ta giga. Don haka, Magatakarda zai yi maganin masu qulle-qulle da maganganun gulma. Haka ma a cikin dai baitin (na 64), Xandago ya yi amfani da kalmar gogarma, domin ya kwarzanta Jam'iyyar xan takararsa.

4.1.9.3 Amfani da Karin harshe

Masana sun bayyana karin harshe da tsarin yadda masu amfani da harshe ke yin amfani da shi ta yadda sauran 'yan uwansa za su fahimta ko da kuwa nasu ya bambanta da na sauran (Galadanci da wasu, 1992:48). Dukan harsuna suna da Karin harshe irin nasu. Misali, Turancin Ingilishin Amurka ya bambanta da na Ingila (Skinner, 1979: 8). Haka ma abin yake a Hausa. Domin kuwa, ana samun bambanci a magana daga wuri zuwa wuri. Wannan ya sa ake da Katsinanci da Sakkwatanci da Kananci da Dauranci da Zazzaganci da Bausaci da Guddiranci. (Zulyadaini, 2005: 211).

Don haka, shi ma Xandago a cikin waqasa ya yi amfani da karin harshen sakkwatanci a wasu wurare. Misali, a baiti na 37 da 59 da kuma 73. Ga abin da ya faxa:

ii. A baiti na 37 inda ya ce:

37. "Sakkwatawa kuna da azanci,
Na bar ku yau da alqalanci,
Xan xanku an ka ci wa mutunci,
Ku yi xamara ku sai masa girma.

A nan ya yi amfani da Karin harshen Hausa daya ce "*Xan xanku an ka ci wa mutunci,"* maimakon ya ce Xan xanku *aka* ci wa mutunci.

iii. A baiti na 45 ya yi amfani da kalmar *sure* , maimakon yakuwa.

45. *Ahmad Yarima* babban qyaure,
Mai qin ka ya zame makararre,
Qarshensa zai yi tallar ***sure****,*
Jam'iyya gaba ya faxa xamamma.

iv. A baiti na 59 inda ya ce:

59.Sakkwato mutum ga ne dattijo,
Mulkin Jaha mu kore Ojo,
Za ka koma wa tallar gwanjo,
Tun da ka aje silar da ka girma.

A wannan baiti ya yi amfani da Sakkwatanci day a ce "*Sakkwato mutun ga ne dattijo".*

Maimakon ya ce *wannan mutum*

v. A baiti na 73 inda ya ce:

73. Nasiru Itali Sannu da fama,
Sakkwato kana da qima kai ma,
Mai samarin jiha mai himma,
Gayun jahag ga ba su musa ma."

Ya yi amfani da Karin harshen Sakkwatanci da ya ce "*Gayu <u>jahag ga</u> ba su musa ma*

maimakon ya ce <u>wannan jaha</u>. Da sauransu.

4.1.10 Tsarin Waqar

Wannan waqar tana da jimillar baitoci tamanin-da-bakwai (87). Kuma qwar-huxu ce. Haqiqa mawaqin ya yi amfani da basira, inda yake qulla tunanins a cikin baitoci ta yadda a kowane baiti, yana bayyana tunaninsa yawanci ta amfani da gangara. Wato yakan faro magana a cikin xango, a qare ta a wani xango cikin baiti. Misali, a baiti na biyu (2), inda ya ce:

2. "*Rabbana qara dukkan tsira,*
Gun wanda yaf fi kowa qara,
Xan Abdullahi Baban Zara,
Nai salatinka nai taslima".

4.1.11 Amsa -Amon Waqar

Amsa-Amo yana xaya daga cikin sifar waqa da aka aro daga Larabci. Shi ne yadda sauti ke maimaita kansa a gava ko kalma a cikin waqa. Amsa – Amon ciki, shi ne sautin da yake wanzuwa a qarshen layuka a cikin baiti. Wannan sifa an fi samun ta a cikin waa mai qwar- uku da mai qwar- huxu da mai qwar- biyar (Zulyadaini, 2005: 217). Mawaqin ya yi amfani da amsa-amon ciki da na waje a cikin waqarsa. A qaramin amsa- amo (na ciki) akwai bambanci a tsakanin wasu baitoci: Rabin waqar, wato kimanin baitoci 43, qaramin amsa amon shi ne sautin wasalin "a". Misali, a baiti na farko:

1. "*Bismillahi Jalla gwanin<u>a.</u>*
Khaliqi mai dare mai ran<u>a</u>
Ba ni iko ka gyara shirin<u>a</u>
In yi waqa ga zakin fam<u>a</u>."

Babban amsa-amon waqar kuwa, shi ne "ma" wanda ya tafi bai-xaya tun daga farkon waqar har qarshe (baiti na 1-87). Misali, tun a baiti na farko:

2. "*Bismillahi Jalla gwanina,*
Khaliqi mai dare mai rana,
Ba ni iko ka gyara shirina,
In yi waqa ga zakin fama".

Haka ma, har zuwa baiti na qarshe (na 87), ga abin da mawaqin ya ce:

87. "*A nan za ni dakata in huta,*
Na gode wanmda yai mini mafita,
Yau basira ka qara daxa ta,
Jalla Sarki ina gode ma".

Wani abin sha'awa da wannan binciken ya gano daga wannan waqar, shi ne cewar babun inda aka ambaci sunan wata Jam'iyya. Kai ko ma alamar wata Jam'iyya, ba ma sunanta ba, ba a ji xuriyarta ba tun daga farko har qarshen waqar. Abin da kawai mawaqin ya mayar da kai a cikin waqar, shi ne kushe abokan hamayya da kuma tallata gwaninsa.

4.1.12 Amsa – Amon Karin Waqar "*Adon Gaskiya Ba ya Vata".*

Amsa-amon kari ana samun sa a waqa rubutatta ko ta baka. Wannan shi ne ake samu a masabka ko madira a qarshen kowane baiti (na rubutattar waqa) ko kowane xa (na waqar baka) (Muhammad, 1978:61). Gava muhimmiyar aba ce a wajen kari. Gava ita ce xaya daga cikin furuttan da suka haxu suka yi kalma, wato furuci wanda baqi da wasali suka haifar (Dunfawa, 2003:5).

A cikin wannan waqar, za a duba misalai daga baiti na 1 zuwa na 3 kamar haka:

1. Bismillaji Jalla Gwanina
Khaliqi mai dare da rana
Ba ni iko ka gyara shirina

In yi waqa ga zakin fama

2. *Rabbana qara dukkan tsira,*
Gun wanda yaf fi kowa qara,
XanAbdullah Baban Zara,
Nai salatinka nai taslima

3. *Na yi niyyar in qyanqyashe qwaina,*
Don muradi na nunin qauna,
Allah ka qara jin tausaina,
Yadda waqar ta zan shane ma.

Daga waxannan misalai na baitoci ana iya fahimtar cewar amsa-amon karin waqar ya daidaita a kan hawa da saukar murya a gavovin qarshe na kalmomin. Wato amsa-amon karin, shi ne sama-qasa.

4.2 Salon Waqar " *Yau Nijeriya Riqo Sai Mai Gaskiya*"

A cikin wannan waqar an yi amfani da miqaqqen salo, wanda ya gamsar. Domin kalmomin da aka yi amfani da su, ba masu wahalar da mai saurare ko karanta waqar ba ne. mawaqin ya yi amfani da salailai daban-daban domin isar da saqonsa da kuma nuna qwarewarsa a cikin waqar. Misali, kamar siffantawa da mutuntarwa da sauransu.

4.2.1 Siffantawa a Cikin Waqar

Ibrahim Hayin banki ya yi amfani da gajerar siffantawa a baiti na 32 inda ya ce:

32. "*Ka zama jinjirin wata kai ne ake jira,*
Rana ka riga ka fito ka gagara
Dutse ka wuce bugu koko tokara,
Har mai gatari Muhammad zai juriya".

A nan mawaqin ya siffanta Buhari da jinjirin wata da rana da dutse domin nuna yadda al'umma suka zaqu da ya hau kan karagar mulkin Nijeriya. Da kuma yadda ya gagari kowa, ya kuma bambanta da kowa a wajen halin kirki. Ma'ana, idan ya ce ya zama "Jinjirin wata", wato yana nufin yadda jama'a suka qosa su ga Buhari ya hau mulkin Nijeriya, domin jinjirin wata, musamman na azumi ko sallah, shi ne abin da mutane ke qosawa su gani. Haka da ya ce "rana", watau karin maganar nan ne ta Hausawa: "Idan rana ta fito, tafin hannu ba ya kare ta". A nan yana nuna cancantar Buhari da kuma yadda ya samu karvuwa da farin jini ga jama'a, to don haka, ya gagari kowa.

4.2.2 Kwatancen Fifiko

An yi amfani da kwatancen fifiko a cikin waqar. Misali shi ne a baiti na 13 kamar haka:

13 "*Wanda ya ja da kai Buhari zai sha wuya,*
Domin ka fi wane mai halin 'yan giya,
Mai fuska kamar ana murjin taliya
Kai hango shi ba ya qaunar Nijeriya".

A wannan baiti ga alama anaga cewar mawaqin yana so ne ya kwatanta Buhari da abokin hamayyarsa, domin ya nuna cewar Buhari ya fi cancanta ga shugabancin Nijeriya. Don haka ne, duk wanda ya yi jayayya da Buhari, lallai zai yaba wa aya zaqi.

4.2.3 Abuntarwa

Wannan kamar yadda aka gani a baya, dabara ce ta mayar da mutum ko dabba ko wani abu mai rai zuwa wani abu maras rai. Akan sami irin wannan salon sau da dama a cikin

waqoqin siyasa. Haka kamar sauran mawaqan siyasa, shi ma Ibrahim Hayin Banki, ya yi amfani da irin wannan salo a baiti na 26 inda y ace:

26. ” *Sannu fiya- fiya dab a ka yin murxiya,*
Zo ka kawar da Tanko mai fuskar saniya,
Har da su Babalola mai halin ‘yan giya,
Wanda suke ta vata tsarin Nijeriya. ’’

Ibrahim Yala ya yi amfani da salon jinsintarwa a inda ya abuntar da Buhari ya mayar da shi fiya-fiya domin ya kwatanta qarfinsa a kan na abokan hamayya. Ya kwatanta shi da wannan domin an san sinadari ne da yake gamawa da duk wani qaramin qwaro. A nan ma ya nuna cewar Buhari duk zai gama da abokan hamayya. Wato shi ne maganinsu.

4.2.4 Alamtarwa

Ibrahim Yala Hayin Banki a waqarsa ya yi amfani da irin wannan salon a baiti na 34, inda yake cea:

34.“*Ado Bayero da ke mulkin ‘yan kano,*
Ya ce kai suke buqata faxin kano,
Ka zama xa da ke daxin xanxano,
Sannu Buhari shugaban ‘yan Nijeriya.”

A nan mawaqin ya alamtar da Janar Buhari, domin ya nuna shi ne wanda ake so da gani, kuma ake kwaxayin samun sa a matsayin shugaba. Kamar dai yadda mutum yakan so ya sami wani kayan marmari mai zaqi ko zuma da dai wani abin da yake da zaqi da daxin xanxano. Ya yi haka ne don ya nuna cewar Buhari ne zavin jama’a.

4.2.5 Aron Kalmomi

Duk da cewa dai babu yawan aron kalmomi a cikin waqar, an yi amfani da wannan salo a baiti na 18, inda mawaqin ya ce:

18.“*Har na tsallaka a Legas domin na ji,*
Sun ce ba su bin wanda bai yin agaji,
Na ji suna oshe Buhari mai agaji,
Sare wa taho ka karve Nijeriya”.

A wannan baiti an yi amfani da aron kalmomi daga harshen yarabanci a waxannan kalmomi kamar haka:

Oshe Buhari – mun gode Buhari
Sare wa – zo maza

Wannan baiti na nuna goyon bayan Buhari, a bakin Yarabawa, har suke godiya da buqatar Buhari cikin sauri domin su sami taimakonsa.

4.2.6 Karin Harshe

An yi amfani da karin harshen Sakkwatanci da kananci a baiti na 18 da na 19. Misali a baiti na 18, an yi amfani da Kananci, inda ya ce:

18.“Har na tsallaka a Legas domin na ji,
Sun ce ba su bin wanda bai yin agaji,
Na ji suna oshe Buhari mai agaji
Sare wa taho ka tallafi Nijeriya.”

A cikin wannan baitin Yala ya yi amfani da karin harshen kananci inda ya ce “na ji” maimakon “In ji”.

Haka ma a baiti na 19 an yi amfani da sakkwatanci inda ya ce:

19. “Oyo su da can Ondo sun faxa,

Har Ogun da naz zaka duk sun daxaxa,
Duk sun ce shi Buhari bay a jan faxa,
Shi ne za su zava a nan Nijeriya."

An yi amfani da "naz zaka" Sakkwatanci, maimakon ya ce "na zo", domin ya daidaita karinsa, sannan kuma ya nuna cewar duk mutanen Sakkwato, su ma suna tare da Buhari..

4.2.7 Nahawu

An yi amfani da qa'idojin harshe a cikin wannan waqa. Amma akwai wuraren da aka kauce qa'idar. Misali, a baiti na 19 da na 26. A baiti na 19 yana cewa:

19."*Oyo su da can Ondo sun faxa,*
Har Ogun da naz zaka duk sun daxaxa,
Duk sun ce shi Buhari ba ya jan faxa,
Shi ne za su zava a nan Nijeriya".

A nan ya yi amfani da baitin givin kalmomi cikin jimla inda ya ce:

"Oyo su da can Ondo sun faxa…"

Maimakon (mutanen) Oyo da (na) can Ondo sun faxa. Kalmomin da ke cikin baka su ne givin da aka bari domin dai karin waqarsa ya tafi yadda yake buqatarsa.

Haka ma a baiti na 26 inda ya ce:

26 "*Sannu fiya-fiya da ba ka yin murxiya,*
Zo ka kawar da Tanko mai fuskar saniya,
Har da na Babalola mai halin 'yan giya,
Wanda suke ta vata tsarin Nijeriya".

A nan ya kauce qa'idar nahawu inda ya ce: "*Har da (na) Babalola mai halin 'yan giya."*

Idan aka lura a nan, qari aka samu na kalmar "na" maimakon ya ce:

"*Har da Babalola mai halin 'yan giya".*

Duk wannan na faruwa ne saboda 'yancin waqa. Inda mawaqin kan qara ko ya rage kalma ko ma ya canza mata sifa don cim ma gurinsa waqar ta tafi yadda yake so.

4.2.8 Azancin Magana a Cikin Waqar

Azancin magana a cikin waqa ya haxa da karin magana da kirari da habaici a cikin waqa kamar yadda (Funtua, 2003:117) ya bayyana. Waxannan zantukan hikima kamar yadda (Xangambo, 2008:48) ya bayyana, ana la'akari da su ne don fahimtar tasirinsu da muhimmancinsu a cikin waqar da ake nazari.

Da haka ne za a fahimci cewar waxannan zantukan hikima sun zama ado a cikin waqoqi ba ma na siyasa ba kawai. Don haka ana samun irin waxannan zantuka a cikin waqoqin siyasa, kamar yadda za a ga misalai daga wannan waqar da ake nazari.

4.2.8.1 Karin Magana

Kamar sauran waqoqin siyasa na jamhuriya ta huxu, an yi amfani da karin magana a baiti na 24 inda mawaqin ya ce:

24."Ga zakaran da rabbana Sarki yan nufa,
Dole a qyale maigida ko ko a ranqwafa,
Don haka kar ku ja da shi balle ku zurfafa,
Yau Allah yana a bayan Mai Gaskiya."

Wannan karin maganar nan ce da Hausawa ke cewa: "zakaran da Allah ya nufa da cara, ana muzu ana shaho, sai ya yi". Mawaqin ya yi amfani da hikimarsa ne ya rage wani abu daga cikin karin maganar don karin waqarsa ya tafi yadda yake buqata. Manufar maganar

dai, ita ce, Buhari sai gani, sai hange tsakaninsa da abokan hamayya. Domin kuwa Allah ya riga ya xaukaka shi. Don haka ko dai a bi shi, ko kuma duk wanda ya ja da shi, to a qasa yake.

4.2.8.2 Zambo

Ibrahim Yala hayin Banki ya yi amfani da zambo a cikin waqarsa domin nuna qwarewarsa a harshe. Sannan kuma ya tallata xan takararsa ta hanyar kushe abokin hamayya. Ga misali a cikin waqar a baiti na 13 kamar haka:

13."Wanda ya ja da kai Buhari zai sha wuya,
Domin ka qi wane mai halin 'yan giya,
Mai fuska kamar ana murjin taliya,
Kai! Hango shi ba ya qaunar Nijeriya".

A wannan baitin mawaqin ya yi wa abokin hamayyar Buhari zambo, domin ya kushe shi da munana halittarsa da ya ce "mai fuska kamar ana murjin taliya". Lokaci guda an yi masa ba'a ne tare kuma da habaici da mawaqin ya ce:

"*Ka fi wane mai halin 'yan giya,*
Mai fuska kamar ana murjin taliya".

Abin da wannan ke nunawa, shi ne fifita Buhari a kan Obasanjo.

4.2.9 Tsarin Waqar

Mawaqin a cikin waqar ya tsara baitocinsa ta yadda sun bayyana manufarsa kai tsaye. Waqar gaba xayanta, ta qunshi baituka 43. Kuma an yi ta a kan zubin qwar-huxu. Sai a baitoci guda biyu da suka bauxe wa tsari ko zubin waqar, waxanda suka kasance qwar-uku-uku, maimakon hurhuxu. Waxannan baitocin su ne: baiti na 41 da kuma na 42.

Idan aka lura, a wannan waqar ita ma, wato " *Yau Nijeriya Riqo sai mai Gaskiya,"* ba a mayar da kai a kan Jam'iyya ba. Maimakon haka, an raja'a ne a kan xan takara. Wato waqa ta biyu kuwa, kamar yadda aka gani, wato , Ibrahim Yala Hayin Banki, ambatar sunan Jam'iyya kawai ya yi ta xan takarar da yake tallatawa. Ya ambaci sunan Jam'iyyar a baiti na 12, da kuma alamar Jam'iyyar abokan hamayya ta PDP inda ya ce:

12. "*Ke **lema** baqar daga kin mana yau tsiya,*
Ba kya maganin ruwa duk mun sha wuya,
*Ke **lema** fa mulkinki ba kya gaskiya,*
***ANPP** zo ki tallafi Nijeriya.* ''

Sai kuma a baiti na 37, a nan ma, ambatar sunan Jam'iyya kaewai ya yi ta xan takarar da yake tallatawa, inda y ace:

37. *"Sannu Kabiru Umar Ciyaman **APP**,*
In a riqe da qarfi a yau kai ne ka ci,
Alhaji Sa'idu xan Basawa kai tallafi,
Don na san kana da kishin gaskiya.''

Mawaqin ya yi haka ne domin kuwa babbar manufarsa it ace ya nuna gwanin nasa a idon duniya.

4.2.10 Amsa-Amon Waqar

Qaramin amsa-amon waqar mafi rinjaye, shi ne harafin *"a*" sai kuma babban amsa-amon da ya mamaye waqar gaba xaya shi ne, *'ya"*. Ga misali daga baiti na farko zuwa na uku (1- 3) inda ya ce:

1. "*Allah Khaliqu da yay yo duka duni**ya***
*Mu roqon da za mu yi duka bai xa**ya***
Bai wa Buhari mulkinmu duk Nijeriya,

*Don shi ne muke buqata Mai Gaski**ya.***

2. *salli ala Muhammadu Annabi Shugaba,*
   Mai ceton mu radda kowa ke fargaba,
   Annabi ran qiyama ka sa mu sahun gaba,
   Mun ga Rasulu xan Amina mai gaskiya.

3. *ka zo ka fitar da mu a quncin da muke ciki,*
   Don mun shs wuya a kullum kai farmaki,
Ana satan kuxinmu a yau ba shamaki,
   Ka ji halin da muke ciki Nijeriya."

4.2.11 Amsa-Amon karin waqar "*Yau Nijeriya Riqo Sai Mai Gaskiya".*

A wannjan waqar ta Ibrahim Yala Hayin Banki, za a xauki baitocin kamar haka:

1."*Allah Khaliqi da yay yo duka duniya*
Mu roqon da za mu yi mu xauka bai xaya,
Bai wa Buhari mulkinmu duk Nijeriya
Don shi ne muke buqata mai gaskiya

2.Salli ala Muhammadu Annabi Shugaba
Mai ceton mu radda kowa ke fargaba,
Annabi ran qiyama ka sa mu sahun gaba,
Mun ga Rasulu xan Amina mai gaskiya,

3.Ka zo ka fitar da mu a quncin da muke ciki,
Don mun sha wuya a kullum kai farmaki.
Ana satan kuxinmu a yau ba shamaki
Ka ji halin da muke ciki Nijeriya

A waxannan baitocin a kalmomin qarshe na kowanne layi idan aka lura suna amsa-amon karin sama-qasa, wato a gava xaya sauti na hawa sama, a yayin da gavar qarshe na sauka. A haka karin ya daidaita cikin baitocin waqar.

Gava muhimmiyar aba ce a wajen kari. Gava ita ce xaya daga cikin tarurrukan da suka haxu suka yi kalma, wato furuci wanda baqi da wasali suka haifar (Dunfawa, 2003:5).

4.3 Salon Waqar "*Mu Kasa Mu Tsare Mu Raka*"

Mawaqin ya yi amfani da miqaqqen salo wajen isar da saqon waqar. An yi amfani da taqaitattun kalmomi kuma masu sauqi. Misali, a baiti na biyu (2) ya ce:

2."Maza da mata dangi guna,
Na yi kiran ku xan saurara".

A nan ya yi amfani da kalmar "*dangi*" da ya ce: "*Maza da mata dangi guna…*"

Manufarsa, 'yan'uwana maza da mata. Yataqaita maganar ba tare da ya wahalar da mai saurare ba.

A wannan waqar '*Mu Kasa Mu Tsare Mu Raka*,' ta Mohammed Aminu Musa Dako, a amshin waqar ne kawai ake ambatar sunan Jam'iyyar xan takarar da ake tallatawa, inda yake cewa:

*" **CPC** canji muka nema,*
Mu ba mu yarda da shashanci ba."

Wannan shi ma ya nuna cewar babban burin mawaqin, shi ne ya tallata xan takararsa na Jam'iyyar CPC, wato, Buhari.

4.3.1 Amsa- Amon Waqar

Qaramin amsa amon wannan waqar shi ne harafin "a ," haka ma babban amsa amon. Duk da cewar akwai wuraren da aka sami savanin haka. Misali, a baiti na 4, qaramin amsa amon ya qare da harafin " i, " inda ya ce :

4. 'Ku amsa kiran da nike yi,
Ko ku gane nufin manufata'.

Haka kuma a babban amsa amo, shi ma a baiti na 8, ya qare da harafin 'o', inda ya ce :

'Koway yarda da ikon Allah,
Ga damarmu ta yau ta dawo.'

4.3.2 Amsa-Amon Karin Waqar

Amsa-amon karin wannan waqar za a iya gani daga misalan wasu baitoci a cikin wannan waqar. Saboda haka, za a taqaita a nuna abin da ke faruwa a qarshen gavar kowane layi na baitocin. Misali, a baiti na 1-3 na waqar:

1."CPC Canji muka nema
Mu ba mu yarda da shashanci ba.

2. Maza da mata dangi guna,
Na yi kiran ku, ku xan saurara.

3.Manya da yara dangi guna,
Na yi kiran ku, ku xan saurara."

A baiti na farko, layi na farko kalmar qarshe ta nema yana da amsa-amon kari mai hawa da sauka gavovin qarshe na kalmar (wato sama- qasa). Haka ma abin yake a gavovin qarshe na sauran baitukan. Wato a kalmomin *nema* da *ba guna* da *saurara* da *guna* da *kuma saurara* a gabovin qarshe na baitocin. Wato gavovin farko na kalmomin qarshe suna da amsa-amon kari mai hawa sama, a inda gavar qarshe take sauka qasa (wato sama-qasa).

4.3.3 Tsarin Waqar

An tsara waqar a kan zubin qwar-biyu kuma tana da baiti talatin (30).

Tana da qaramin amsa-amo na sautin harafin "a". misali a baiti na 2 :

Maza da mata dangi guna,
Na yi kiran ku, ku xan saurara.'

Haka ma babban amsa-amon waqar, shi ne harafin "a" . Sai a baiti na 8 da na 13 da 26 da 29, sun qare da wasu sautuka. Misali , a baiti na 8 inda ya ce :

' *Koway yarda da ikon Allah,*
Ga damarmu ta da ta dawo.

Qaramin amsa- amo a cikin baitin ya qare da harafin 'h', shi kuma babban amsa- amo ya qare da harafin 'o.'

4.4 Kammalawa

A wannan babi an yi sharhin waqoqi guda uku da suka haxa da "Waqar Adon Gaskiya", ta jam'iyyar PDP da waqar "Nijeriya Riqo sai Mai Gaskiya" ta jam'iyyar ANPP da kuma waqar "A Kasa A Tsare a Raka", ta jam'iyyar CPC. Dukkansu an xauke su a matsayin misalai daga waqoqin siyasa na jamhuriya ta huxu (4).

Wannan bincike ya nuna cewa waqoqin siyasa cike suke da hikimomi na isar da saqo ga jama'a. Don haka ne an lura akwai qwarewar harshe a cikin irin waxannan waqoqi. Misali, salo da kuma azancin magana kamar karin magana da Habaici da kamance da sauransu. An duba waxannan waqoqi ta fuskar jigo da salo da kuma tsari.

Daga qarshe, abin da aka yi la'akari da shi daga waxannan waqoqi ya haxa da:

i.Dukan waqoqin babu wadda ta mai da hankali a kan yaxa manufa da aqidun jam'iya.

ii. Dukkansu sun raja'a ne ga 'yantakara don nema masu goyon baya da kuma tallata su a zave su.

iii.A waqa ta farko ta "Adon Gaskiya", (PDP) mai baiti 87, ba inda aka ambaci ko da sunan jam'iyya, ballantana yaxa manufarta ko aqidarta.

iv.A waqa ta biyu, "Waqar Nijeriya sai Mai Gaskiya", (ANPP) mai baiti 43, a baiti xaya tak ne aka ambaci sunan jam'iyyar ANPP ta hamayya, sai kuma alamar jam'iyya mai mulki (PDP) da aka ambaci alamarta kawai (lema) duk a baiti na 12.

v.Haka ma a waqa ta uku mai baiti 30, ta "A Kasa a Tsare a Raka", a wajen amshinta ne kawai ake ambaton sunan Jam'iyya (CPC). Ita ma ba tare da bayyana manufa da aqidun jam'iyyar ba.

BABI NA BIYAR: NAXEWA

5.0 Jawabin Kammalawa

Nazari waqa abu ne mai muhimmanci matuqa a fagen nazarin Hausa, saboda irin sauye-sauye da ake samu ta fuskar su kansu waqoqin a rayuwar yau da kullum. A nazari mai taken " salon Tallar Xan Takara A Waqoqin Siyasar Jamhuriya ta Huxu: Nazari A Kan

Wasu Waqoqin Siyasar Jamhuriya Ta Huxu," an yi amfani da misalin waqa daga kowace jam'iyya daga cikin jam'iyyu uku da suka yi fice a qasar Hausa. Waxannan jam'iyyu su ne: PDP da ANPP da kuma CPC. Jam'iyyar PDP, ita ce jam'iyya mai mulki a yayin da ANPP da CPC suke a matsayin Jam'iyyun hamayya.

Binciken tun farko ya yi waiwayen ayyukan da suka gabata masu dangantaka da wannan aiki ta kusa kai tsaye ko kuma mai alaqa da shi. An kuma waiwayi tarihin siyasa a Nijeriya, ma'anarta da ire-irenta da samuwarta. Sannan kuma an bibiyi samuwar waqoqin siyasa da yadda suka sauya salo a jamhuriyya ta huxu (4).

An duba ire-iren jigogin da ake samu a cikin waqoqin siyasa, da kuma misalai daga wasu waqoqin. Haka kuma an duba salo na waqoqin siyasa da yadda masu shirya waqoqin siyasa ke amfani da wannan dabara. Dabaru irin su Kamance da Siffantawa da Jinsirtarwa da dai sauransu. Sannan kuma an yi sharhin waqoqi guda uku; xaya daga kowace jam'iyyu uku da aka ambata a sama (ANPP da CPC da kuma PDP)

Wannan bincike ya qunshi nazari ne a kan wasu waqoqin siyasar Jamhuriya ta huxu (4). Binciken ya duba yadda kakar waqoqin siyasa ta vulla a Jamhuriya ta huxu, wadda har ta kai ga an sami wani salo da ake tallata xan takara ko wasu kevavvu ko xaixaikun 'yan siyasa kacokam a cikin wasu waqoqin, ba tare da mai da kai ga manufofi da aqidun Jam'iyyu da kuma mutanensu ba. Saboda haka, abubuwan da binciken ya gano sun haxa da:

1. A irin waxannan waqoqi an gano cewar waqoqi ne da suke na siyasa, domin suna zuwa ne a qarqashin rumfar wasu jam'iyyun siyasa, waxanda mutanen da ake yi wa waqoqin suke a cikinsu. Sai dai, ba a gina jigogin irin waxannan waqoqi a kan jam'iyyu ko aqidunsu ba. A maimamakon haka, mawaqan na karkata ne ga tallata ko kuma wasa wasu xaixaikun 'yan siyasa ko 'yan takara na waxannan jam'iyyu. An fahimci haka daga waqoqin da aka nazarta, inda ga cewar duka waqoqin da aka nazarta, kowace tana tallata xan takara ne kawai, ba tare da tallata aqidar jam'iyyarsa ba.

2. An kuma fahimci cewa a mafi yawan lokuta a cikin irin waxannan waqoqi, sunayen jam'iyyun ne kawai ake jin xuriyarsu. A wasu lokuta ma, cikin amshin waqoqin ne kawai ake jin xuriyar suna ko ma wasu lokuta alamun jam'iyyun kawai. Abin da ke nuni da cewar an sami sauyi, inda aka samu wani sabon salon a yadda ake gabatar da waqoqin siyasa a Jamhuriya ta Huxu. Hakan kuwa ya bayyana daga waqoqin da aka xauka a matsayin misali a cikin binciken. Idan aka lura, a waqa ta farko, wato *"Waqar Adon Gaskiya,"* ta Ibrahim Aminu Xandago, za a ga cewar kwatakwata babu inda aka ambaci sunan wata Jam'iyyar siyasa, ko ma alamarta. A waqa ta biyu kuwa, kamar yadda aka gani, wato *"Waqar Nijeriya Riqo Sai Mai Gaskiya,"* ta Ibrahim Yala Hayin Banki, ambatar sunan Jam'iyya kawai ya yi ta xan takarar da yake tallatawa.

A waqar '*Mu Kasa Mu Tsare Mu Raka*,' kuwa ta Mohammed Aminu Musa Dako, a amshin waqar ne kawai ake ambatar sunan Jam'iyyar xan takarar da ake tallatawa. Wannan ya nuna cewar babbar damuewarsu ko manufar su a cikin waqoqin nasu, ita ce tallata 'yan takararsu.

3. Sannan kuma binciken ya gano cewar hanya da aka bi ta nazari ta fuskar sigar ayyukan adabi, ta nuna cewar su ma waxannan waqoqi suna amfani da kayan cikin da ake samu a cikin waqa, da ma waqoqin siyasa da suke bayyana manufa da yaxa aqidun siyasa. Wato a waqoqin Jamhuriya ta huxu ma, ana da amfani da salon sarrafa harshe, kamar abubuwan da suka qunshi siffantawa da kwatantawa kirari da zambo da zuga habaici da Karin magana dai sauran makamantansu, domin su cim ma gurinsu na bayyana manufarsu ta xaga mutatanen da suke nuna goyon baya gare su, duniya ta san su, kuma ta amince da su.

Haka kuma, kamar yadda aka gani kowace siyasa ko zamanin siyasa da irin salo da siga da yake xauke ta fuskar waqoqinsa. Don haka, a wannan bincike an gano wasu daga cikin muhimman abubuwa ko siffofi da wannan Jamhuriya da waqoqinta suka qunsa kamar haka:

i. An sami wasu waqoqin siyasa na jamhuriya ta huxu da suka raja'a ne a kan tallata xan takara kawai ba tallata aqidu da manufofin jam'iyya ba. Ke nan, a iya cewa an sami wani sabon salo na yadda ake gabatar da waqoqin

siyasa a wannan jamhuriyya (ta huxu). Savanin waqoqin siyasar jamhuriyoyin da suka gabata waxanda suka rinjaya ga yaxa manufofi da aqidun jam'iyyu. Duk da haka, su ma waxannan waqoqin, za a kira su waqoqin siyasa. Domin kuwa, ana shirya su a qarqashin tutar Jam'iyyu.

ii. Mawaqan kan fito da halayen kirki na xan takara ta hanyar yabo da kuma zuguguta shi ta hanyar zuga da kirari. Haka kuma sukan kushe abokan hamayya da bayyana miyagun halayensu ta hanyar zambo da habaici.

iii. Binciken ya gano cewar mafi yawan mawaqa a wannan Jamhuriya suna raja'a ne ga 'yantakara, maimakon manufofin jam'iyyu da yaxa aqida. Hakan kuwa ta faru ne saboda da son abin duniya da ya mamaye mafi yawan zukatan 'yan Nijeriya.

iv. An kuma gano cewar jamhuriya ta huxu, tana da yawan jam'iyyu fiye da sauran jamhuriyoyi da suka gabata. Wannan ya taimaka an sami wayewa a cikin harkokin siyasa, wanda kuma hakan ya haifar da samuwar waqoqin siyasa masu yawan gaske da suke zuwa da salo da sigogi iri- iri. Misali, akwai masu amfani da salon kayan kixa na zamani da waqoqin bijirewa ga wasu shugabanni da jam'iyyun siyasa da kuma masu tallata xaixaikun 'yan siyasa kamar yadda aka gano a wannan bincike.

v. Tana da tsawon rai, wato qarko fiye da sauran jamhuriyoyi idan an kwatanta ta da sauran zamunnan siyasa.

vi. Akwai raunin aqida a tare da wasu ‘yan siyasar wannan jamhuriya ta huxu, inda wasu ke yin ta saboda kwaxayin dauxar duniya (kuxi) ba don kishin qasa ba.

5.1 Shawarwari

Daga qarshe ana ba da shawara ga manazarta harshen Hausa da su ci gaba da ba da himma a kan nazarin waqoqin siyasa domin su tafi da zamani. Ta haka ne ganin yadda ake da jam’iyyu da yawa kuma ake ta samun ‘yantakara daban-dabam, to za a yi ta samun vullowar waqoqin siyasa da dama. Don haka a taskace su, a kuma nazarce su domin qara inganta harshen Hausa da kuma bunqasa shi a fagen ilimi. Domin ta haka ne za a iya adana ximbin hikimomin da ke qunshe a cikin harshen Hausa, ta yadda har al’ummomin da za su zo, za su ci gajiyar nazarce-nazarcen da aka gabatar a kan waqa. Kuma hakan zai taimaka wajen xorewar qimar harshen da yadda ake amfani da salon harshen ta yadda hikimomin ba za su vace wa ‘yan baya ba.

Haka kuma ta yin nazarin irin waqoqin da za su zo nan gaba, zai iya bad a damar a san irin yadda ake aiwatar da su, da irin bambance- bambancen da aka iya samu ta fuskoki daban- dabam. Misali , ta fuskar jigo da salo da tsari da saurayin hanyoyin nazarin waqa. Ta haka za a iya warware matsaloli da yawa da suka shafi siyasa, ta hanyar tsarkake yanayin waqoqin (watau su kasance ba masu kawo husuma da haddasa gaba ba) a tsakanin al’umma. Wannan zai taimaka ainun wajen kawo cigaban siyasa da ma qasa

baki xaya. Domin sai da zaman lafiya za iya samun kowane irin cigaba. Kuma hanyar nazarin irin waxannan waqoqin ne jama'a za su iya tantance irin mutanen da ya kamata su zava. Domin za su san halayensu da irin abubuwan da suka gabatar na alkhairi da kuma irin qudurorinsu a cikin tallata su da ake yi cikin waqoqin.

5.2 Manazarta

Abdulqadir, D. (1974). *The Poetry, Life and Opinions of Sa'adu Zungur.* Zaria: Northern Nigerian Publishing Company.

Adamu, Y. (2006). "Tasirin Waqoqi Kan Ci Gaban Siyasa A Jamhuriya ta Huxu." Kundin Digiri na Farko, Sakkwato: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Adamu, S.S. (2007). *Nazarin Waqoqin Hausa.* Kano: Samarib Publishers.

Adamu, M.T. Baba Impossible (ed.) (2008, 2009). "Nazari A Kan Waqoqin Siyasa Littafi 1-20." Ayyukan Xaliban Aji Uku, Darasin Dabarun Bincike (Research Methodology). Kano: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero.

Abdullahi, N.U. (2011). " Tarken Waqoqin Adawar Siyasa na Haruna Aliyu Ningi." Kundin Digiri na Biyu. Zariya: Sashen Harsuna da Al'adun Afirka. Jami'ar Ahmadu Bello.

Abdulmumini, S.A. (2009). "Hausar Talla a Rediyo: Tsokaci a Kan Tallar Hana Cin Mutuncin Takardar Kuxin Naira", Himma Journal of Contemporary Hausa Studies, Vol.1 Sashen Harsunan Nijeriya, Katsina Jami'ar Umaru Musa 'Yar'adua.

Abbas, U.A. (2011). "Nazarin Adon Harshe a Wasu Rubutattun Waqoqin Siyasar Jamhuriya ta Uku." Takardar da aka gabatar a taron qara wa juna illimi, Katsina: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Umaru Musa Yar'adua.

Auta, A.L. (1999). "Samuwa Da Havakar Rubutattun Waqoqi" Laccar Xalibai a Kwas mai Lamba Hau 2206, Kano: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero.

Amin, M. L. (2005). "The Tabuka Epic in Hausa Literature: A Case Study of Audu Makaho's Version." Xunxaye Journal of Hausa Studies. Sokoto: Department of Nigerian Languages. Usmanu Xanfodiyo University. Vol. 1, No. 2.

Amin, M. L. (2006). " Reformism as a Theme in Hausa Religio- Political Poetry." Journal of African Cultural Studies, A Paper Presented at the West Africa

Seminar of the Anthropology Department. London University College. Vol. 18, Number 2.

Ajiwa, H.R (1998) "Rubutattun Waqoqin Siyasa a Zamanin Shirin Miqa Mulki na Abacha". Kundin Digiri na Farko, Zaria: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka. Jami'ar Ahmadu Bello.

Bayero, A.Y. 2010 *Salo Asirin Waqa*. Kaduna: Fisbas Media Services.

Bayero, A.Y da Dunfawa, A.A (2010). "Waqar Zamani.," Mujallar Xunxaye, Sakkwato: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Xanfodiyo. Vol. 1, Number 3.

Binta, S.S. (1997). "The Language of Poetry: A Stylistic Study of Selected Poems of Soyinka and Osundare." M.A. Thesis, Kano: Department of English and European Languages, Bayero University.

Bello, B.M.(2007). "Kamanci Da Bambanci Tsakanin Waqar Siyasar Shegiyar Uwa da Waqar Ba Mu Yarda Tazarce Ba Na Haruna Aliyu Ningi." Kundin Digiri na Farko. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya Da Na Afirka. Jami'ar Ahmadu Bello.

Bello, S. and Yusuf, M.M. (edit) (2012) *Popular Participation and Democratization In Nigeria Under the Fourth Republic.* Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited.

Birniwa, H.A. (1987). "Conservatism and Dissent: A Comparative Study on NPC/NPN and NEPU/PRP Hausa Political Verse from Ca. 1946 to 1983." Ph.D Thesis. Department of Nigerian Languages, University of Sokoto.

Birniwa, H.A. (2010). "Matsayin Rubutattun Waqoqin Siyasa Wajen Yaqin Neman Zave: Misalai daga Jamhuriya Ta Xaya da Ta Biyu." Takardar da aka Gabatar a Taron qara wa Juna Sani, Katsina: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Umaru Musa 'Yar'adua.

Birniwa, H.A. (2005).” Tsintar Dame A Kala: Karin Magana A Cikin Waqoqin Siyasa.” Xunxaye Journal of Hausa Studies, Kakkwato: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami’ar Usumanu Xanfodiyo. Volume 1, No.2

Birniwa, H.A. (2013). “Waqoqin Siyasa A Matsayin Gishirin Siyasar Zamani ,” a Cikin Nazarin Hausa, Harshe da Adabi da Al’adu. Taron Qasa na Farko, Kano: Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Bunguxu, Y.A. (1990). “Muhammadu Auwalu Isa Bunguxu da Waqoqinsa.” Kundin Digiri na Farko. Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Sakkwato.

Babanzara, M.H. (1980). “A Critical Study of Specimens of Hausa Political Verse Relating to the 1979 General Elections in Nigeria.” M.A. Thesis. London: SOAS University.

Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero, Kano. 2006.*Waqa a Bakin Mai Ita.* Zariya: Kamfanin Xab’i na Nijeriya ta Arewa.

Xambatta, M. (2010). *Pull of Fate: The Autobiography of Magaji Xambatta.* Zaria: A.B.U. Press Ltd.

Daura, U.Sama. (2004). “Jigon Yabo a Waqoqin Jatau Kamba.” Kundin Digirin Farko. Sakkwato: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami’ar Usmanu Xanfodiyo.

Xalladi, A.L. (2003). “Tallar ‘Yan Siyasa a Gidan Rediyo Nijeriya Kaduna a Jamhuriya ta Huxu,” Kundin Digiri na Farko. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Na Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello.

Daure, B. (2000). *Tuna Baya: Tarihi Da Al’adun Mutanen Nijeriya.* Kaduna: Informat Publishers. Tudun-wada.

Xangulbi, A.R. (2003). “Siyasa a Nijeriya: Gudunmuwar Marubuta Waqoqin Siyasa na Hausa ga Kafa Dimokuraxiyya.” Kundin Digiri na Biyu. Sakkwato: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami’ar Usmanu Xanfodiyo.

Xan'illela, A. (2010). "Rubutattun Waqoqin Siyasa: Nazari a Kan Jihohin Sakkwato da Kebbi da Kuma Zamfara." Kundin Digiri na Biyu. Sakkwato: SaShen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Xiso, A.H. (1997). "Zambo da Yabo a Matsayin Dabarun Jawo Hankali A Rubutattun Waqoqin Siyasa na Hausa. "Kundin Digiri na Biyu. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero.

Dokaji, A. (1978). *Kano Ta Dabo Cigari.* Zariya: Kamfanin Xab'i na Nijeriya ta Arewa.

Xangambo, A. (2008a) *Rabe-Raben Adabin Hausa* (Sabon Tsari). Kano: Amana Publishers Limited.

Xangambo, A. (1981) "Salon Jawo Hankali Cikin Rubutattun Waqoqin Hausa" akardar Da Aka Gabatar a Taron Shekara-Shekara a kan Rubutattun Waqoqin Hausa. Argungu: Hukumar Fasaha da Al'adun Gargajiya, Sakkwato.

Dunfawa, A.A. (2003). *Ma'aunin Waqa.* Sokoto: Garkuwa Publishers.

Xan Hausa, A.M. (2012). *Hausa Mai Dubun Hikima*. Kano: Centuary Research and Publishing Company.

Xangambo, A. (2008b). *Xaurayar Gadon Fexe Waqa* (Sabon Tsari). Zariya: Amana Publishers Limited.

Dailytrust Tuesday 4th March, 2014, p3.

Everyman's Encyclopaedia Vol.10. (1967). Purnell and Sons Ltd, Pauliton (Somerset) and London.

Funtua, A.I (2003). "Waqoqin Siyasa na Hausa A Jamhuriya ta Uku: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu." Kundin Digiri na Biyu. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero.

Furniss, G. (1996). *Poetry, Prose and Popular Culture in Hausa.* London: Edinburgh University Press.

Galadanci, M.J.M. da Wasu (1992). *Hausa Don Qananan Makarantun Sakandare* Littafi na biyu. Ikeja: Longman Nigeria Plc.

Gusau, S.M. (2008). *Dabarun Nazarin Adabin Hausa.* Kano: Benchmark Publishers Ltd.

Gusau, S.M (2008). *Waqoqin Baka a Qasar Hausa*: Yanaye-Yaneyensu da Sigoginsu. Kano: Benchmark Publishers.

Gaya, A.M. (1988). "Tsarin Mulkin Gargajiya Jiya da Yau Musamman a Kano." Kundin Digiri na Biyu. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero.

Gumi, A.M. (1979). *Al-qur'ani Maigirma da kuma Tarjaman Ma'anoninsa zuwa ga Harshen Hausa.* Madina: Wurin da aka Tanada Musamman na Sarki Fahad don Buga Al-qur'ani Maigirma.

Hiskett, M. (1975). "The Development of Sa'adu Zungur's Political Thought from Maraba da Soja, through Arewa Jamhuriya ko Mulukiya to Waqar 'Yanci". *African Language Studies.* Vol./6. London: School of Oriental and African Studies, University of London.

Hiskett, M. (1977). *An Anthology of Hausa Political Verse (Hausa texts edited and annotated*). London: Department of Africa. SOAS.

Ibrahim, G. I. (2009). "Nazari A Kan Waqoqin Jam'iyyar PSP a Kano." Kundin Babbar Diploma a Hausa. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero.

Ibrahim, I.M (2007). "Nazarin Yabo da Zambo a Rubutattun Waqoqi na Siyasa na Haruna Aliyu Ningi", Kundin Digiri na Farko, Kano: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero.

Ibrahim, B.A. (2007). "Fa'idoji Da Illolin Waqoqin Siyasa." Kundin Digiri na Farko. Sakkwato: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Ibrahim, S. (2012). "Harshen Talla a Qasar Hausa". Kundin Digiri na Biyu". Sokkwato: Sashen Harsunan Nijeriya Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Junaidu, I.(1981). *Ciza Ka Busa*. Lagos: Longman Nigeria Plc.

Jaridar "Leadership" (ta Ingilishi) Litinin 21 ga Fabrairu, 2011.

Jaridar DailyTrust ta ranar Juma'a 14 ga Maris, 2014, shafi na 16.

Jaridar Dailytrust ta ranar Litinin 17 ga Maris, 2014.

Kafin Hausa, A.U. (1983). *Jiya da Yau*. Legas: Longman Nigeria Limited.

Klarer, M. (2004). *An Introduction To Literary Studies*. London and Newyork: Routledge, Taylor and Francis Group.

Kuna, M.J. and Malumfashi, I.A (1998). "The Politics of Abuse and the Poetics of Violence in Northern Nigeria, 1946-1966." A Paper Presented at the Aminu Kano 15th Year Memorial Conference on Northern Radicals and their Struggles. African Centre for Political and Social Research. Zaria: Ahmadu Bello University.

Kafin Hausa, A.U. (1983). *Jiya Da Yau.* Longman Nigeria Ltd.

Leon, P.B. (2008). *Political Ideologies; Their Origins and Impact. Ninth Edition.* New Delhi: Asoke K. Ghosh, Prentice- Hall of India, Private Limited.

Leadership Talata 04 ga Fabrairu, 2014, shafi na 5

Leadership Juma'a 13 ga Disamba, 2013, shafi na 7

Mohammad, J.S. (2007). "Tasirin Farfaganda a Tallar 'Yan Siyasa," Kundin Digiri na Farko. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Na Afirka. Jami'ar Ahmadu Bello.

Mohammed, Binta.B. (2007). " Kamanci Da Bambanci Tsakanin Waqar Shegiyar Uwa da Waqar Ba mu Yarda Ta Zarce Ba." Kundin Digiri na Farko. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Na Afirka. Jami'ar Ahmadu Bello.

Mashi, M.B (1986). "Waqoqin Baka na Siyasa: Dalilansu da Tasirinsu ga Rayuwar Hausawa." Kundin Digiri na Biyu. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero.

Malumfashi, I.A. (2009). "Yankan Kunkurun Bala: Nazarin Tashin-Tashina da Samuwar Ayyukan Adabin Hausa." A cikin Mujallar Himma. Katsina: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Umaru Musa Yar'adua.

Muhammad, D.Y. (2003). " Ginuwar Salo A Waqoqin Musulunci na Hausa Daga qarni Na 17 zuwa na 20." Kundin Digiri Na Biyu. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero.

Mukhtar, I. (2004). *Jagoran Nazarin Qagaggun labarai.* Kano: Benchmark Publishers Limited.

Mu'azu, M. (2002). "Adabi Madubin Aqida: Nazarin Arewa Jamhuriya ko Mulukiya da Waqar Jihadin Neman Sawaba na Ahmed muhammad Sa'adu Zungur". Kundin Digiri na Farko. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka. Jami'ar Ahmadu Bello.

Musa, I.I. (2007). "Nazarin Yabo da Zambo a Rubutattun Waqoqi na Siyasa na Haruna Aliyu Ningi." Kundin Digiri na Farko. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero.

Mohammed, B.S.S. (1997). "The Language of Poetry-A Stylistic Study of Selected Poems of Soyinka and of Osundare." M.A. Thesis. Kano: Department of English and European Languages. Bayero University.

Muhammad, D. (ed) (1990). *Hausa Metalanguage.* Vol. 1 Ibadan:University press Ltd.

Muhammad, D. (1978). “Waqa Bahaushiya.” a Cikin Harshe da Adabi da Al’ada. Taron Farko na Qasa da Qasa. Kano: Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya. Jami’ar Bayero.

Ngu, S.M. (2003). *Political and Administrative Development in Some Selected Anglophone African States*. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited.

Nuruddin, I. (2005). *Mu’ujamu Nuruddini Al-Wasid.* Beirut: Darul Kutubi Al-Ilmiyati.

Paden, J.N. (2008). *Faith and Politics in Nigeria: Nigeria as a Pivotal State in the Muslim World.* USA.

Sa’adiyya, O. (Mrs.) (1983). “Style and Theme in the Poems of Mu’azu Haxeja,” M.A Thesis, School of Oriental and African Studies, University of London.

Sa’id, B. (1978). “Salo da Tsarin Rubutacciyar Waqar Hausa ta Qarni na 20 a cikin: Tarin Takardun Taron Farko na Qasa da Qasa a Kan Harshe da Adabi da Al’ada. Kano: Jami’ar Bayero.

Salamatu, B. (2006). “Nazari Kan Waqoqin Bijirewa Na Siyasa.” Kundin Digirin Farko. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da na Afirka. Jami’ar Ahmadu Bello.

Salisu, G. (2011). “Salon Sarrafa Harshe A Waqoqin Aqilu Aliyu.” Kundin Digiri na Uku. Zariya: Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello.

Samira, X. (2010). “Nazari a Kan Waqoqin Siyasa na Abdullahi Stim.” Kundin Digiri na Farko. Sakkwato: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Jami’ar Usmanu Xan Fodiyo.

Sani, S. (2011). *Political Language and Hausa Lexical Expansion*. Kano: Benchmark Publishers Limited.

Shehu, M. (2005). “Nazari A Kan Waqoqin Siyasa ta Auwalu Isa bunguxu”. Takardar Xalibai Qarqashin Jagorancin Malam Muhammad Tahar Adamu. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya. Jamia’ar Bayero.

Shu'aibu, M.(2013). "Tasirin Mazahabobin Adabi Kan Tarken Adabin Hausa." Kundin Digiri Na Uku. Kano: Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Skinner, N. (1979). *A Grammar of Hausa*. Zaria: Northern Nigeria Publishing Company.

Sipikin, A.M. (1971). *Tsofaffin Da Sababbin Waqoqin Mudi Sipikin*. Zaria: Northern Nigeria Publishing company.

The Columbia-Viking Desk Encyclopedia, (1953). New York: The Viking Press, INC. Vol. 2

Tsoho, M. Y. (2002). "Eulogues, The Building Blocks of Hausa Praise Song : A Thematic and Structural Examination." Ph. D Thesis. Zaria: Department of Nigerian and African Languages. Ahmadu Bello University.

Tsoho, M. Y. (1987). " Tarkakken Matanin Waqar Kanzil Azimi ta Aliyu Namangi." Kundin Digiri Na Biyu. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da na Afirka. Jami'ar Ahmadu Bello.

Tsoho, M.Y. (2013). "Adabi da Harkokin Siyasa: Bijirewa a Waqar "*Shegiyar Uwa Mai Kashe 'Ya 'yanta PDP*' ta Haruna Aliyu Ningi". a Cikin Harshe da Adabi da Al'ada. Taron Qasa na Farko. Kano: Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero.

Tijjani, S.A. (2002). "Adon Harshe: Nazarin Kwalliya a Adabin Baka." Kundin Digiri na Farko. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da na Afirka. Jami'ar Ahmadu Bello.

Umaru, A. (2003). *Rigging Ways: The Constitution and the Electoral Process in Nigeria.* Kaduna: Axis Research Agency, Ltd.

William F. Arens da Wasu. (2008). *Contemporary Advertising*. New York: MC Graw - Hill

Weeklytrust Asabar 15 ga Fabrairu, 2014, shafi na 6

Yahaya, I. (2011). “Waqoqin Addini na Siyasa: Nazarin Waqoqin Emmanuel Wise mai Molo.” Kundin Digiri na Biyu. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka. Jami’ar Ahmadu Bello:

Yahaya, A. (2000). “Sharhi a Kan Rubutattun waqoqin PDP,” Kundin Digiri na Farko. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da na Afirka. Jami’ar Ahmadu Bello.

Yahaya, I.Y. (1988). *Hausa A Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa*. Zaria: Kamfanin Xab’i na Nijeriya ta Arewa.

Yahaya, I.Y. (1986). Jagoran Nazarin Hausa. Zaria: Gaskiya Corporation Limited.

Yahaya, A.B. (2001). Salo Asirin Waqa. Kaduna: Fisbas Media Service.

Zulyadaini, B. (2005). “Dialectical Switching in Hausa Poetry: A Case Study of Maraba da Soja Poem,” Xunxaye Journal of Hausa Studies. Sokoto: Department of Nigerian Languages, Usmanu Xan Fodiyo University. Vol. 1 No. 2.

Zainab, I. (2013). “Farfaganda a Waqoqin Fiyano na Hausa.” Kundin Digiri na Biyu. Zariya: Sashen Harsuna da Al’adun Afirka. Jami’ar Ahmadu Bello.

An ziyarci shafin yanar Gizo www.en.wikipedia.org/wiki/Republic a ranar 28- 11- 2011

Mutanen da aka yi Hira da su :

Dr. Aliyu M. Muri, Sashen Tarihi da Harkokin Tsaro na Jami'ar Umaru Musa 'Yar'adua, Katsina, a ranar Litinin 17 ga Nuwamba, 2013 a Sashen Tarihi, UMYUK.

Farfesa Aminu Isiyaku 'Yanxaki, Sashen Tarihi, Jami'ar Usman Xan Fodiyo, Sakkwato, ranar 17 ga Nuwamba, 2013, a Sashen Tarihi, UMYUK.

Alhaji Mamman Magaji (Easy) ranar Alhamis 20 ga Fabrairu, 2014, a gidansa.

Alhaji Ibrahim Aminu Xandago, ranar Juma'a 21 ga Fabrairu, 2014, a Mai Zinariya Multi-Media Sitidiyo, Layin Gidan Adamu Xankura Zoo Road, Kano.

Ibrahim Yala Hayin Banki Kawo Kaduna, ranar Lahadi 23 ga Fabrairu, 2014, a Sitidiyonsa, Yalawa Production Sitidiyo, Liberia Street, Hayin Banki Kawo Kaduna.

Mohammed Aminu Musa Dako, ranar Litinin 24 ga Fabrairu, 2014, a gidansa da ke Dako.

5..3 Rataye

"*Adon Gaskiya Ba Ya Vata*" (PDP) ta Alhaji Ibrahim Aminu Xandago (Kano) 2007

AMSHI:

Sakkwatawa suna bayanka
Sarkin yamma Allah saka ma.

1. Bismillahi Jalla Gwanina,
   Khaliqina mai dare mai rana
   Ba ni iko ka gyara shirina,
   In yi waqa ga zakin fama

2. Rabbana qara dukkan tsira
   Gun wanda yaf fi kowa qara
   Xan Abdullah Baban Zara
   Nai salatinka nai taslima

3. Na yi niyyar in qyanqyashe qwaina

Don muradi na nunin qauna
Allah Ka qara jin tausaina
Yadda waqar ta zan shane ma

4. Allonmu ya cike da rubutu
Saura kaxan mu fara karatu
O'o ko za ya hau sambatu
Za ya koma kwatancen kurma.

5. Mai kare maza ka kama karenka
Na ga zaki yana sausaka
Sakkwatawa suna bayanka
Baba Allah ya yarda ka kama

6. Wanda ka qin ka ne gafalalle
Ya kasance baqin wahalalle
Soko yana ta faman jele
Ba ya qaunar mu dunga yaba ma.

7. Na ji qauye ana begenka
Ko'ina yau ana ta yaba ka
An tabbatar da babu kamarka
Har da yaranmu sun gurje ma

8. Sakkwatawa ku rungume xanku
Mai juriyar da zai goya ku
Alhaji Aliyu bai qyamar ku
Ga abin bi da babu nadama

9. Sarkin Yamma kai muka zava
Mulkin jaharmu ko za ka karva
Albishir har mutanen Rava
Kai suke so su sami salama

10. Sarkin yawa dole yakan fi
Mai taqama da tarin qarfi
Yau ba a qara ci mana zarafi
Mun yi saqar farar tabarma

11. Mulki qwarai abin sha'awa ne
Samunsa ko nufin Allah ne
Tarin yawan kuxi shirme ne
Mu ga Allah kawai muka nema

12. Ba mu da qarfi babu dabara
Ga magauta muna shan sara
Su taqamarsu sun aje naira
Sun fi qarfin bixar alfarma

13. Jam'iyata da tai mini riga
Babu hujjar in qi ta in zaga
Ban barin jam'iyya mai siga
In fita in kama qarma-qarma

14. Kai kwaxo ma-sha ruwa ya yi wanka
Zahiri gobe za kai hauka
Tun da ka qetare usulinka
Ga shi danginka sun bijire ma

15. Mai ganin sai da kai za a iya
Qaryarka o'o ta sha qarya
Yau da Allah kake jayayya
Yin xagawarka ta jawo ma

16. Shi mulki Ilahu ke bayarwa
Wanda Ya nufa yake miqawa
In Ya so ba ka ba a tarewa

Wane mutum ya sa a hana ma.

17. Mai tunanin ba za mu iya ba
Ban san a inda kai ka qware ba
Ba kwalliya ka wa Allah ba
Mulkinsa ne ya xan gutsura ma

18. Wa za ka yi wa burgar wofi
Rabbu shi ke da dukkan qarfi
Sakkwato wuqarka ta rasa kaifi
Ba mu tsoronkla don mu gaya ma.

19. Allah kaxai ka ba da abinai
Xandago tun tuni na fuskanci
Shi ke mai da mutum ma'azurci
In yai ka babu mai canza ma.

20. Na qi in bi ka don ka qi ni
Ba ka da kuxin da za ka saye ni
Mai mutuncin ga shi yaj ja ni
Yau ina nan ga sarkin yamma

21. Shi in ka je gun sa bai maka fara'a
Yaya za ai nai maka xa'a
Yau rundunarka na ce a'a
Na bi wannan da kai ke qyama

22. Ya fi ka boko yai Arabiya
Ga shi sannan yana tuna baya
Mai hankali marar jayayya
Daure Ilahu zai saka ma.

23. Qoquwar qi ka sa a kashe ni
Na sani Jalla zai kare ni

Ko za ka sa a yau a dafa ni
Ban barin Ali zakin fama.

24. Da ma da ni da kai ta qare
Tun tuni na gane ba ma tare
Kwanon tuwonmu tuni ka shure
Ka daina ba mu ba ma nema.

25. Ba bara ce sana'ata ba
Ban yo kama da mai roqo ba
Rayuwata ba tai cikas ba
Na iya rubutu hauni da dama.

26. Jam'iyyarmu ta fifita
Sarkin yamma yai mata gata
Sakkwatawa suna kwaxayinta
Wancan yana ta hauma-hauma.

27. Qwace goruba hannun kuturu
Ba wuya babu sai an taru
'Yan'uwa ta riga ta faru
Kitifinmu zai kasantu a noma.

28. Jirginmu ya riga yai lodi
Yai kayan turaren wardi
Yanzu mu ke da xaurin gindi
Kai da danginka ta rikice ma.

29. Shi kama damisa sa'a ne
Wasa da ita rashin kunya ne
Tsokanar Ali ko haxari ne
Ka yi tilas in jajanta ma.

30. Kai za kai mana handin oba

Ko ka so ko ba kai niyya ba
Ba sai abin da ranka ya so ba
Duk jidalin da kai kan nema.

31. Wankan wuta guda ba qari
Mun gane masu yi mana sharri
Motarku dole sai kun turi
Tun da muka gane mai mana gulma.

32. Ga alqunuta da la'ilafi
Za mui ta yin su don rage zafi
O'o sai mun rage maka kaifi
Kafin tuwon da za mu varar ma.

33. Jama'a ku ji ni ga wani zance
Yanzu zan fara ba da kwatance
Mulki ya sa shi har ya ximauce
Ya mance haka a kai masa shi ma

34. Ka mance kai da Malam Yahaya
Abdulkarimu xan tuna baya
Haka nan kukai Allahu ya juya
Kai martani ga shi mu tuna ma.

35. Yau babu tantama tarihi
Maimaita kansa zai wallahi
Bar maza gobe ka tuba ga shehi
Kan kekenka ya koma qwama.

36. Yau ba mu qara qyale baqo
Ya shigo gari da babban qoqo
Ya tarqwashe ya bi mu a miqo
Ga nasiharmu nan gwagwama.

37. Sakkwatawa kuna da azanci
Na bar ku yau da alqalanci
Dan xanku an ka ci wa mutunci
Ku yi xammara ku sai masa girma.

38. Sakkwato ku zo ku yi masa gata
Don ku fid da mu qangin bauta
Yai biyayyar da babu irinta
Ba yau ba har a da can-can ma

39. Ina ka ga qadangare bi-bango?
Na ga an ba shi sabon bargo
Ka kusa ka fara kwanan shago
Yau ga tsiyarka ta koma ma

40. Sau biyu ana yi mini alqawari
An ba ni Makka an mini kuri
Na cancanta a ba ni da fari
Sai a Zamfara na san alfarma

41. Sau uku Yarima na ban Makka
Ahmed Sani muna gai da ka
Gwamna mai san sanin albarka
Babu gwamnan da yai ka a girma

42. Mai ilimi yake jan gora
Harka ta zama da kyau na lura
Ahmed Sani yarima Bakura
Ya goya nasa ba wata qyama

43. Aiki na hankali ga Yarima
Zo Baba goya sarkin yamma

Ahmed a taimaka masa shi ma
Sakkwato mu yada rigar tsumma

44. Tauraruwarka ke haskawa
Ahmed Yarima ka dushe kowa
Ba a zarta ka, ba a musa ma

45. Ahmad yarima babban qyaure
Mai qin ka ya zame makararre
Qarshensa zai yi tallar sure
Jam'iyya gaba ya faxa xamamma

46. Dole waqar mu sanya matasa
Tun da su ka iya xaukar fansa
Tu tauzan Sabir ba wasa
Kowat tava ku kui bambarma.

47. Ku matasa ku bar jin tsoro
Zaven da za a je nai horo
Ran da za ai ku rarraba goro
Ba gudu babu tsoron fama

48. Mai taqama da ikon Allah
Wallahi sai da nai ma talla
Yau ga shi ka zame mana fitila
Tun da qaunarka ta kankama

49. Kaska tana da haushin kifi
Sarkin yamma ya haxa qarfi
Dangi mu qara yi masa tafi
Tun da hauyarsa ta zama galma

50. Sarkin yamma albishirinka

Sakkwatawa suna bayanka
Sun kasance suna ra'ayinka
Sun yada hauni sun riqe dama

51. Sarkin yamma kar ka ji komai
Yau a gonarka ka haxa dammai
Ka buge mai sifar qanqarmai
Wanda bai bai wa kowa girma

52. Ga gajimare mai rufe hadari
Ya lulluve dukan taurari
'Yan adawa ku bar mana kuri
Rundunar mai dabo ta suma

53. Mai arziqin siyasa ga shi
Xa da ba ya hushi bai qyashi
Ya yi fara'a ya yi maka toshi
Har ku ci abinci tare da shi ma.

54. Sakkwato a yanzu sun lamunce
Sarkin yamma zo ka kasance
Ba batun ai ta dogon zance
Sun amince ka kore kunama

55. A gunka Allah munke daxa roqo
Mun durqusa da babban qoqo
Hannunmu sa ya koma maiqo
Al'umma bana su samu makoma

56. Allahu mai cikakken iko
Dubi zakaranmu ya haxa zanko
Ya Rabbi qara qarin qarko
Sarkin yamma in masa dama

57. Tu tauzan sabin ta doso
Sarkin yamma kowa ke so
Kai kaxai bana ake wasoso
Quri'armu dukka za mu saka ma

58. Sakkwatawa ku bar tababa
Ali wallahi shi ne a gaba
Dole maqiyinka sai ya tuba
In ya qi ya je ya taka kunama

59. Sakkwato mutum ga ne dattijo
Mulkin jaha mu kore Ojo
Za ku koma wa tallar gwanjo
Tun da ka aje silar da ka girma

60. Kai ba ka a tsuntsu ba ka a tarko
Sakkwato a yanzu ka zama fanko
Sauran kaxan ka koma a faqo
Haqqinmu ba batun yafe ma

61. Qarya fure take na gane
Bunne-bunnenku mun tottone
Tsarinku yau shirin banza ne
Mun laqance ku ta kwave ma

62. Yanzu zan zo da baitocina
Na masoya da ke gwada qauna
Su suke tallafa wa zamana
Ba ni yunwa bare nai rama

63. Shugaban jam'iyya Haji Tsalha
Yaqi da ku abin ba arha

Babanku shi ya qwallanta jaha
Sidi Mamman mafi alfarma

64. Jam'iyya yau tana hannunku
Alhaji Tsalha ba mu da shakku
Ka ga mai maganin 'yan tsurku
Jam'iyya ta zame gogarma

65. Kun ji baitin sahabi Isah
Nai jinjina ga gagara gasa
Nawa maqiyanka kai masu nisa
Ka gagare su ba su iya ma

66. Alhaji mai mai Nasiru Wurno
Taso mu toshe ramin gwano
Qulle-qullenka dum mun gano
Wandonsa yau ciki da kunama

67. Abdullahi Sipikin sannu
Tsarinmu kai ka tsone idanu
An yi binnenka ka qi ka binnu
Allahu shi yake kama ma

68. Gaisuwa mai yawa Xangoggo
Mugun madambaci kake Shago
Sakkwato da kai nake yin
Babu na biyunka na shaida ma

69. Xangoggo ke sanar da zuwana
Shi yake ba ni xakin kwana
Kullum na zo ya zo shi ya zauna
Baqo ya san nishaxi shi ma.

70. Mukhtari assalamu alaikum

Maigona za mu yo takenka
Jarumi ne da ba ya shakka
In ka ja dole ne a sakar ma.

71. Allah ya qara xaukaka qadari
Mukhtari mai dubun alkhairi
Maigona kai nake wa kirari
Baitin yabo nake qara ma

72. Ahmad Aliyu ban baiti ba
Ban gane duniyar shagali ba
Ban san zuma akwai zaqi ba
Da nai rashin dawo mai girma

73. Nasiru Itali sannu da fama
Sakkwato kana da qima kai ma
Mai samarin jiha mai himma
Gayu jahag ga ba su musa ma

74. In ka ce hauni sai sui hauni
In ka ce dama ba su aruni
Nasiru Hali mai zamani
Sannu jigo na sarkin Yamma

75. Yau sakkwato abin faharina
Alhaji Dodo kana rayina
Kai na zava na bai wa amana
Na san ka ba ka gutsiri da tsoma

76. Yau ga Baba Ata ya gane
Wasu sirrukan da shi aka binne
Daure ka kai mu Baba mu tone
Da guda-guda mu samu makama

77. Alhaji Uban Dawaki karimi
Tsarinka na daxa mini qaimi
Na arziqi da yau nas sami
Sunanka har nake rera ma.

78. Ga gaisuwar Abu Dankure
Jam'iyyarmu ba ya da bare
In ka je da matsala ta qare
Je gano Din zai sauke ma

79. Alhaji Ma'azu Zabira ga ni
Zazzavin sonku ya kama ni
Mai yunqurin ya sa a hani bin ku
Zai sha wuya zai fama

80. Waqar ba za ta je qarshe ba
In Abu NEPA bai bijiro ba
Da dole sai in ce na tuba
Tilas in bixi zaren saqa ma

81. Muhammadu kaka ga baitinka
Waqarmu dole ne in saka ka
Zahiri na yaba da halinka
Ga salihi da ba ya huguma

82. Hajiya Hafsatu Ibrahimu
Taso bikin zuwa ya samu
Saura kaxan mu sha shagalinmu
Kar ki bi makaryaciyar roroma

83. Hajiya Fatima 'yar Kangiwa
Mai qin Ubanmu ya zama wawa
Shashasha yake xan baubawa
Babarsa na kira ta qazama

84. Shugaba mai matasan mata
Hauwa'u zan yi wa baitin ga
Da zan daxi a qarin mata
Da sai in zo ki ba ni Zabarma

85. Sunan mai waqa ga shi
Ibrahim nake ba na qyashi
Baban Humaira 'ya mai goshi
'Yar qanena xiya ga halima

86. Sunan mai waqa ga shi
Ibrahim nake ba na qyashi
Baban Humaira 'ya mai goshi
'Yar qanena xiya ga halima
87. A nan za ni dakata in huta
Na gode wanda Yai mini mafita
Yau basira Ka qara daxa ta
Jalla Sarki ina gode ma.

Waqar "*Yau Nijeriya Riqo Sai Mai Gaskiya*" (ANPP) ta Ibrahim Yala Hayin Banki Kawo Kaduna

AMSHI:

Yau Nijeriya riqo sai Mai Gaskiya
Sannu Buhari kai muke so Nijeriya

1. Allah khaliqu da yay yo duka duniya,
   Mu roqon da za mu yi mu duka bai xaya
   Bai wa Buhari mulkinmu duk Nijeriya

Don shi ne muke buqata Mai Gaskiya

2. Salli ala Muhammadu Annabi shugaba
Mai ceton mu radda kowa ke fargaba
Annabi ran qiyama ka sa mu sahun gaba
Mun ga Rasulu xan Amina Mai Gaskiya

3. Ka zo ka fitar da mu a quncin da muke ciki
Don mun sha wuya a kullum kai farmaki
Ana satan kuxinmu a yau ba shamaki
Ka ji halin da muke ciki Nijeriya

4. Tanko da Babalola suna ta halin tsiya
Mu da kuxinmu ga shi duk an mana murxiya
Shi yas sa muke bixa yau Mai Gaskiya
Wanda idan ya zo, za ya gyara Nijeriya

5. Allah wadan ku tun da ba kwa qaunan mu mu
Tun da kuna ta mulkinku ba ku kula da mu
Don Allah Buhari mu zo ka fitar da mu
Yau kai ne muke so a nan Nijeriya

6. Ni na san ka tun kana mulkin gaskiya
Kun ga a lokacin Buhari bai danniya
Duk ya kau da wanda ke halin murxiya
Sannu Buhari kai muke so Nijeriya

7. Sanda ya karvi mulki Buhari a nan qasar
Duk ya tadda an cinye kome nan qasar
Sai yag gyara kome da ke a cikin qasar
To me zai hana mu so ka a Nijeriya

8. Kun ga a lokacin yaq qi bashin Ingila
   Har da Amerika masu halin baxila
   IMF ya ce ba ya so don mattsala
   Mun gode Buhari mai kishn gaskiya

9. Ya kaudar da ‘yan ta’addar da suke qasa
   Masu kuxin da ba su zakka sun bar qasa
   Kun ji a lokacin tattali ya bunqasa
   Har a qasarmu mun kasance ba ma tsiya

10. Mu wallahi lokacin ba ma yin tsiya
    Tun da akwai Buhari mai halin gaskiya
    Mun ci abinci har da nama ba sa wuya
    Kun ji a lokacin Buhari Mai Gaskiya

11. Wancan lokacin farar hula sun gudu
    Domin sun yi varna dole su zan gudu
    Yanzu idan ka hau dole wancan nag gudun
    Zai tsere ya bar qasai don bai gaskiya

12. Ke lema baqar daga kin mana yau tsiya
    Ba kya maganin ruwa duk mun sha wuya
    Ke lema fa mulkinki ba kya gaskiya
    ANPP zo ki tallafi Nijeriya

13. Wanda ya ja da kai Buhari zai sha wuya
    Domin ka fi wane mai halin ‘yan giya
    Mai fuska kamar ana murjin taliya
    Kai! Hango shi ba ya qaunar Nijeriya.

14. Lallai Daura kin yi xa wanda yake da kyau
    Wanda idan na gan shi ni ba na zudda yau
    Ku jama’a ina kira sai ku riqe da kyau

Sannu Buhari shugaban ‘yan Nijeriya

15. Ka ji mutan Kano Kaduna har Katsina
Ga na Jigawa har Borno duk sun jinjina
Sakkwato Kebbi zamfara duk sun jinjina
Sun ce yanzu ne qasar za ai gaskiya

16. Yobe da Bauchi har da Gombe sun sallama
Har Adamawa ‘yan Taraba ba tantama
Su Binuwe Pilato suna yin sallama
Sun ce sai Buhari mai mulkin gaskiya
17. Na je Neja Kogi Kwara sun sallama
Sun ce su dai kai Buhari sai lalama
Su ‘yan Lafiya batunsu ba tantama
Za su bi shugaba Buhari Nijeriya.

18. Har na tsallaka a Legas domin na ji
Sun ce ba su bin wanda bai yin agaji
Na ji suna Oshe Buhari mai agaji
Sare wa taho ka karve Nijeriya.

19. Oyo su da can Ondo sun faxa
Har Ogun da naz zaka duk sun daxaxa
Duk sun ce shi Buhari ba ya jan faxa
Shi ne za su zava a nan Nijeriya

20. Har Inugu da Imo su ma sun ambata
Kun ji Anambara da su za a yi karin batta
Sun ce za su bi Buhari don cancanta
Sannu Buhari shugaban ‘yan Nijeriya

21. Kun ji qasarmu ta haxe sai Mai Gaskiya
Mun haxa kai qasarmu yau duk Nijeriya
Hausawa Igbo da Yarabawa mun tsaya

Mun ce sai Buhari mu duka baki xaya

22. PTF da kar riqe ai duka mun gani
Kai ciki da gaskiya ai ni na gani
Asibitinmu ko'ina mun san magani
Hanyoyinmu sun yi kyau duk Nijeriya

23. Don haka zo na ja mu don kai ne ja-gaba
Mu a qasarmu kai muke so yau shugaba
In ka riqe Buhari mu ba ma fargaba
Zo ka riqe mu kar mu kauce daga gaskiya

24. Ga zakaran da Rabbana sarki yan nufa
Dole a qyale maigida ko ko a ranqwafa
Don haka kar ku ja da shi balle ku zurfafa
Yau Allah yana a bayan Mai Gaskiya

25. Zan yi kiranku Rivers Patakwal 'yan'uwa
Kar mu bari a cuce mu da tsarin rantsuwa
Don na tabbata a da ba mu da damuwa
Yanzu ko ga Buhari shi ne bai danniya
26. Sannu fiya-fiya da ba ka yin murxiya
Zo ka kawar da Tanko mai fuskar saniya
Har da na Babalola mai halin 'yan giya
Wanda suke ta vata tsarin Nijeriya

27. Kun ga halin siyasarmu mun koma bara
Don haka nai kiran mutane kui hattara
Kan zancen da nay yi walla ba na qirqira
Sai mu zage mu zavi mai kishin gaskiya

28. Da a qasarmu babu yunwa in kun tuna
Sai kuna abinci da ga shi a ko'ina
Babu faxa a lokacin in har kun tuna

Yanzu idan ka gan mu ko duk mun sha wuya

29. Ku da kuke ta sukan Buhari ubanqasa
Ku ne kuka kwashe fetur da kuxin qasa
Don tsabar rashin mutuncinku cikin qasa
Har ma dukiyar marayu kun murxiya

30. Allah wadan ku masu halin salmaniya
Wannan xan baqin da qira ta ‘yan giya
Tinqaho yake yana halin danniya
Mugun in ka gan shi ka san bai gaskiya

31. Kun cuce mu da da yanzun mun ankare
Kar ku sake ku zo wurinmu ba ma tare
Dan na san ka kai na yamma mai halin kare
Mun riqe mu Buhari don shi ne Mai Gaskiya

32. Ka zama Jinjirin wata kai ne ake jira
Rana ka riga ka fito ka gagara
Dutse ka wuce bugu koko tokara
Har mai gatari Muhammad zai juriya

33. Ka ji Wada fa Nas yana son ka da shugaba
Mai Katsina Kabir yana son ka da shugaba
Har da na Daura Bashir shi ma ya yaba
Sun ce zo ka yi ka gyara shirin gaskiya

34. Ado Bayero da ke mulkin ‘yan Kano
Ya ce kai suke buqata faxin Kano
Ka zama xa da ke da daxin xanxano
Sannu Buhari shugaban ‘yan Nijeriya

35. Rabi’u Kansilan Garo shi ma ya yaba
Abdullahi Gwarzo wannan bai fargaba

Har da Litil Aminu shi ma ya yaba
Sun ce za su bi ka don tsarin gaskiya

36. Ka ga Yarima can Zamfara shi ya yaba x2
Har da Bukar Abba Yobe shi ma ya yaba
Sun ce zo ka tallafi Nijeriya

37. Sannu Kabiru Umar Ciyaman APP
In a riqe da qarfi a yau kai ne kaci
Alhaji Sa'idu xan Basawa kai tallafi
Don na san kana da kishin gaskiya

38. Mamman Daura ya faxi kai ne shugaba
Har Muntari zango yana ce kai gaba
Har da Lawwali bawa da ba ya yin gaba
Har da Minista Sani mai kishin gaskiya

39. Sannu iya Bayis Mashal Mukhtar xan'uwa
Abdurrahmani xan Mallam garkuwa
Har Muhtari Shehu koko na Faskari
Duk sun ce ka zo ka tallafi Nijeriya

40. Yakubu Lere sannu mai halin gaskiya
Na sake Abdul Qwaya da ba ya danniya
Xan da yake a Malali bai yin danniya
Har Usman Tabara ya ce zai juriya
Ga Jugunu yana ta kishin Mai Gaskiya

41. Har 'yan Auwulu Fati ta ce ta yaba
Har 'yan unguwar Rimi ba mu da fargaba
Har da Tabawa Inuwa ba ta da danniya

42. Har da Bala Iyan Tama su ma sun yaba
Ali Baba shi ma a yau bai fargaba

Shi ma zai cika yana kishin gaskiya

43. Ni zan dakata a nan sai kuma nan gaba
Don waqa a kan Buhari ban fargaba
Ni Yala na shirya waqar ta shugaba
Ni ne xan hayin banki mai son gaskiya

Waqar "*Mu Kasa Mu Tsare Mu Raka*" (CPC) ta Mohammed Aminu Musa Dako.

Assalamu alaikum
Da fari zan yo salatina
Sallu alaika nabiyyina
Xan Aminatu mai tsira

Ya ku 'yan'uwa 'yan Nijeriya

Ku saurari wannan waqar

Wadda ni Mohammed Mohammed Aminu Musa Dako

Giwa Local Government Kaduna State

Zan yi a qarqashin maigirma Muhammadu Buhari

Shugaban qasa na Jam'iyyar CPC

Mai taken Mu Kasa mu tsare mu Raka

Mu Jira a qidaya xaii xai

Ta Jam'iyyar CPC Canji!

CPC Canji!

Canji in sha Allah

Canji in sha Allah

Nijeriya, sai Buhari!

Nijeriya, sai Buhari!

CPC canji muka nema,

Mu ba mu yarda da shushanci ba.

Amshi: CPC Canji muka nema

Mu ba mu yarda da shashanci ba.

Amshi: CPC Canji muka nema,
Mu ba mu yarda da shashanci ba.

1. CPC Canji muka nema,
   Mu ba mu yarda da shashanci ba.

2. Mazaa da mata dangii guunaa,
   Na yi kiran ku, ku xan saurara

3. Manya da yara dangi guna,
   Na yi kiran ku ku xan saurara

4. Ku amsa kiran da nike yi,
   Ko ku gane nufin manufata
5. Ku daina yawan sa-in-saa,
   Ko kui gane nufin manufata

6. Ku zoo mu rufa mai baayaa,
   Kun ga ya kai mu tudun-mun-tsira.

7. Ku zo mu riqe kata-maqui,
   Ya kai mu tudun-mun-tsira

8. Koway yarda da ikon Allah,
   Ga damarmu ta da ta dawo.

9. Don bai yarda da cin hanci ba,
   Kuma bai yarda da shashanci ba.

10. Ku zo mu riqe kata-maqui,
    Kun ga ya kai mu tudun-mun-tsira.

11. Don bai yarda da zalunci ba,
    Kuma bai yarda da makirci ba.

12. Ku zo mu riqe kata-maqui,
    Kar mu bari ta vare manufata.

13. Watau mu kasa mu tsare mu raka
    Mu jira a qirga xaixai.

14. Ga damar samun manufata,
    Kar mu bari ta vare manufata.

15. Ya Allahu ka yaxa nufin manufata
    Don koowaa ya zan gaanee ta.

16. A yanzu cikin gaggaawaa,
    Ai baa maa samun wata dama

17. Zan yi kiraa ga mutanen kirki
    Yaa Allahu ka saa su fahimta.

18. Yaa Mallam maigirma guunaa
    Naa yi kira a gare ka do Allah.

19. Nemi janar ku haxe manufata,
    Ko ku kai mu tudun-mun-tsira.

20. Haxaa da Ribaaxo na birnin Yoola,
    Neemi Janar mu haxe manufata.

21. Gabas da yamma kudu da arewa
    Na yi kiran ku, ku zan amsawa.

22. In har kun ji kiran kun amsa,
Kar ku kafe baa don gyara ba.

23. In har kun ji kiran kun amsa,
Too kun kai mu tudun-mun-tsira.

24. In kun qi amsa kiran manufaata,
To asarar quri'a ce zallaa.

25. In kun qi amsa kiran manufaata,
To asarar quri'a ce zalla

26. In kun amsa kiran manufata,
Duw wannan varaka ai ta kau.

27. Baba Buhari kana burge ni,
Duw wannan aikin sai dai kai.

28. Ga wata aya za ni karanta,
Ko wa yag gaji, bai saba ba.

29. To a nan ne zan saurara,
Sai wata raanaa in mun sadu

30. CPC Canji muka nema,
Mu ba mu yarda da shashanci ba.

CPC Canji muka nema,
Mu ba mu yarda da shashanci ba.

Ratayen sunayen jam'iyyun siyasar Jamhuriya ta huxu da ake da su daga shekara ta 2010 har zuwa zaven shekara ta 2011:

1. ACCORD
2. AA – Action Alliance
3. CAN –Action Congress of Nigeria
4. APN –Action Party of Nigeria
5. ACD- Advanced Congress of Democrats
6. ADC –African Democratic Congress
7. ALP – African Liberation Party.
8. APS – African Political System
9. ARP – African Renaissance Party
10. ANPP- All Nigeria Peoples Party
11. APGA- All Progressives Gand Alliance
12. AD - Alliance for Democracy
13. ACPN- Allied Congress Party of Nigeria
14. BNPP- Better Nigeria Progressive Party
15. CAP - Change AdvocacyParty
16. CPP- Citicens Popular Party
17. CPN - Community Party of Nigeria
18. CDC – Congress for Democratic Change
19. CPC – Congress for Progessive Change
20. DA - Democratic Alternative
21. DFPF- Democratic Front for Peoples Federation
22. DPA – Democratic Peoples Alliance
23. DPP- Democratic Peoples Party
24. FPN- Freedom Party of Nigeria
25. FRESH- Fresh Democratic Party
26. HOPE- Hope Democratic Party
27. JP- Justice Party

28. KOWA- Kowa Party
29. LP – Lebour Party
30. LDPN - Liberal Democratic Party
31. MMN- Masses Movement of Nigeria
32. MPPP – Mega Progressive Peoples Party
33. MDJ - Movement for Democracy and Justice
34. MRDD- Movement for the Restoration and Defence of Democracy
35. NAC- National Action Council
36. NAP – Nigeria Advance Party
37. NEPP- Nigeria Elements Progressive Party
38. NCP- National Conscience Party
39. NDLP- National Democratic Liberty Party
40. NDP- National Democratic Party
41. NMDP- National Majority Democratic Party
42. NMPP- National Movement of Progressive Party
43. NRP- National Reformation Party
44. NSDP – National Solidarity Democratic Party
45. NTP – National Transformation Party
46. NUP- National Unity Party
47. ND- New Democrats
48. NNPP- New Nigeria Peoples Party
49. NPC- Nigeria Peoples Congress
50. PDC- People for Democratic Change
51. PPN – Peoples Party of Nigeria
52. PMP – Peoples Mandate Party
53. PPP- Peoples Progressive Party
54. PRP- Peoples Redemtion Party
55. PDP- Peoples Democratic Party
56. PAC – Progressive Action Congress
57. PPA – Progressive People Alliance
58. PSP – Peoples Salvation Party
59. RPN- Republican Party Nigeria
60. SDMP- Social Democratic Mega Party
61. UDP- United Democratic Party

62. UNDP – United National Party for Development
63. UNPP- United Nigeria Peoples Party